*_KALBIM_*

Mamuhgee

#Zafafabiyar

1

Bismillahir Rahmanirraheem

Ina rokon ALLAH Subhanahu wata'ala yanda zan fara littafin nan lafiya cikin aminci da yardarsa ya bani ikon kammalawa cikin kwanciyar hankali da nishadi tareda dacewa lfy Ni da yan uwana gabaki dayanmu.AMIN.

Dan Allah ku kasance masu uzuri idan an samu kuskure ko mantuwa da makamantansu,Thank you.

****

ZADEENs HEALTH CEN/SPEACIALIST,

WEDNESDAY 1:40Am

Tin kafin isowan motocinsu da suka tinakaro babbar gate din asibitin securities na asibitin suka taso kusan a tare suna wangale musu gate din cikin sauri sbd irin gudun da motocin Ahalin ZADEEN's din suka tinkaro dashi wanda duk wani ma'aikacinsu yasan idan ciwon motacin suka tinkaro asibitin to Hasken idaniyar ahalin ce ba lafiya wadda kullum take cikin ciwo.

Sauran securities din da basu qaraso bude kofar gate din ba kaf dinsu fitowa sukai suka tsatsaya a gate suna bin motocin guda uku da kallan girmamawa duk da tsakar dare ne tareda fatan Allah ya bata lafiya.

Motocin na gama shigewa aka rufe gate din tareda taresa sbd babu wanda yake shiga ta wannan gate din a qaidarsa sai masu asibitin wanda kusan koyaushe suna hanyar zuwanta.

Kafin suyi parking likitoci uku da nurses biyu suka fito ta private kofar da zata kaika kai tsaye zuwa Vip room din dayake sama gaba daya.

A tare duka kofofin motocin suka bude kusan a tare duka suke fitowa babu wanda baa cikin kayan baccinsa yake ba sai DZAD(Dad Zad) wanda shine asalin Zadeens din a yanzu da babu kakansu kuma shine mahaifin marar lafiyar tasu sanye yake da jallabiya da qatuwar rigar sanyi ash sai hula sbd idan ciwon 'yar dayake gani a matsayin tasa bugawar zuciyar ya tashi saukowa yakeyi gaba daya daga billionaire din da ganinsa ma yake wuya ya koma kaman asalin uban da bayada komai agajin gaske yake nema a gurin Allah.

Gadon da aka tura ta dashi ne komai nata a rufe ko fuskanta baa gani sbd kwata kwata basa bari ana ganinta sosai sai iya likitocin dake kulawa da ita sa ciwonta ne kadai suka san kamanninta sbd tsaro da tsananin rashin wasa da duk abinda ya shafeta.

Suna wucewa ciki sauran familys din suka musu baya babu wanda zuciyarsa bata harbawa da damuwa,

A daidai irin wannan yanayin ne ko lokacin idan suna cikinsa babu abinda bazasu iya kawarwa ba dan biyan buqatansu dan kuwa mantawa suke da komai da kowa sbd JANNAH.

Securities din ZADEEN's dinne da suka iso asibitin ba tareda kayan securities dinsu a jiki ba sbd basa son asan akwai wani me mahimmanci a asibitin suka zagaye private kofar har ciki batareda alamar da zata nuna securities ne su ba.

A sama kuwa suna isa aka shige da ita inda iya doctors dinne zasu shiga familyn kuwa a nan wani wadataccen palon jira dayake a tsare suka zazzauna cikin yanayi

mara dadi wasunsu kuma a tsaye suna kaida kawo cikin rashin sauti ko kadan sbd rashin dadin zuciya.

Mimi data fisu karfin zuciya akan lamarin Jannah din koyaushe itace ta dago idanuwanta da sukai laushi ta kalli Dzad wanda shima juyowa yayi ya kalleta da idanuwansa da sukai jajir kafin ya sauke ajiyar zuciya ahankali yana hade hannuwansa biyu sbd sanyin dayake ratsasa ko zai rage masa wanda kai tsaye zuciyarsa yake jin kaman yana zuwa zai masa illa sbd a wannan lokacin komai zai iya zama ajalinsa dan komai nasa yana gab da mutuwa idan har wani abu ya samu Jannah.

Hannu Mimi ta miqa duka biyu ta dora akan nasa hannuwan tana rufe masa su tareda bude baki cikin tsananin karfin hali da jarumtar da su suke rasawa tace,

"Insha Allah wannan karan zaa dace da zuciyar da zatai mata,

Zaa dace,Jan Zata rayu kaman kowacce 'ya insha Allah,

Jan zata zama kaman kowanne dan adam,zatai karatu me zurfi ta zama abinda kakeson ta zama insha Allah....

Rawa muryanta tafara yi karfin zuciyarta na neman karyewa dan haka tai shiru tana damqe hannuwan Dad din da dan karfi tana qasa da idanuwanta dake neman cikowa da hawaye.

Dzat din sake kame hannuwanta yayi da nasa yana kasa cewa komai dan irin hakan baya magana kowa ya sani.

Anny matar yayan jannah din wadda ke tsaye gefen mijinta MAHIR ZADEEN riqe da hannunsa tana kokarin kwantar masa da hankali tareda basa kwarin gwiwa dik da itama a sanyayen take sbd duk lokacinda zaa ce jannah ba lafiya a cikin matsanancin tashin hankali take duk da tasan ta riga ta tsira ta fita daga layin wainda zaa iya rabasu da zuciyar dake bugawa a kirjinsu sbd dubawa ko zata daidaita da wadda zata zaunu a kirjin wadda suke son nemowa zuciya kota halin yaya.

Baro gurin Mahir tayi ta dawo gefen Mimi tayi ta zauna ahankali tareda dafata ahankali tana furta mata kalaman kwantar da hankali da fatan ranar warakar jannah taxo.

Mahir zaunawa yayi shima yana dora kafarsa daya akan daya sbd sanyi da shima yake ratsashi wanda yakejin kamar fatar jikinsa ce ta bude kai tsaye sanyin na shigar masa kashi yana daskarar da jininsa gashi kayan bacci ne a jikinsa riga da wando masu tsananin taushi sbd tsadarsu sai jacket daya doro akai.

SALEEM ZADEEN wanda yake bin mahir kuwa kasa zama yayi sbd kansa dayake jin kaman yana motsi dan shi sam dan zafi ne baya da hakurin suspense irin wannan kansa yakejin kaman zai zare.

Shima riga da wando ne a jikinsa na bacci sedai shi hoodie jacket ce a jikinsa sai kai da kawo yakeyi yana kasa dago jajayen idanuwansa da suka sauya.

Kofar palon aka turo da sauri wadda ta saka dukkaninsu dagowa suna kallan Dr AMMAR ZADEEN wanda kai tsaye ya komar da kansa baya ne yayi karatun likitan Zuciya sbd Jannah kadai.

Idanuwansa da sukafi na kowannensu sauyawa ya dago ya kalli kowannensu kafin ya kalli dzat ya basa kwarin gwiwa ya juya ya fice zuwa dakin da jannah din take da doctors sbd shi biyawa yayi inda aka sanar dashi ana tinanin an samu donor kafin ya wuto nan shiyasa suka rigasa isowa.

Zaman kusan awa daya zuwa biyu sukai cikin tsananin daci da damuwar zuciya kafin Ammar ya fito ya shigo dakin yana sauke numfashi me tsananin zafi da huci ya qaraso ya zauna kujeran datake kallan su Dad din ya dago idanuwansa ya kalli dad.

Ajiyar zuciya me sanyi dad din ya sauke a natse yanajin hankalinsa na dawowa jikinsa take yaji dacin zuciyarsa ya ragu sbd yasan Ammar ko zuciya dubu jannah ke buqata zai nemosu ayita gwadawa har a samu wadda zatai daidai a saka mata kota halin yaya ba damuwarsu bane.

Mahir ma ganin hakan ya sauke ajiyar zuciya a boye kafin ya juya ya kalli Anny da kusan itama take ta fahimci akwai wani abin kenan da ido yai mata maganar ta fita da Mimi.

Ajiyar zuciya da numfashi itama ta sauke tareda dafa Mimin cikin kulawa da nuna tausayawa sosai da nutsuwa tace,

"Mimi muje mu duba Jannah din doctors din sun fito"

Dagowa Mimin tayi ta kalli Ammar wanda ya gyada mata kai alamar eh zasu iya zuwan,

Mahir ta kalla shima ya sakar mata murmushin karfin halin alamar insha Allah jannah yanzu zata samu sauki.

Miqewa tayi Anny tabi bayanta suka fice daga gurin Anny taja kofar ta rufe suka nufi dakin da jannah din take.

Suna ficewa Ammar ya sauke numfashi tareda dagowa ya kalli dzad dake jiran bayaninsa ya bude baki yace

"Ansamu donor wanda ta ko ina muke saka ran tayi....

Katsesa DadZad yayi da cewa

"Mene ake jira to?

Saleem da baida hakurin jiran komai batareda sanin abinda Ammar din zai fada ba ya matso gaban Ammar din kai tsaye yace

"Indai ansamu zuciyar da zataiwa Jan ko duka tawa dukiyar dana mallaka akeso zan bayar a karbo heart din ko a inane take kawai ka tabbatarda ka amsota Jan ta sameta"

Yana gama fadar haka ya juya ya nufi kofa ya fice zuwa dakinda jannah din take ya turo musu kofar da karfin daya saka dukkaninsu rintse idanuwansu banda Dad da bai motsaba har lokacin jiran sauran bayanin Ammar din yake wanda daman ba duka zance sukeyi da Saleem ba sbd zafinsa da rashin hakurinsa tareda rashin yadda da raayin kowa wani lokacin sai na kansa.

Ammar takardin dake cikin aljihun jacket dinsa ya fitar ya ajiye akan table din gabansu ya mayar da bayansa jikin kujeran dayake ya jingina yafara cewa

"Daya daga cikin asibitin da muka saka likitocinmu aka samo wadda zatai daidai insha Allah kuma kusan shekarunsu daya da Jannah din sedai matar Aure ce dan tanada tsohon ciki ma sedai batareda saninta ba likitocin sun duba zuciyar komai lafiya kalau."

Ajiyar zuciya me tattareda samun kwanciyar hankali mahir da dad din suka sauke lokaci daya sbd abinda kawai suke son ji kenan indai komai lafiya kuma ana tinanin zatai to sauran bayanin ba damuwarsu bane sbd sai sun rabata da wannan zuciyar datake bugawa a kirjin ta sun sakawa tasu yar batareda saninta ba sbd itace kusan ta numbar da bazasu iya kirgawa ba sai an cire aga bata daceba.

Dad din a natse yana komawa take Dzad dinsa ya gyara zamansa na asalin Me kudin dayake murza lokacinsa a yanzu ya kalli takardun batareda ya miqa hannunsa ya tabasu ba yace

"Kawai ku saka lokacinda zaayi aikin shine abinda yakeda mahimmanci amma sauran aikin ba buqatan damuwa,

Ku saka likitan datake gani acan asibitin gwamnatin ya turota nan asibitin batareda bata lokaci ba."

Mahir daya miqa hannu ya dauko takardun ya bude ya zubawa sunan dayake kai idanuwansa tsawon seconds ya duba bayananta da bai fahimci komai a cikinsu ba sbd tin daga sunan da garin datake babu wanda ko a cikin wani yare ya taba ji sbd ba anan suka tashi ba bare susan sunayen garuruwa duka bare qauyuka dayake ganin kamar dabbobine kadai suke iya rayuwa a cikinsu.

Jefa takardun yayi a kan table din kafin ya kalli dad din a natse yace

"Inaga zaifi tinda an samu wanda zatai din and she's preg abari ayi amfani da tsufan cikin da haihuwansa"

Kallansa Ammar yayi yana tinanin abinda yake fada wanda shi idan tasa zaa bi babu abinda zai tsaya jira bayan cirewa da sakawa Jan.

Dad shiru yayi batareda ya kalli kowannensu ba sbd maganar mahir din dan mahir shine kusan kamar me hangen lamuransu a duk lokacinda zaayi huldan business da irin wannan mummunar ta bayan fagen shine yake aunawa da hangowa ya fada yanda zaayi kuma hakan akeyi a dace sbd yanada ilimin nutsuwar fahimtar komai da mutane,

Hakama yanada wani irin ilimin dayafi duka familyn harshi dad din dan duk da dukkaninsu baa qasar suka taso ba sai yanzu ne da suka zabi dawowa gida sbd nemawa jannah kalbim.

#MAMUH

#ZAFAFABIYAR

#MASTERPIECE

#BESTSTORY

#BESTLOVE

#BESTROMANCE

#BILLIONAIRES WAR

#CRAZYLOVE

#ZADEENS

#LIMBAS

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*KALBIM*

Mamuhgee

#ZafafaBiyar

2

ZUZEAMVENTURES

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k 08144015291 kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Shiru dukkaninsu sukai daga dzad din har Ammar suna sake shiga nazarin maganar mahir wanda yake sake kokarin nazarta yanda zasu samu damar samun komai batareda wani damuwa ba dan shi sam baya yadda da damuwa ko tangarda a aikinsa shiyasa yake tamkar maye gurin nutsuwa ya hango ya hanga kafin ya fada.

Dzad duk abinda mahir ya fada yana kokarin bada damar abi hakan sbd yafi kaf yayansa nutsuwa da bin komai a tsare amma ayau yanajin kaman hakurinsa bazai barsa ya jira lokacin da mahir din yake fada ba sbd kada su rasa zuciyar wadda ake jiran kokuma idan gurin haihuwar ta rasu fa.?

Sun raba mutane da dama zuciyoyinsu sbd jannah amma babu wanda aka dace wanda ma basu san adadinsu ba ta boyayyar hanya

To ayanzu da suka samu bayan tsawon lokaci ana nema kuma a tsaya jiran wani haihuwar.

Mahir daya fahimci tinanin da Dad din yake sake bude baki yayi yace

"Jiran haihuwarta na nufin samun dama da dalilin rasuwarta ga mutane da yan uwanta shiyasa ana buqatan a jira lokacin haihuwan tayi sbd lokacin haihuwar ya matso sosai hakan ne zai saka komai ya tafi very neat tin daga cirewa da sakawan da rufe komai".

Ammar da zuciyarsa ke bugawa da sauri yana jin kansa na juyawa idanuwansa na ja jin yakeyi kaman bazai iya jiran lokacinba dan kuwa shi jinma yake kaman ya fizgo zuciyar a daren nan yazo ya sakawa Jan,

Shi a yanda yakejin yana zaucewa akan ciwon jannah duk mutanen dayake gani suna yawo zai iya ringa binsu yana fasa kirjinsu yana qwato zuciyoyinsu babu ruwansa da rayuwarsu indai jannah zata rayu.

Mahir ganin alaman Dad ya aminta da hakan ya sakasa kallan Ammar shi da Dad a tare sbd sanin shine mai juyewan kai idan wannan lamarin ya taso kwata kwata bayaji baya gani kawai abu daya ya sani shine karban kalbim kota waye ba ruwansa.

Dad ne ya bude baki a natse yace

"Ammar abari ayi hakan sbd tafiyar da komai batareda garaje ba ko dan ita jannah din hakama aikin nutsuwar da kwanciyar hankalin zaifi,

Tinda aka riga aka sameta duk inda zata shiga bazata gujewa abinda yake jiranta ba sbd yanzu zuciyar Jannah ce kai tsaye take bugawa a kirjinta babu abinda zai hana jannah mallakar wannan zuciyar me bugawa."

Numfashi me zafi da damuwa Ammar ya sake kafin yaji ya aminta da hakan dan haka zasu saka masu bibiyar yarinyar da bincike sosai akanta duk da babu ruwansu ba abinda ya shafesu da inda ta fito kokuma wace ita waye danginta.

******ASALIN LABARIN/SHEKARUN DA BAYA.

PROF ZAHARADDEN ZAADEN shine asalin mahaifin Yayansu uku biyu maza sai mace daya wadda yayunta mazan ke tsananin kauna sbd mahaifiyarsu ta rasu a hannun matar mahaifinsu suka taso,

Prof dan bokon gaske ne wanda ilimin bokon dana addinin suka shigesa sosai hakama yanada arziki sosai wanda ya dade sa barin qasar yana malaysia acan yake zaune da iyalinsa gabaki dayansu.

BOUKHAR Zadeen shine babba sai MAHMOUD Zadeen tukuna qanwarsu ZAYNEB,

Matar Mahaifin nasu bata taba haihuwa dashi ba dan haka su kadaine yayansa wanda suka girma kowannensu ya zama babban mutum,

A malaysia suka taso acan sukai karatu sai daga baya dukkaninsu su ukun suka dawo Nigeria tareda mahaifin nasu wansa tsufa yazo masa sosai.

Bayan tsawon shekaru Anyiwa Zeynab aure da wani prof itama a porthacort,

BOUKHAR da MAHMOUD kuwa kowannensu na qasa daban gurin karatu,

Mahmoud ya riga boukar aure kuma daga mahmoud din har zayneb babu wanda ya samu haihuwa a cikinsu har saida Boukhar yayi aure shine ya fara haihuwa a cikinsu.

Familyn ZADEEN's din sunada wani irin tarin arzikin dayake da yawan gaske da basuma san ya zasuyi dashi ba,

Bayan arzikin mahaifinsu prof me tarin yawa su kansu sun tara na kansu me yawan gaske dan kuwa ko Zaynab datake mace a cikinsu itama tanada nata arzikin sosai.

Suna tsananin son junansu wanda hakan ya saka iyalansu ma kansu yake a matiqar hade duk da su ukun gaba daya basa qasa daya.

Mahir shine babban dan Boukhar zadeen wanda ya haifesa a Greece,

Bayan haihuwar Boukhar Prof ya rasu wanda hakan ya saka dukkaninsu tattarowa suka dawo Nigeria.

Mahaifinsu nada kadarori sosai wanda bazasu iya gama hadasu lokaci daya ba dan haka mahmoud ne kadai ya koma boukar kuwa dole ya zauna Nigeria tareda iyalansa.

Umma matar mahaifinsu wadda ta riqesu tamkar yayan data haifa ba cuta ba cutarwa hannun Boukhar ta dawo dan yayansu ma basusan cewan ba itace ta haifi iyayensu ba sbd kulawa da kaunar dake tsakaninsu ta uwa da yayanta.

Mahir nada shekara biyar a duniya Zayneb ta samu ciki wanda yazo mata da matsala sosai sbd manyanci da dadewan datai bata haihun ba.

Cikinta na sake gaba girman matsalarta na qaruwa wanda daga baya aka gano tanada heart diseases wanda basu taba sani ba.

Hankalin familyn ya tashi sosai wanda ya sakasu dawowa da ita hannunsu aka fara neman mata lafiya.

Lokacinda aka gama bincike sosai akan ciwon nata aka gano tana buqatan heart transplant maana dashen zuciya.

Hankalinsu ya tashi sosai sbd ciwon nata bawai sbd zuciyar da zaa nema dinba sbd ganin sukeyi sunada dukiyar da zasu iya siyan mutum gaba dayansa su cire abinda sukeso a jikinsa.

Cikinta na kaiwa wata tara suka tattara gaba daya familyn suka koma Greece sbd haihuwarta da basa fatan matsala komai kankantarta.

Tin daga kan ummah da zayneb din da boukar da matarsa da mahir da mahmoud ma acan ya samesu da fmlynsa suka dawo zama.

Cs akaiwa zayneb aka ciro mata Baby boy wanda Boukhar ne ya saka masa suna Ammar sbd har lokacin mijinta bai taho ba yana porthacort da matarsa daya dan haka suka suka tattara suka watsar.

Tinda zayneb ta haifi Ammar bata sake lafiya ba sai ramewa takeyi tana wani irin hasken daya saka hankalin duk wanda yake familyn nasu tasu musamman yayun nata wainda suka ringa nema mata donors tako ina amma babu inda aka samu,

Sassaucin da suke samu a zuciyoyinsu shine likitoci sun tabbatar musu da akwai sauran time sosai kafin zuciyar ta gaza gaba daya dan haka suka ringa zubarda dukiya qasa qasa suna neman donor.

Ammar kuwa kusan Mimi ce mahaifiyar mahir matar Boukhar din ta renesa tin daga ranar da aka haifesa itace ta zama uwarsa dan ko nonon mahaifiyarsa baisha na wata biyar ba wata hudu aka ciresa daga nonon sbd bazata iyaba ta bushe sosai.

Duk wannan ciwon da haihuwar mijin zayneb din baizo yaga matarsa da dansa ba sai so daya dan haka su kuma basajin zasu taba basa ita ta koma bare Ammar da sukejinsa fiyeda komai sbd tsananin kaunar da sukewa kanwarsu.

Ammar tinda ya taso ya samu mahaifiyarsa a cikin mummunan hali harya fara girma a hakan yake ganinta wanda hakan ya taba zuciya da kusan lafiyarsa dan kuwa yanada qawa zucin mahaifiyarsa sosai musammam daya fahimci baida uba bayan Boukhar wanda Suke kira da Dad Zad sai Daddy mahmoud wanda takanas ya bude babbar asibiti sbd ciwon Zayneb kawai dan samun donors.

Mommah zayneb tinda ta haihu ta cire rai daga rayuwa sbd yanda takejin ita kadaice ta sani a hakan tana dauriya ne sbd ragewa yan uwanta damuwa da 'danta wanda ya sakata aransa sosai fiyeda komai.

Sbd ciwon zayneb Boukhar da Ammar da mahmoud saida suka koma abin tausayi duk girman arzikinsu,

Ummah kuwa babu ranar da bata kuka idan ta kalli yanda zayneb ta koma,

Mimi kuwa sosai itama ta tashi akan Ammar sbd saida ya zama traumatised kwata kwata baya gane karatun komai a school duk da mahir yana kokari sosai akan dan uwan nasa amma saida teachers suka gano suka bada shawarar Ammar din ya fara ganin likita.

Ana cikin hakan ne Mimi ta samu ciki wanda itama ta fara shiga matsalar rashin lafiya me nauyi sbd ga cikin dayazo da ciwo ga lalurar Ammar ga kuma ta familyn da kowa yake cikin damuwa da qunci.

a wannan lokacin ZAADENs suka shiga matsanancin halin damuwa da qunci,

Gasu da abin duniya me tarin yawan da basa ma san menene rashi ba ko wata kalmar datai kama da hakan amma sam basa cikin farin ciki.

A haka cikin Mimi ya isa haihuwa ta haifi Saleem wanda haihuwarsa ta fara dawo sa farin ciki rayuwarsu.

Mahir da Ammar kusan tare suka taso kaman ba shekaru sosai tsakaninsu sbd kaunar datake tsakaninsu tafi karfi akan wadda ke tsakanin mahir din da saleem.

Haihuwar saleem da shekaru biyar Allah yayiwa zayneb rasuwa bayan ta gama qarewa ta koma kamar qaramar yarinya hakama anyi mata dashen zuciyar wanda ta samu chronic rejection maana transplant failure.

Rasuwar Zayneb ta girgiza duniyar ZADEEN's gaba daya ta yanda tin daga lokacin suka sauya kaman basu din ba.

Ammar ya shiga sabuwar trauma wadda ta sakasu barin qasar gabaki dayanta sbd a sauya environment a bisa shawaran doctors dake dubasa.

Daddy mahmoud ma barin qasar yayi kwata kwata ya koma Nigeria.

Dad Zad kuwa UK ya koma da iyalinsa da ummah suka bude sabuwar rayuwa acan doctors kuma na duba lafiyar Ammar wanda kansa kamar ya tabu amma ahankali ahankali ya samu sauki harya koma karatunsa tareda yan uwansa.

Hankalinsu ya kwanta rayuwarsu ta koma ta asalin jin dadi da kwanciyar hankali arzikinsu kuwa sai abinda yaketa qara yin gaba duk da ciwon rashin Zayneb yana zuciyar dadzad kwata kwata ya kasa dena jin radadin rasata hakama Ammar ya kasa cire ciwon da rashin mahaifiyarsa yabar masa duk da ya danne ya koma kaman kowanne dan adam karatu yakeyi sosai.

Mahir,Ammar da saleem ZADEENs sun taso cikin wani irin gata da hutu tareda rayuwar rashin kwaba da rashin sanin mahimmanci komai da kowa bayan abinda sukeso.

#MAMUH

#ZADEENS

#LIMBAS

#BESTLOVE

#BESTSTORY

##CRAZYLOVE

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_KALBIM_*

Mamuhgee

#ZafafaBiyar

3

ZUZEAMVENTURES

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Mahir Zadeen shine kokarin naci akan komai saiya gano komai akan duk abinda yaga zai shiga rayuwarsa ko ta familynsa,

Baya maamala da mutune ko abu ko wane iri ne kuwa batareda ya samu sanin mai zurfi akansa ba,

Bayan familyn baya son kowa dan hakan ne ma baya shiga mutane sosai ko hulda dasu hakama bai yadda kowa ya kusanci fmlynsa ba sbd bai yadda da kowa ba akansu,

Hakama tin kafin shekarunsa sukai ya fara shiga huldodin familynsa sbd bi da kauce duk wani abu da zai cutatar dasu ko dukiyarsu.

Allah ya basa wani irin sharp kai da qwaqwalwa kamar maye dan hakan ne yasa dole da wuri su Dad suka bari ya shiga huldan duka zadeens babu wanda bai sani ba.

Hakama tin daga Dzad da daddy mahmoud babu wanda yake boye masa komai sbd ganin wani sharp kaine dashi.

Ammar ma yanada ilimin sosai sedai trauma dinsa tana damar masa da lissafi so da dama dan haka shi ya kasance kamar mara hankali akan abinda yakeso,

Akan familynsa zai iya komai me kyau da mara kyau bai damu ba,

Kaf familyn ZADEEN's babu wanda yake kallan gaskia ko adalci akan yan uwansu,

Sunada wani irin son kai da basa duba komai da kowa sai kansu,

Babu ruwansu da ko rai zaa rasa indai akan buqatarsu ne ko abinda suke so kuma hakan tamkar a jininsu yake dan kuwa babu wanda bazai iya komaiba a cikinsu akan abinda suke so ko buqata,

Inda tsananin son zuciyarsu da son kansu yayi mugun munana shine ko dayansu yake buqatan abu to zasu hadu su samar masa da abin nan koda kuwa hakan na nufin wasu zasu shiga mummunar matsala koda kuwa ta rasa rai ce su ba damuwarsu bane.

ZADEEN's sunada power me karfin gaske,sunada kudi,sunada kwarjini sunada isa,sunada duk abinda dibbin mutane da yawa ke tsananin nema da so na rayuwa basu samu ba,

Duk wannan lokacin da aka dauka bayan qara habbaka da samun power babu abinda sukeyi dan hakan ne ma ya saka koda basa zama a qasarsu sunyi suna da ficen da aka sansu dan kuwa ko a Nigeria din sunada power din da ko wasu masu mulkin basuda ita.

Sukan taho Nigeria din sosai dukkaninsu sedai basa wani jimawa sosai suke komawa dan hakan kan yayan yake sake budewa da gogewa a harkansu sosai.

Wani cikin Mimi ta samu wanda ya saka ya saka Ammar ajiye komai ya koma kulawa da ita sbd dukkanin qawa zucin dayake dashi da mommah akan mimin ya dawo

Hakama wani irin tsananin so da kaunar cikin Allah ya jarabcesa dashi wanda ya ringa rokom Allah yasa mace zaa haifa a saka mata sunan mahaifiyarsa.

Yanda Ammar ya kwallafa rai akan son cikin da fatar a haifi mace ya saka kusan kowa familyn tsananin son hakanta shigesa sai gasu dukansu kaf sun qwallafa ran Wata zayneb zaa haifa.

Kusan komai ajiyewa sukai suka maida kaf nutsuwarsu akan cikin dan haka Mimi ta dage da adduar Allah ya bata mace sbd samunta shine hasken dazai qara cike rayuwar zadeens da suka kasa manta radadin rashin zayneb.

Yanda kaf familyn suka duqufa da rokon samun Zayneb suka manta da komai zaka roqa ka roqi me albarka ko kuma zabin mafin alkhairi,

Ita haihuwa sam ba sai wanda kakesoba

Duk wanda Allah ya baka ka roki me albarka kawai kokuma lafiyayye.

Tin daga kan ummah datake tsohuwarsu har kan duk wanda yake familyn Allah suka ringa roqo akan zayneb sukeso kota yayane Allah ya basu wata zayneb din da suka rasa.

Hankalin Mimi fara tashi yayi ganin yanda duka hankalinsu ya gushe ko yayane so suke Allah ya karbi Addua da fatansu.

Damuwa da tsoro ya saka naquda zuwar mata batareda cikin ya isa haihuwa ba dan haka suka dunguma asibiti.

Ko asibitin da aka kaita babu me zuwanta sai wanda yakeda matsayi da kudin da kusan koina ka san dashi dan haka tin tana ciki aka fara yada ZADEEN's na shirin welcoming sabuwar princess din familyn.

Tsaron asibitin kadai zakasan masu abin duniya ne a asibitin dan haka Kusan su kadai ne a asibitin ranar.

Naquda sosai Mimi tayi kafin Allah ya bata ikon haihuwar abinda suka roka

'Ya mace Kyakkyawa da ita fara tas kuma kusan kammanin mommah zayneb din ta dauko dan kusan familyn kamanninsu daya shiyasa suke da wani irin kyau da kwarjini dukkaninsu tin daga kan su dzad din.

Tin a asibitin Dad ya saka mata sunan ZAYNEB BOUKHAR ZADEEN bayan ya dauketa da hannuwansa yanajin soyayyarta da kaunarta fiyeda duka sauran yayan daya haifa sbd tsananin kaunarsa ga zayneb da suka rasa.

Mahir ma jin yayi tafi masa duk abinda suka mallaka dan haka ya rungumeta sosai yana addua.

Saleem kuwa take yaji zai iya komai akanta.

Ammar ne na karshe a daukanta sbd idanuwansa da suka ciko da hawaye zuciyarsa na harbawa da wani irin tsananin kaunarta dan fuskan mommansa kawai yake gani akan nata ga kuma sunan da Dad ya ambaceta dashi na mommansa.

Ahankali ya rungumeta a kirjinsa hawayen dake idanuwansa na gangarowa ya bude baki Ahankali yace

"JANNAH"

Tausayinsa me tsananin gaske ne ya rufe Mimi ta miqa masa hannu tana kokarin boye nata hawayen sbd rasuwar momman data dawo musu sabuwa.

A sanyaye ya qaraso gurinta ta nuna masa gefenta ya zauna ahankali yana kama hannunta daya datake miqa masa ta dan kwanta gefen jikinsa tana cewa

"Ka samu jannah"

Murmushi yayi yana zubawa fuskan babyn idanuwansa tana baccinta hankali kwance kamar ba rai a jikinta.

Saida Mimin ta kwana asibiti kafin aka sallamesu suka koma gida cikeda farin cikin da suka manta rabonsu da irinsa.

Haihuwar Jannah zadeens itace babban Farin cikin daya cike gaba daya rayuwar ahalin gabaki dayanta dama duk wanda yake muaamala da huldan business dasu,

Duk wanda yake aiki a karkashinsu ma yayi farin cikin samun jannah sbd tayasu farin ciki dan haka tin tana jaririyarta duniya tasan da irin tsananin son da Ake mata,

Duniya ta sheda jannah zadeen itace hasken idaniya da rayuwar ZADEEN's.

Rayuwarsu ta dawo kamar sabuwar duniya da suke barewa a leda yanzu,

A baya komai ma wasa ne a yanzu ne ZADEEN's ke sake zamowa ZADEEN's da kowa yake shakka gashi daddy mahmoud ma ya dawo da familynsa sun hade sun

sake bunqasar datake bawa mutane tsoronsu amma har lokacin matarsa shi bata haihuba amma bai wani damuba sbd yayan 'dan uwansa da Ammar dan zayneb sun ishesa.

*******A DAYA BANGERN KUWA CAN BAYA.

Kauyen Bondi Ruwa akeyi sosai tsakiyar dare guraren karfe daya da rabi gari yayi tsit babu kowa babu komai bayan ruwan da suke sauka sosai da karfi.

Qaramin gidan ne sosai wanda rabinsa yake a zube katangar ruwa ya zubar tintini.

Dayan bangaren da bai fadi ba daki daya ne sai qaramin ban daki wanda shima rabinsa ya zube buhu ne a rufe da rabin,

A cikin dakin macen datake kwance tana hada wani irin zufa me tsananin gaske duk da sanyin ruwan da akeyi yana zubowa cikin dakin daga sama sbd gefe daya langa langar dakin ya bude.

Dan ta dake gefenta idanuwansa sunyi jajir sbd tsananin dacin ganin mahaifiyar tasa a hakan.

Tsohon cikin dayake jikinta ya kalla idanuwansa suka sake kadawa sbd damuwa da dacin a halinda mahaifiyarsa zata haifo masa kaninsa ko kanwarsa.

Hannuwansa ya miqa ahankali ya janyo zanin da bayada sanyi ya rufawa Umman tasa ya bude bakinsa da muryansa me sanyi yace

"Umma sannu"

Kasa magana tayi sbd wani tsananin azababben ciwon marar daya taso mata tanaji jini na balle mata amma ta danne cikin tsananin azabar da bata taba jinta ba sbd batason daga hankalin 'danta dayake shi kadai hasken rayuwarta da batada kowa sai shi hakama batason ya gani ya duk da tasan duk ayita a qare shine zai tayata haihuwar kila tinda batada me taimakonta a rayuwar nan yanxu bayan shi data haifa.

Daqyar ta iya bude idanuwanta da sukai tsananin nauyi ta kalli farar fuskansa ta asalin fulani da dasashiyar murya tace

"ABDULAZIZ"

kasa dagowa yayi ya kalleta sbd hawayen da suka ciko idanuwansa yanajin duk duniya babu abinda ya tsana kamar dangin mahaifinsa da suka kasa taimakon mahifiyarsa bayan rasuwar mahaifinsu.

Numfashi take kokarin saukewa cikin azaba sbd sanin taurin zuciya irin ta ABDULAZIZ har abada bazai taba so da kaunar ko mutum daya a cikin dangin mahaifinsa ba dan duk da abinda ya tsana da gaske yake tsanarsa.

Jini ne ruwan dayake zubo musu ya gangaro daga karkashin Umman.

Jajayen idanuwansa ya dago cikin duhun daren zaiyi magana sai kawai umman ta masa wata irin riqo me qarfin gaske tana rintse idanuwanta cikin azabar gaske tayi wani irin nishi take ta haifo abinda yake cikinta.

Hawayen azabar ne suka gangaro musu shida umman a tare sbd irin riqon datai masa amma jin kukan jaririyar ya sakasa bude idanuwansa duk da baya ganin komai sosai ya sunkuyar da kai yana Godewa Allah cikin hawaye duk da ba wasu shekaru ne dashi ba sosai iyakacinsa shekaru goma sha hudu.

Batason abinda zai saka Abdul din yasan meyake wakana dan haka ta dade da tanadar rezanta dan haka da kanta ta yanke cibiyar ta dauki yar hannunta na rawa da hannu ta shafa gabanta taji mace ce dan haka yaye zanin daya rufa mata ta saka yar a ciki ta miqa masa tana numfashi daqyar sbd jinin dayake neman bugar da ita.

Hannuwansa rawa sukeyi sosai ya karbeta tana bude idanuwansa sosai a cikin duhun dan yaga halinda umman take ciki amma baya ganin komai.

Shiru dakin ya sake dauka yana rungume da yar yana jin wani irin tsananin so da kaunarta da yakejin ko rayuwarsa zai iya badawa dan bata kariya itada ummansa.

Kanwarsa ce uwa daya ta haifesa hakama daga tsotsan uba daya suka fito kuma batada kowa bayan shi da umman,

Hakama ummansa batada kowa sai shi,

Shine zai zama gatanta itada umma koda kuwa zai rasa ransa to tabbasa zaiyi gwagwarmaya dan inganta rayuwar su biyun nan.

Guraren asuba ruwan saman ya dauke dan haka ya ciro yarinyar daga jikinsa ya kwantar gefen umman ya fita cikin duhun ya nufi can karshen kauyen gurin macen da ita kadaice aminyar mahaifiyarsa duk kauyen kuma ita kadai take taimaka musu.

#MAMUH

#AZIZ AY LIMBA

#BESTLOVE

#BESTSTORY

#HEARTTRANSPLANT

#JANNAH ZADEENS

#UMMITA LIMBA

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_KALBIM_*

Mamuhgee

#ZafafaBiyar

4

ZUZEAMVENTURES

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata 😆☹Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Duk duhu da tsit din daren baitaba jin tsoronsu ba dan a haka ya taso komai dare haka yake ratsasa gurin nemowa ummansa Abincin da zata sakawa cikinta sbd ita da babyn datake cikinta su rayu.

Tafiya yayi mai nisa kafin ya isa gidan da zashi din,

Kofar gidan ya tsaya idanuwansa da sukai jajir ya dago ya kalli kofar gidan yana jin zuciyarsa na quna sbd baida ikon buga kofar bisa ga dokar mai gidan,

Ya saba komai dare haka yake zuwa ya buga kofar gidan idan mahaifiyarsa bata lafiya sbd Mama Sakina taje ta taimaka mata,

Mama sakina kuwa komai dare yaxo ya buqaceta bata taba fashin xuwa komai fadan da mijinta zaiyi kuwa,

Duk masifarsa da tsanar da yayiwa Abdul din da mahaifiyarsa sbd sun hanasa kwanciyar hankali da masifar rayuwarsu amma hakan bai taba saka sakina janyewa daga garesu ba sbd kauna ce sosai a tsakaninta da Fatimar da bazata iya barinta a mummunan halinda take ciki ba itada Abdul.

Ba so daya ba mijinta ya saba yiwa Abdul din dukan tsiya sosai akan zuwar masa gida tsakiyar dare.

Zafafan hawaye ne suka cika idanuwansa yana kallan kofar gidan kaman zuciyarsa zata fashe da ciwo da radadin bazai iya kiran Mama sakinar ba dan yana taba kofar gidan baba ilan dukan da bazai iya bawa ummansa kulawa ba a yanzu datake tsananin buqatansa zai masa shikuma bazai iya barin komai ya samesaba a yanzu dayake son kulawa da umman da 'yar data haifo musu.

Gefen kofar gidan ya koma kadan ahankali ya durqusa yana sunkuyar da kansa qasa dan jiran ayi kiran asubar da yasan lokaci yayi insha Allah.

Wani irin sanyi ake kadawa sosai

Sauran ruwan da aka dan dauke suna yayyafowa akansa ahankali suna ratsasa amma bai ko matsaba bare alamar tashi bakin kofar gidan.

Jiran kusan awa daya da mintina yayi kafin masallaci daya kwal dayake kauyen suka rangada kiran sallan daya sakasa miqewa da dauri kafafunsa da sukai wani irin riqewa suka kasa daukansa ya zube a gurin cikin ruwa da lakar datake lalace sosai da kofar gidan.

Rintse idanuwansa yayi zuciyarsa data fara bushewa tin yana karamin nasa ta masa wani irin nauyi yana jin kirjinsa na masa ciwo.

Hawaye masu dumi ne suka gangaro masa ya dafa yana kokarin miqewa aka bude kofar gidan.

Baba ila ne da babban dansa dayake uztaz wanda shi yake sako uban nasa gaba zuwa masallaci lokutan asuba a gida yake sallan baya zuwa masallaci da asuba.

Bude kananun idanuwansa masu kama da kamar an kashe kwarkwata ya waresu akan Abdul din duk da akwai duhu sosai har lokacin amma baya buqatan wahalarda kansa gurin sanin waye dan kai tsaye yasan baida tsohon dan iskan dazai zuwar masa gida bayan Abdul din wanda yake fatar Allah ya nuna masa sunbi duniya sunbar kauyen ko gidansa zai huta da maitar Abdul din.

Cikin zafin rai ya harbi Abdul din da kafarsa yana cewa

"Uban waye a kafar gidana cikin duhun nan??

Cikinsa daya harba ya dafe da hannunsa daya yana dagowa cikin tsananin azaba ya dafa hannunsa daya ya miqe yana kokarin bude baki zaiyi magana Baba ilan ya rigasa da cewa

"Nace uban waye ne a gurin?

Gali dayake gefen baban fitilar hannunsa ya kunna yana haske Abdul din da ita cikeda mamakin ganinsa duk da yasan yana zuwan amma a cikin ruwa da sanyin nan me yakeyi a kofar gidan wanda da alama ya dan jima.

Wasu hawayen ne suka sake gangarowa daga jajayen idanuwansa kafin ya bude bakinsa muryansa a sanqare da sanyi duk da yasan suna sane da waye din amma bude baki yayi yace

"Nine Abdul"

Katsesa Gali yayi da cewa

"Lafiya kuwa cikin sanyin?

Bude baki yayi zaiyi magana amma Galin ya wuce cikim sauri yayi masallaci sbd jin angama kiran.

Baba ila ne ya kallesa cikeda baqin ciki da tsana me tsananin gaske yace

"Allah ya tsinewa sanayyar datake tsakanin Sakina da Uwarka dan kuwa babu abinda kuke qararta dashi sai baqin talauci da baqaqen masifun da kuke yawo dashi,

Ace har tsakar dare bata huta da masifunku ba,

Yanzu ubanme zatai muku da asubar farin??

Wani abu me daci da nauyi Abdul ya hadiye kafin ya bude baki yace

"Haihuwa ummana tayi"

Cikin sabon baqin cikin daya tirniqe baba ilan ya tsaki tsokin daya saka Abdul din rintse idanuwansa yace

"An haifowa sakina wata sabuwar Masifar kenan,to wlh tallahi baa gidana ba,

Na gaji bazan iya ba,duk yanda nake shan rantsuwa da masifa sakina ta ture bata ji bata gani saita ringa daukan abincin danake wahala ina nemowa na gidana ta baku to daga yau ankai karshe sbd bazai yiyu ni ban tara nawa yaran dazan ringa ciyarwa ba haka kawai na koma ciyar da 'yayan wani katan"

Juyawa yayi ya koma ciki yana fasa zuwa masallacin bakinsa na cikowa da kumfan masifa sbd yasan yana tafiya wlh sai an dauki abincin gidansa ko wani abin antafi

dashi sbd sakina dai sedai ya barwa fatima da 'danta dan bazata iya rabuwa dasu ba.

Abdul cikin tsananin sanyi da azabar data gama shigarsa ya bi bayan baban da sauri dan kada ya hanasa ma shiga.

Kai tsaye dakin sakina ya nufa ya kiran sunanta cikin tsananin baqin ciki da masifa taresa bacin rai yana cewa maza ta fito.

Daman ba wani nauyin bacci ne da ita ba dan haka cikin bacci taji yana kiran sunanta da karfi ta bude idanuwanta tana kokarin tashi zaune ya shigo dakin sbd daman baa dakinta ya kwana ba ranar a dakin uwargidansa ya kwana.

Yana shigowa dakin ta lalubo fitilarta ta kunna haske ya wadata dakin,

Akan Abdul dayake tsaye a kofa bai qarasa shigowaba idanuwanta suka sauka.

Faduwa gabanta yayi da sauri ta janyo dankwali tana daurawa akanta ta miqe daga katifar datake kai tana ambatar sunansa baba ila ya katseta da cewa

"Ayau idan har kika fita gidan nan kika bi yaron nan gurin uwarsa wlh tallahi a bakin aurenki hakama abinci na ko wani abin dayake nawa a gidan nan kika basu shima a bakin aurenki,

Bazan iya ba na gaji da renan 'da da uwar da banda hadi komai dasu bare yanxu wata wahalar da aka sake haifowa.....

Da sauri sakina ta dago idanuwanta da ciko da hawayen tashin hankali da firgicin maganarsa ta farko ta kalli Abdul jin maganar haihuwar.

Shima dago jajayen idanuwansa yayi ya kalleta cikeda girgiza da tsoron abinda Baba ilan ya fada.

Gangarowa hawayensa masu tsananin zafi sukai ya dan ja baya ahankali batareda ya iya cigaba da tsayawa ba sbd bai san me zai fadawa mama sakinan ba kuma.

Bude baki tayi ahankali tace

"ABDULAZIZ"

Cak ya tsaya batareda ya dagoba.

Kofar inda kayanta suke tai batareda ta cewa baba ilan komaiba,

Zannuwan kayanta na sakawa masu tsafta ta dauko tareda guda biyu da rigarta ta sanyi daya da ita kadai takeda ita ta dauko wanda itace da kanta ta siya abinta da yan kudinta.

Inda take ajiye kudi ta duba tana saka hannu cikin kofin silver me murfi taji babu komai a ciki.

Juyawa tayi ta duba gurin ajiyarta daya taga dari bakwai ne kadai da ita dan haka ta dauko dari biyar ta juyo ta nufi kofar ta fito.

Kayan ta miqa masa cikeda kunyarsa duk da yana qaramin yaro ta bude baki asanyaye tace

"Ka siya mata koko me zafi sauran canjin ka siya itace ka dafa mata ruwan zafi tayi wanka itace da abinda aka haifa"

Hawayensa ne suka gangaro ahankali suka sauka akan dari biyar din data dora masa a tafin hannunsa.

Kasa magana yayi kai ya gyada mata ahankali yana damqe kayan hannuwansa na qara daukan sanyi.

Baba ila daya kasa motsawa sbd baqin ciki da mamaki kallanta yayi ita kuma taqi kallansa

Baqin ciki sake rufesa yayi kamar zai fashe sbd baqin ciki yace

"Sbd ki nunamun ban isaba shine a gaban nawa ko matsawa daga inda nai maganar banba zaki dauki abubuwa ki basu??

To meye amfani na a rayuwarki sakina tinda kinada Fatima da 'danta ai saiki fice ki bisu kije na bar musu ke wlh"

Abdul kafafuwansa da sanyi yayiwa mugun shiga ya ja ahankali yabar gurin yana qanwame kayan data basa da kudin.

Yana ficewa gidan Mama sakina ta dago ta kalli baba ila har zatai magana sai ya katseta cikin tsananin zafi da cewa

"Wlh tallahi na barwa fatima ke kawai ki tattara ki bar mun gidana ki bita can saiki kwasheta kiyi kauyenku da ita da 'yayanta"

Kofa ya nufa yana ball da butarta dake hanyarsa ta wucewa yana jin zuciyarsa na wata irin tafasa da bacin rai me tsanani.

Numfashi me sanyi da mutuwar jiki ta sake tana danne zuciyarta akan furucinsa wanda shedan ke ingizata data bar masa gidan nasa ta tafin sbd su fatima sunfi buqatarta amma kuma girman auren nata take kalla ta danne zafi da bacin da ranta

yayi dan yanzu ne zata biye masa suyita masifa a cikin gidan har wayewar gari da wuni zasu iya wuni suna masifa.

Butarta dayayi wurgi da ita ta nufa ta dauka tana qarasa zubar da ruwan ciki da suka rage ta nufi gurin diban wasu ruwan tana duba butar idan bai fasa mata ita ba.

Tana diban ruwan bandaki ta fara shiga tana fitowa tai alwala ta shige dakinta.

#MAMUH

#ZADEENS

#LIMBAS

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_KALBIM_*

Mamuhgee

#ZafafaBiyar

5

ZUZEAMVENTURES

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉☹Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Abdul kuwa yana fita gidan tafiya me dan tsayi yayi kafin ya durkushe a gurin yana fasa wani irin kuka me tsananin gaske sanyin gaske na ratsatsa.

Saida aka fito masallaci kafin ya daure ya qarasa gida,

Koda ya isa zanin dayake rufe da umman me sanyi kawai ya yaye mata ya rufa mata daya daga cikin wanda mama sakina ta basa,

Leqa babyn datake kwance gefen umman yayi yaga bacci takeyi lafiya kalau dan haka ya fice.

Alwala yayi ya dawo daga kofar dakin ya samu inda yayi sallah.

Yana idarwa ya dawo cikin dakin ya taba ummansa yaga tana numfashi.

Ajiyar zuciya me tsananin sanyi ya sauke kafin ya fita sbd gari ya waye sosai.

Gurin me siyarda koko ya tafi

Sai alokacin ma take hada wutar hada kokon dan haka yabar kudinsa ya koma ya nufi daji ya samo abinda zai hura wutan ruwan zafin da mama sakina tace.

Duka sun jiqe abubuwan daya tsinto amma hakanan yaje ya siyo ashana ya karbo kokon daga nan ya kawo mata.

Daqyar ya iya taimakawa umman ta tashi zaune ya dora mata robar kokon wadda ta bude bakinta daqyar kokon na shiga wanda zafinsa ya sakata jin hanjinta da suka nade suka dunqule fara warwarewa harma cikin na dan mata ciwo.

Tana gama shanye kokon amai ya taso mata gabaki daya ta amayar dashi.

Wutar ya hau hurawa wadda ta cinye gaba daya ashanar daya siyo sai daya koma ya qaro wata itama saida ta kusa qarew kafin wutar ta kama jikinsa na rawa ya dora ruwan.

Hura wutar ya zauna yanayi sosai batareda ya hutaba har saida ruwan sikai zafi sosai.

Umman daqyar ta iya tasowa ta nufi bandaki yakai mata ruwan shima ya fito ya dauko babyn ya fito daga daki sai a lokacin ya zuba mata idanuwansa yafara yi mata wani irin kallan tsafta me hade da wata irin kauna me tsananin gasken da batada sirki.

Wanka sosai umman tayi ta gyaro kanta ta fito har lokacin bata iya ko tsayuwar kirki.

Uwar haihuwar data bari a dakin ta shiga ta dauko ta goma gefen gidansu daya zube ta binneta daqyar jikin yana kakkarwa sosai sbd jirin gaske ma take gani.

Yana ganin hakan ya shiga dakin da sauri ya dan gyarosa ya share ya goge duk sanyin dakin tas ya sake shimfida mata wani zanin akan qaramar katifarsu umman ta kwanta.

Fita yayi ya sake siyo mata koko da saura Canjin daya rage ya kawo mata sedai koda ya dawo gabaki daya ta fice hayyacinta bama zata iya ko motsawa ba bare sanin meyake fada.

Ajiye robar hannunsa yayi yana kokarin dagota amma gaba daya jikinta ya sake.

Ambatar sunanta yafara yana shafa fuskanta zuwa wuyanta kuka na zuwar masa sosai.

Kuka me qarfin gaske babyn datake gefensu ta fasa wanda ya sakasa saurin juyowa yana rasa ya zaiyi.

Kuka sosai baby tafara wanda ya sakasa sakin umman ya zauna tsakiyarsu yana sunkuyar da kai shima ya fara kuka yana wani sheshekan da har jikinsa rawa yakeyi.

Ya jima a hakan batareda yasan me zaiyiba har babyn ta gaji tayi shiru ta koma bacci.

Ummansa kuwa wata firgita ta fara tana jijjiga.

Qanqameta yayi yana ambatar sunanta amma batasan ma yanayi ba.

Kusan awa daya a hakan kafin jikinta ya sake sakewa tayi baccin wahala.

Shima a gurin cikin jikinta baccin walaha da yunwa ya daukesa.

Sai azahar ya farka ya fita gidan ya nufi gurin aikin lakar dayake zuwa yana dan tayasu suna basa nera dari.

Acan yayi sallah yayita musu aiki har wanda yafi karfin shekarunsa.

Daga can wani kokon ya sake siyowa ya kawo yasha shida umman wadda sedai ya bata daga kwancen dan bata iya tashi hakama gabaki daya ta koma kamar ba umman tasa ba sbd wasu abubuwa takeyi da fizge fizge da zabura.

Yamma nayi yasan baba ila baya gida dan haka ya dauke babyn ya rufeta da zani kusan uku ya nufi gidan mama sakina da ita sbd tanada kuka.

Harya isa gidan babu wanda ya taresa ya tambayesa sbd gudunsu ma akeyi a kauyen sbd camfa ummansa da akai da baqar mace.

Mama sakin wuni tayi cikin damuwa da tinaninsu dan haka tana zaune tana hada saka da warwara tagansa ya shigo da zani

kallo daya tai masa ta gane jaririyarce ya dauko.

Cikeda mamaki da tsoro ta kallesa tana miqewa ta karbi 'yar tana cewa

"Abdul meyasa ka fito da ita??

Yaya ummanku?

Ya jikinta?

Kasancewarsa mara hayaniya da rashin sabo da magana sosai sbd baida abokan wasa ko wasu yan uwan daya taso cikin gata yasa ita kadaice ma wacce yake magana da ita sosaima

Ya dan dago kansa batareda ya kalleta ba yace

"Tanata kuka ne tin dasafe,

Umma kuma batada lafiya tanata firgita"

Kasa cewa sakina tayi ta nufi daki takai yar da sauri tana fitowa ruwan zafi tafara dorawa kafin ta dauko abincinta na rana da bata samu ci ba sbd damuwa ta miqa masa tace

"Maza zauna ka cinye yanzu"

Zaunawa yayi yaci abincin ita kuma tana sauke ruwan dauko babyn tayi tahau yi mata wanka sbd batason baba ila ya dawo ya taddasu hakama batason yayi dare a hanya da 'yar.

Wanka sosai me kyau tayi mata duk da bata taba haihuwaba batasan yaya akeyiba amma dayake anata haihuwa a gidan tana gani kuka tana dan saka hannu sai ta iya.

Tana gama mata wanka kayan data siya guda daya na jiran haihuwar matar Gali 'dan mijinta ta dauko ta sakawa yar ta dauko madarar shanun datake da ita me kyau ta bata kuma cikin ikon Allah yarinyar tasha take ta koma bacci abinta.

Sake nade masa ita tayi sosai ta basa tace maza ya koma.

Karbanta yayi ya juya ya fice daga gidan.

Koda ya isa gida ummansu ta tashi tana zaune ta zubawa kofa idanuwanta da sukai fari fes hakama bakinta ya bushe sosai.

Cikeda mamaki da dan farin cikin ganin ta tashi ya qaraso yana cewa

"Umma kin samu lafiya?

Juyo idanuwanta da suke kamar a buge tayi ta zuba masa batareda tace komaiba sbd kamar ba yayanta bane take gani.

Sake tambayarta yayi yaga ko kyaftawa idanuwanta basayi kallansu takeyi numfashinta baya fitama daidai.

Babyn ya bude daga zaninta ya dora mata a hannunta yana cewa

"Mama sakina tai mata wanka ta saka mata kaya"

Babyn ta saukar da idanuwanta ta zubawa ido tsawon mintina kafin ta dago ta zubawa Abdul din idanuwan shima

Shima ita yake kallan cikin tsoron irin kallan datake musun.

Sakin babyn tayi da sauri ya tare tareda daukanta ya ajiye gefensu yana cewa

"Umma kin gaji ne?

Har lokacin batace komaiba bata kuma dena kallansaba kaman wanda bata saniba ko bata taba ganiva.

Zamewa tayi ta koma ta kwanta tareda zubawa babyn gabanta ido.

Har dare yai suka kwanta batareda sun samu abinda zasu ci ba umman batai magana ba har lokacin hakama bata dena kallansu ba.

Cikin tsakar dare cikin bacci yaji motsin umman ya bude idanuwansa sai yaga ta tashi zata fita ko dan kwali babu a kanta hakama bata ko iya tsayuwa da kyau.

Kasa daukanta kafafunta sukai ta zube qasa kanta na buguwa da bangon kofar fita dakin take goshinta ya fashe da jini.

Tashi yayi da sauri yana riqota cikin tsoro da tashin hankali yana cewa

"Umma ina zaki?

Zaki bandaki ne?

Kallansa ta juyo tanayi kafin ta dago hannunta dayake wani irin rawa ta nuna masa kofa batareda tace komaiba.

Kofar ya kalla kafin ya kalleta sai ya rasa me zai fada ya kamo hannunta kawai ya dawo da ita kuma ta biyosa kamar yarinya qarama.

Kwantawa suka koma sukai take kuma saita koma baccinta.

Gari na wayewa yaje yayo aikinsa ya dawo mata da koko ya sake dafa mata ruwa ya sake ficewa.

Sai yamma ya dawo musu da tuwon dawa da miyar kuka dan kadan wanda aikin wahala yayi ya samosa.

Kasa cin abincin umman tayi duk yanda yayi sa ita dan haka kaman yanda yake bata koko haka ya zauna ya bata abincin a baki da kansa.

Babyn kuwa sake kaita yayi gurin mama sakina ta bata irin madaran jiya tasha ya dawo da ita gida.

Yana dawowa a hanya ya hadu da ummansa tana tafiya tana jiri ba dankwali akanta,

Da sauri ya kama hannunta suka juya gida yana mamakin abinda ya samu umman ga jikinta duk jini.

Suna komawa gida ya zaunar sa ita yana mata magana amma kwata kwata batacewa komai kallansa kawai takeyi.

Hawaye ya fara batareda yasan me zaiyiba.

Da daddaren ranar ma so biyu tana kokarin fita yana dawowa da ita tim anan ya fahimci ummansa ta kamu da wani sabon rashin lafiyar.

Kuka ya ringa yi har safe kuma da safen ma daqyar ya iya fita yabarta.

Koda ya dawo bata fita ba amma tana zaune babyn nata kuka sosai kamar bataji sai kallanta takeyi idanuwanta sunyi jajir kamar zasu fashe.

Daukan babyn yayi ya zauna gaban umman ya fada jikinta yana fasa kuka shima yana ambatar sunanta.

Kukansa ne ya saka wani irin hawaye masu tsananin zafi da ciwon da bata saniba tsinke mata tana qanqamesa tana jin tsananin sonsa shi kadai dan shi kadai take jin sonsa amma babyn kwata kwata kamar bata santaba dan kanta dake kokarin juyewa koma ya juyen.

Sun jima a hakan suna kuka duka su ukun harda babyn da suka matse a tsakiyarsu.

Sun jima a hakan kafin umman tayi bacci da babyn shi kuma ya fita sallan magrib yana dawowa a gida yayi ishai sukai baccinsu.

***kwanaki suka fara tafiyar musu ahankali ahankali ya fahimta da kyau kamar ummansa ta haukace sedai hauka bame tashin hankali ba wanda asalin yunwa da infection ne daya mummunan shigarta a gurin haihuwar me mugun karfi daya juyar mata da kai kwata kwata ta manta wai haihuwa tayi.

Mama sakina na cikin tsananin damuwa da tashin hankalin da suke ciki sbd yunwa da ciwo me karfin gaske na kokarin shigar babyn wadda tafara qanqamcewa ga Abdul din da shima wahala take neman kashesa da qananun shekaru.

Abdul kuwa da ummansa sun koma masu baran karfi da yaji sbd duk zai tafi gurin aikin wahalar dayake yi binsa takeyi bata zama fitowa takeyi dan haka tare suke zuwa ya zaunar da ita guri daya wasu su bata sadaka sbd tinanin almajirace wasu kuma gudunta ma sukeyi.

A cikin wannan halin sukai sati kusan uku sedai zuwa lokacin duk jamaar kauyen sun fahimci fatiman ta samu tabin kwakwalwa dan haka sadakar ma aka dena bata.

****FATIMA UMMITA shine sunan da Abdul ya sakawa qanwarsa dayake jinta kamar ransa dan kuwa shine me goyata da kansa duk yawon da zaiyi da ummansu yarinyar tana bayansa harya saba yanzu kauyukan gabansu suke zuwa tallan yalo dayake sara yana siyarwa.

UMMITA daga baya umman na bata nono dan haka tafara lafiya ta koma cikakkiyar lafiyayyar baby sedai har lokacin sitirar sakawanta daya ce tak wadda mama sakina ta saka mata,

Wanka kuwa sai suyi sati baayi mata ba sai daga baya yake kaita mama sakinata tayi mata harda hudan kunne tai mata ta saka ma yan kunne harda wasu kayan ta sake siya mata guda daya dan itama batada wani karfi.

##MAMUH

#LIMBAS

#ZAADENS

#BESTSTORY

#UMMITA LIMBA

#JANNAH ZADEEN

#DONOR

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

6

ZUZEAMVENTURES

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😄🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Malam AYOUB LIMBA ma'aikacin wata maaikatar qera robobi ne dayakeda gaskia da amana tareda kwarjini da farin jini sosai ga duk wanda yayi hulda dashi sbd gaskiyansa da hakurinsa tareda sanyin halinsa.

Ayoub baida uwa a cikin matan babansa ya taso sbd tasa uwar ta rasu tin yana qarami,

Cikin azabar yan ubanci data matar mahaifinsa ya taso babu sauki ko sassauci a halinda ya taso cikinsa a gidan mahaifinsa gashi mahaifin nasu bame zama bane yawon nema yake zuwa,

Azaba da ukubar gidan ya sakasa zamowa me zafin nema da kokarin aiki wanda ya saka ya fara banbanta da yaran gidan sbd yanada 'da'a kokarin bin na gaba,

A cikin masu aikin me gari ya samu ya shiga suna zuwa kauyuka cin kasuwa suna siyar masa da hatsi da albarkatun gona sukan yi kwana biyu basu dawo ba.

Tin ana ganinsa yaro shekarunsa basu kai ba har kokarinsa ya kwacesa ya zama sharp yana iya huldodi sosai wanda ya saka ya samu matsayi me tsafta a zuciyar me gari daga nan ya hadasa da wasu mutanensa dake wani kauye masu zuwa birni suka fara zuwa dashi,

Cikin kankanin lokaci acan ma ya samu mutane masu kaunarsa ya bar kauyen kwata kwata sedai yazo ganin gida Allah ya fara rufa masa asiri.

A wannan lokacin da Megari yake tamkar mahaifinsa sbd kauna da kuma juya masa dukiyar dayake yi a can birin sbd shekarunsa sunja sosai ya zama matashi me gaskia da amana kwatsam Allah ya karbi ran maigari wanda hakan ya saka kaf yan kauyen masu hassadarsa suka taso suka zuga iyalan megarin suka kwace komai nasu tas basu bar masa komai ba.

A cikin gidansu kaf daga yan uwansa har matan babansa harma maqota hassadarsa sukeyi dama matasan kauyen kaf sbd babu wanda ya taba fita birni nema a tarihin kauyen sai shi ya shiga cikin masu arziki harma da dan karatunsa ya koyo dan haka tsanarsa suke ji sosai da baqin cikinsa sbd babu me abinyi a cikinsu

Gashi ko gona babansu baida bare suyi noma daga me saida rake sai me saida itace da dadai sauran irinsu da baa wani samun komai.

Rasuwar me gari da wata hudu nasu mahaifin ya rasu dan abinda ya bari wanda duka idan aka hada bazaa samu dubu dari ba aka tattara aka raba aka bawa kowa ya tattara yabar kauyen.

Watansa biyar da tafiya ya samu aiki a wani kamfanin qera roba wanda gurin qerawan yake wajen birni sosai harya zo kusa da kauyensu sosai dan haka sai hakan yai masa dadi dan babu jimawa ya fara gini a kauyen da dan qaramin filin daya siya.

Aikinsa yana rufa masa asiri sosai dan abinda yake samu din yanayi ba laifi hakama shi kadaine dan kauyen a cikin kaf ma'aikatan gurin dan haka shine kusa yakeda sani sosai a bangaren dan haka kowa ya tashi neman abu shi ake nema.

Hakurinsa da kwantar da kansa tareda rashin rawar kai ya saka yayi farin jini sosai da suna a gurin,

Sabuwar hassada ce da baqin ciki ta sako yan kauyen da yan uwansa gaba daya suka fara kokarin ganin sun masa baqin ciki amma bai taba damuwa kuma yana taimaka musu sosai.

A maaikatar yake kwana amma yana gama gininsa na qasa ya dawo gidansa daga nan yake zuwa aikinsa kullum akan kekensa sabuwa dal daya siya.

Gama gidansa da wata uku ya hadu da Fatima da sakina qawayen da suka taso tare tin yarinta baa kauyensu suke ba kauyen kusa dasu,

Fatima a hannun kawunta take sbd itama marainiya ce dan haka kawun na ganin Ayoub nada abin lasawa tini ya basa aurenta ba bata lokaci akai auren bayan tabarma da buta sai setin kayan cin abinci na silver babu abinda ya siya mata ya tattara aka kaita sedai daga baya ayoub ya siya musu katuwar katifa da abubuwan buqatarsu suka gyara gidansu.

Zuwan sakina gurin fatima kauyen Allah ya hadata da baba ila shima ya aurota suka dawo zama kauye daya.

Baba ila kwata kwata baya kaunar Ayoub dan yana cikin yan hassadarsa dan haka ya fara shiga tsakanin Amintar Sakina da fatima duk da sam sakina bata yadda da hakan ba saida fatima taga hakan zai fara kawo matsala a auren sakinar se ta dan ringa janyewa sbd a zauna lafiya.

Shekara daya da auren cif Fatima ta haifi Namiji wanda Ayoub ya sakawa sunan Maigari wato ABDULAZIZ AYOUB LIMBA.

Abdul ya taso mahaifinsa da ummansa suna tsananin sonsa da kaunarsa cikeda gata da kulawa musamman da mahaifinsa ya kasance masu dan karfi a kauyen,

Ayoub baya barin Abdul fita waje wasa ko yawo kaman yanda yaran kauye sukeyi hakama sitiran sakawansa da cimarsu ma daban take me tsafta da wadata,

Ayoub ya killace iyalinsa sam baya barinsu shiga mutane sosai sbd yasan baa kaunarsu a kauyen dan haka zaa iya cutatar dasu dan haka ko fatima bada kowa take hulda ba bayan danginsa wainda itama suka tsaneta da 'danta amma duk da hakan tana dan mu'amalantarsu.

Abdul yana kaiwa shekarun fara karatu Ayoub ya sakasa primary school dake can local government kullum yana kaisa da keke ya daukosa idan antashi.

Fara karatun Abdul ya sake banbantasa da yaran kauyen gashi ya taso baa wani shiga mutane dashi sai ya kasance baida iya muaamala da mutane,

Gurin aikin babansa ne kadai yake sakewa yayi wasa sbd acan suna sonsa kasancewansa fari sosai Kyakkyawa sbd daga babansa har ummansa farare ne tas.

Abdul ya dauko farin jinin babansa da kwarjini tin yana yaro duk inda akaje dashi idan ba kauyensu ba da bazasu taba sonsu ba sansa akeyi sosai.

Abdul nada shekara goma sha uku ya zama wani irin nitsatsen yaro mai daukan ido da nutsuwan data kere ta masu shekarunsa wanda asalin miskilanci ne daya taso a cikinsa na tasowa kai daya ba abokin wasa sai iyayensa yai masa yawa gashi lokacin ilimin boko da addini duk babansa ya tsaya akai yana basa.

A ranar wani jumaa da ayoub yayi kwana biyu yana kwana gurin aiki sesai ya dawo gida ya koma sbd ayyukan da sukai yawa gashi maaikatansu da yawa basa nan sbd lokacin baa gama dawowa hutun sallah bane.

Ranar a gida ya wuni tareda Abdul sukaje local government sallan jumaa sukayo siyayyar kayan kwalama suka dawo

Duk inda suka wuce take zakasan uba da 'da ne sbd kamanninsu dasuke bayyane.

Suna dawowa gida a tsakar gidan fatima tai musu shimfida suka zauna dukkaninsu tana gyara musu su lemun da suka siyo da karas da harma da yalo suna fira suna ci.

Ayoub bai bar gidan ba sai da yayi sallan ishai yai musu seda safe ya fice Abdul nai masa saida safe kaman ya bisa amma fatima ta hanasa duk da washe gari ba makarantar boko.

Karfe biyun dare kauyukan kusa suka dauki hayaniyar gobara data tashi a ma'aikatar robobin take jamaa suka ringa fitowa cikik mamaki da tsoron kada wutar ta biyo daji tayo musu nan.

Wasu kuwa haka kawai suka ringa godewa Allah da wutar sbd dukkanin baqin cikinsu akan maaikatar yake.

Fatima dayake basa shiga huldodin mutane taji hayaniyar sama sama amma bata fito ba duk da ba baccin takeji ba kirjinta kawai takejin yayi mata wani irin nauyin gaske kamar numfashinta zai dauke,

Ga Abdul a gabanta sai wani irin gumi yakeyi kamar yana mafarki mara dadi.

Hannunta da yai mata nauyi ta miqa inda yake kwance kan katifarsa ta tayar dashi tana karanta masa addua.

Bude idanuwansa yayi tareda tashi zaune.

Ajiyar zuciya ya ringa jerowa yana hada zufa tana share masa kafin tace

"Tashi je ka wanko fuskarka kayo alwala kazo kayi sallah kayi mana addua ni banajin dadi."

Miqewa yai ya nufi kofa ya fito tsakar gidan wanda yana fitowa abind kunnuwansa suka fara ji shine ihun da mutane keyi suna cewa

"GOBARA TA KONA GIDAN ROBAR SU AYOUBA" kalmar da harya mutu bazata taba fita daga kansa da kunnuwansa ba.

Faduwa gabansa yai tsoro me tsananin gaske ya shigesa ya juyo da sauri zai kalla ummansa ashe itama ta jiyo hakan.

Tana fitowa tsakar gidan ko takarmi bata tsaya sakawa ba ta nufi kofar fita gidan tana saka hijabin dayake hannunta.

Bayanta Abdul din yabi jikinsa na rawa tsoro na shigarsa.

Tafiya takeyi kamar mahaikaciya Abdul na riqe da hijabinta batareda sunsan insa suke jefa kafafunsu ba.

Fitarsu gidan ashe ana ankare dasu suna yin nisa aka fada gidan aka kwashe musu kusan fiyeda rabin kayansu da abubuwansu harda katuwar katifarsu.

Tafiya me dan tsayi sikai tin daga nesa taji ana fadar wanda suke ciki mutum uku ne sedai ayi hakuri dasu dan kam babu ta yanda zaa iya fiddasu.

Sarewa kafafunta sikai ta kife a gurin Abdul yayi saurin kamota jikinsa na rawa yana kiran sunanta.

Da rarrafe ta qaraso Abdul din na kamata duk da tafi karfinsa.

Da sauri aka riqeta tana kokarin yi cikin wutar tana kiran Ayoub da karfi jikinta na wani irin rawa da tashin hankalin dayake neman juyar mata da kwakwalwa.

Abdul ma kuka yakeyi sosai yana kiran sunan babansa shima yana kokarin tafiya ana riqesa yana ihu me karfin gaske.

#MAMUH

#LIMBAS

#BESTYSTORY

#BESTLOVE

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

7

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😄☹Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Gawar da aka jera part part dinta kamar gawayi a gabansu ne ya saka ummansa somewa a gurin shima zubewa yayi a gurin yana wani irin jijjigar data saka daya daga cikin abokan aikin baban nasa dake gurin rungumesa ya qanqamesa da karfi yana kira masa sunayen Allah tareda addua.

Umma kuwa maza ne suka zuba mata ruwa a gurin sbd babu mata a gurin dan girman lamarin itama dan tanada dolenta ne a cikin wutar ta iso gurin batareda ta sani ba.

Tana farfadowa ta sake somewa jini na balle mata a gurin wanda babu wanda ya lura sbd duhu da kuka tashin hankali duk da anriga anyi asuba a lokacin.

Abdul dinne ne da aketa tofawa addua ya lura da umman tasa da gudu yayi kanta yana kallan jinin daya bata kayanta.

Daidai nan sakina ta iso gurin cikin matsanancin tashin hankalin daya sake daga hankalin Abdul da tsoro sbd kwasar umman da akai zuwa gida hankali tashe.

Suna isa gida mama sakina cikin gaggawa ta taimakawa fatiman jinin ya tsaya ta kwantar da ita tana karanta mata yan adduain data sani tinda ba wani ilimi me zurfi ne dasu sosai ba.

Rasuwar Ayouba tayiwa fatimar mummunan dukan daya saka cikin da basusan dashiba kusan zubewa,

Ayoub ne gatanta,

Ayoub ne a matsayin uwa da ubanta da danginta sbd batada kowa bayan kawunta wanda ya aurar da ita ya tattarata ya watsar sbd daman neman hanyar rabuwa yake da ita ya huta daga wahalar dayake ganin yanayi da ita.

Ayoub baida uwa baida uba sai yan uba da matan mahaifi wanda sukafi son balai akansa,

Waye zai zama gatanta dana yayanta a duniyar yanxu?

Abdul yayi kuka yayi kuka harya rasa ya zaiyi wani kukan sbd gawar mahaifinsa da aka jera masa baisan yaya zaiyi da ita ba,

Durkusawa yayi gaban gawar yana sake fasa wani sabon kuka kirjinsa na wani irin radadin da baisan mene ba.

Baba Ahmed wanda yake abokin aikin baban shine ya karbi ragamar komai sbd karfe tara na safe ma ta kusa kusan dukkanin maaikatansu na nesa da kusa sun iso tardda yan kallo na kauyen da makotan kauyen dan haka ba bata lokaci akai taho gida aka hada gawar aka yayyafa mata ruwan wankan gawa sbd bazaa iya maza wankan ba aka hadasa a farin likafaninsa aka nade akai masa janazah a kofar gidansa inda ya samu mutane daidai gwargwado sbd a cike kauyen yake ranar da mutane sbd abinda ya faru.

Tinda Abdul ya rungumi gawar babansa dayake nade a kyalle yaji zuciyarsa na wani irin ciwo da nauyi kaman zata zazzago tareda wani irin radadi kaman tana bushewa.

Kukansa daukewa yayi tsaf saida aka dawo daga kai baban ya dawo gida shi kadai batareda wani ya biyosa ba yana shigow gidansu ya tararda ummansa kwance daga ita sai mama sakina da wasu daidaikun mutane da suka gama gaisuwa suka miqe suka fice.

Tahowa yayi ya zauna gefen ummansa wadda ta dago jajayen idanuwanta da sukai mata tsananin nauyi ta xuba masa shima ita ya kalla ya sunkuyar da kansa wasu hawaye masu tsananin zafi suka gangaro masa suna sauka qasa gabansa.

Mama sakina ma kasa riqe kukanta tayi tafara hawaye masu zafi tana rufe fuskanta da tafukan hannayenta.

Duka a cikinsu babu wanda ya damu koma tsayawa tantance irin satar da akai musu a gidan bayan fitarsu mama sakina ma data lura batai magana ba sbd radadi da ake cikinsa.

Shiru gidan yayi har yamma babu wanda ya sake shigowa gidan sedai ayi sallama abdul din ya fita idan abokan aikin baban sukazo amma ko yan gidansu Ayoub din tinda safe suka zo akai komai dasu daga nan suka watse kowa yake harkan gabansa.

Mama sakina tayi abinci tayi duk dubaran da zatai suci babu wanda ya iya cin komai a tsakaninsu dan haka ta hakura itama bata iya cin abincin ba sbd har cikin rai da

jininta take jin ciwo da radadin da fatima ke ciki sbd kaunar datake tsakaninsu me girman gaske ce wadda suka taso a cikinta tin yarinta sbd itace ta zama kamar gatan fatima tin suna qananu har girmansu sbd ita tanada mahaifiya sabanin fatima data taso ba uwa ba uba.

A gidan mama sakina ta kwana duk aike da fadan da baba ila yai mata bata koma ba dan haka ya zuba mata ido yaga gudun ruwanta.

Washe gari da safe shugaban gurin aikinsu Ayoub din ya taho gaisuwa ya kawo musu abinci sosai da abubuwan buqatarsu tareda biyan kudin makarantar Abdul din wadda yake a local government harya gama.

Yaso bada kudin dayake ganin kaman diyya ce zai biya amma ganin Abdul din yaro ne kuma matar ayoub din batada me tsaya mata hakama yan uwansa sun saka zalamar jiran ya bayar sai kawai ya fasa ya fadawa baba Ahmed idan Abdul din yagama karatu ya isa fara business zai basa da hannunsa insha Allah kuma zai rubuta hakan ya ajiye koya mutu bashi ne Abdul yake binsa zaa basa.

Babu wanda yasan da hakan sai baba Ahmed wanda yayi naam da hakan dan haka bayan tafiyar alhaji Kabir din shima Ahmed tafiyarsa yayi sbd ba maganar aiki a gurin yanxu sbd kamfanin dai ya mutu mutus sai ansake sabon ginin ma dan haka yanzu maaikatan duk sun tafiyarsu sai kuma an sake ginin kamfanin akan wannan tukuna.

Kwanan mama sakina bakwai a gidan yan kauyensu suka taho gaisuwa da matan kawun fatiman dashi kansa da wasu yan uwan sakinar da yawansu.

Fatima a cikin kwanakin ta zama abar tausayi sbd abinci ma bata iya ci haka kawai cikin jikinta ya hanata lfy sbd damuwa da tsananin quncin da zuciyarta take ciki.

Abdul ganin halinda mahaifiyarsa take ciki shima ya tabasa dan haka kwata kwata baya cikin walwala ko kadan daman babansa shine abokinsa kuma abokin wasansa sbd baya fita koina wasa bai sababa tin tasosawarsa.

Mama sakina ma bata cikin walwalan kwata kwata sbd ganin halinda suke ciki dan haka bayan yan garinsu sun koma itama ta koma gida sedai duk bayan kwana daya sai tazo ta dubasu.

Kawun fatiman da zai tafi ganinsu da abinci sosai baiji tausayi ko kunya ba ya diba abincin sosai ta tafiyarsa.

Yan uwan ayoub din ma da sukaga hakan suma suka taho suka debi abincin me yawa sosai da cewa ai suma sunada gadon Ayoub dan haka tinda baibai komaiba a basu abincin.

Abdul ne rayuwarsa tafara sauyawa sbd karatunsa daya fara rawa sbd kulawa da mahifiyarsa wadda ta kasa dangana da rashin baban dan haka lafiya kwata kwata tafara kaurace mata,

Ta rame ta koma kamar wadda bata taba lafiyaba rayuwarta,

Bata wani ci bata wani sha bata cewa komai sai dole ga cikinta yanata girma dan haka komai a gidan shine yakeyi masu,

Shine yake musu wanki,ya dafa musu abinci,ya kai mata ruwan wanka yayi shara ya nemo,ya kuma tafi makaranta,sannan ya zauna yasha kuka a duk lokacinda ta kasa riqe abinda takeji tafara kuka haka yake yi a tareda ita,idan ciwo ya taso mata ma shine me zaunawa ya kula da ita ba magana haka zatai ta warke sbd basuda komai.

Ahankali baba ila ya gaji ya hana sakina zuwa gidan kaman yanda ta saba dan haka duk abinda suke buqata sedai Abdul din yake ya karbo musu dan abincin da zasu ci da wasu abubuwan kaman sabulun wanka ko omon wanki.

Hakan ma baba ila ganin yayi kaman zaa karya tattalin arzikin gidansa duk da na sakinar ne take basu dan haka ya haukace musu yace ya hana,

Ahankali rayuwa tafara yi musu tsananin gaske sbd komai basuda shi basuda me basu basuda hanyar samu,

Umma ta koma masa kamar me tabin hankali yau lafiya gobe ciwo kwata kwata batada sauran lafiyar ma da zata san tawakkali da dangana bare tasan itace ya kamata ta dauki juriya ta kula da Abdul ta tsaya masa sedai shine ya koma ya tsaya akanta.

Tsana me tsananin gaske Baba ila da yan gidansu Ayoub sukai masa sbd yanda tin yan yaro ya tsayu kan uwarsa gashi yai neman taimakon a gurinsu amma sun bayyanar masa da tsanar da sukaiwa mahaifinsa a fili dan haka sai yaji yafisu jin tsanarsu me tsananin gaske dan haka bai sake ko bi ta hanyar kofar gidansu ba Dan yafison mutuwa ta daukesa kaman yanda ta dauko babansa daya sake zuwa gurinsu.

Baba ila kuwa sbd tsananin kaunar datake tsakaninsu da mama sakina dayake jinta kaman ummansa data haifesa yasa yake danne ciwo da radadin tsanar da yayi musu sbd mama sakina ta tabbatar masa har abada kada yace zai rabu da ita sbd itama uwarsa ce ko fatima na raye ko bata raye.

Rayuwa tafara yiwa mama sakina tsanani itama sbd baba ila daya dena bata komai sbd kada ta taimaka musu daman matansa da yayansa kwata kwata basa kaunarta,

Abincin da zata ci kansa ankoma a gidan a qaramar roba ake bata shi wanda ita kanta baya isarta amma a hakan wata ran take juyewa a leda ta bawa Abdul din ya kaiwa fatima wadda da kansa yake bata itama bata wani ci kadan take ci sbd yanayinta.

A haka ya dage yana karatunsa duk da wata rana yaje ne wata ran baya zuwa amma a hakan yana kokari sosai

Suma malamansa da suka gaji da dukansa aka fahimci tsananin rayuwar dayake ciki sai aka dena dukansa aka barsa a hakan idan yazo shikenan idan baizo ba shikenan.

Mama sakina ta koma sabulun da zatai wankan ita kanta batada shi batada ko man shafawa masifar rayuwa tafara sakota gaba dan haka Abdul din daya fahimci hakan saiya rage zuwa kwata kwata gurinta yafara aikin wahala da wanda zai iya da wanda bazai iyaba haryafara sabawa idan ya samo yana dan siya musu harma da ita mama sakinan yana bata omo ko wani abin idan ya siya musu.

Sun wayo gari sitirar sakawa tai musu wuya daga shi har ummansa sbd sata da aka ringa sakasu gaba da ita saida suka rasa komai a gidan bayan tabarma data mutu sai karamar katifar da itama ta mutu sai kuwa buta daya da bokitin wanka da tukunya shi kadai suka rage musu.

Cikin ummansa ya tsufa harya wuce lokacin haihuwa a lokacin ne katangar gidan ruwa ya zubar musu da ita aka sace duk kwanon langa langar gidan da sauran abubuwan dan haka suke a rabe a gefe cikin gidan wanda har dakin da suke ruwa yake daga saman sbd har saman anhau an sace langalanga kadan aka bar musu dan haka idan ana ruwa suna gefe dan ruwan yana dan shigowa kadan kadan ta sama.

#MAMUH

#BESTLOVE

#BESTROMANCE

#HOT

#STRUGGLE

#BILLIONAIRES WAR

#AY LIMBA

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

8

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😄☹Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse

mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Koda cikin Fatima ya isa haihuwa karfin da zatai naqudar arziki batada shi sbd yunwa da ciwo tareda cikin da duk ya janyeta ta koma kana ganin qashin bayanta ya fito dosai da duk qashin kirjinta kana ganinsu idanuwanta sunyi ciki sosai tayani muni dik ya gama sauya kamanninta sbd ciwon da yunwar da bayan Allah da yayita babu abincin da zai dawo da ita yanda take kila.

Abdul yana kokarin daya fi na shekarunsa sbd har local government yake zuwa nema da aiki harma da tallan rage wadda bayayi da yawa sbd baya iya dadewa waje yake komawa gida gurin ummansa dan komai shine yake mata sbd baba ila ya rabasu da Mama sakina wadda take cikin tsananin daci da ciwon rai na hakan amma Abdul dinne ya roketa akan kada ta rabu da baba ila sbd su shiyasa kawai take zaune a gidan amma aurensa gabaki daya ya fita daga zuciyarta ba sauran sonsa ko qwaya daya a ranta gashi daman Allah bai bata haihuwaba tayi neman haihuwar harta gaji ta barwa Allah.

A cikin wannan halin da suke ciki ne Allah ya kawowa Umman naquda cikin ciwo da ukubar rayuwa tareda yunwar data gama kame duk wani kayan cikinta da gangar jikinta ta haihu,

Haihuwar data taho musu da sabuwar kaddarar da babu yanda zasuyi bayan rungumar rayuwa a yanda taxo musu batareda taimkon kowa ko kulawan kowaba bayan ta mama sakina da suke samu jefi jefi Abdul ya reni kanwarsa da mahifiyarsa wadda ta koma masa tamkar UMMITA wadda take yar shekara biyu zuwa uku dan kuwa duk inda zashi dasu yake zuwa sbd fita sukeyi su tafi yawo dan haka duk inda zashi yanzu suna tare dan haka da yawa ake musu kallan almjirai ko yan yawon neman sadaka duk da yana iya kokarinsa akansu gurin ganin ya tsaftace su.

Yanzu sun dena zuwa irin guraren dake kaman kasuwa ko tasha gurin aikin nema ko sanaa sbd bayason ana kallan ummansa da ummitan dan haka Local government yake zuwa dasu har makarantarsa wadda yake gaf da kammalawa yanzu.

Har ciki a ke barinsa shiga dasu saiya kaisu bayan ajinsu yace su zauna karsu tashi saiya gama ya fito.

Haka zasu sauna suyita wasa a gurin harya gama batareda da damuwa da abinda dalibai ke fada akan mahaifiyarsa da rabin ransa dayake jinta kaman shine babanta sbd BAABAH take kiransa dan bata san kowa ba bayanshi da ummanta hakama shi take kallo ubanta tinda umman ta koma kaman ita tare suke wasa duk da umman ta dena magana.

Daga makaranta shagon dayake aiki yake wucewa dasu ya siya musu abinci suci ya ajesu guri daya suyita walwalansu harya gama se yamma su nufo gida sbd baya kaiwa dare sbd su duk da megidansa yana son ya ringa kwana shagon sbd yadda dashi da yayi da kuma kokarinsa tareda amanarsa amma sam baya iya hakan sbd kare mutuncin ummansa da Ummitansa dan haka duk abinda yake samu a aiki ko sanaa yamma nayi yake wutowa gida dasu su wanka suci dan abinda ya samu ya ringa koyawa ummita dan karatun yara har suyi bacci itada umman ya gyara musu gurin kwanciya ya kaisu su kwanta shima ya zauna gadinsu dan baccinsa rabi da rabi ne akansu sam bayada wata irin yadda da kowa gashi basada koda rabin gidan a zube dan haka baya wani bacci akansu.

Ranar wata alhamis ya samu wani aiki a wani sabon kamfani da zaa gina a local government na gyaran shinkafa me kudin dayafi tsaron shagon dan haka ya karba ya hada biyu yana yi sedai aikin gurin akwai hadari dan haka dole yake barin su ummita a gida amma saiya fada musu yafi so ashirin kada su fita koina.

Sunji maganarsa basa fita dik ya tafi harya dawo baya cikin nutsuwa amma yana tarar dasu a gida basa fita koina sedai gidan zai tarar anyi masa kaca kaca hakama sunyi wata irin dauda hakanan zai tsaftacesu ya gyara gidan ya basu abinci suci su koshi suyi sallah wadda tasa ce kawai ta arziki su kam ture ture sukeyi a gurin sallan tsakanin umman da ummita yana jinsu zai kyalesu a gama a hakan.

Akwai wata irin kauna da so me tsananin gaske tareda shaquwar datake basa tsoron da baisan na mene ba a tsakaninsa da Ummansa da Ummitansa haka suke

sakasa wasa dasu dole wanda su kadai ne suke ganin dariyarsa da walwalwansa dan Allah ya sako masa wani irin kame kai tin yana yaronsa shiyasa ya taso hakan.

Tin yana fargaban barinsu a gida yaje ya dawo harya dan rage fargaban yana aikinsa cikin dan nutsuwa amma bawai hankalinsa baya gidan bane dan baya kara ko minti daya yana tashi aiki yake komawa gidan dan ya dena zuwa makaranta exam kawai yake jiran ranar yinta yazo ta gamawa tinda suka shiga ss3 ya dena zuwan waec kawai yake jiran yi.

A yau tinda ya kamo hanyar zuwa gida yakejin baida nutsuwa dan haka ya qara sauri yana jin kirjinsa na nauyi ya kuma saba da hakan a duk lokacinda bay taredasu jin yake zuciyarsa ta ringa shiga damuwa da nauyi kenan.

Yamma ne sosai dan haka bai biya gidan mama sakina ba dan bata sabulu da omon daya siyo harda ita ba dan haka ya wuce gida saiya dubosu saika ya fito dasu yaje ya kai mata batareda ya shiga gidan ba san anjima da baba ila yai masa iyaka da shigar masa gida sedai ya tsaya daga waje gefen gidan mama sakinar ta fito ko kawai ya aika mata ummita ta shiga takai ta fito shikuma yana waje yana jiranta su koma.

Yana doso gidan tin bai karasa ba ya hango Ummita tana fitowa daga hanyar bayan gidansu tana kuka hannuwanta da kafafunta qasa da jini.

Wani irin abu ne ya daki kirjinsa da tsakiyar kansa dan haka da sauri ya qaraso ya tarbeta tareda ajiye kayan hannunsa ya jawota gaba daya jikinta yana kallan hannuwanta muryansa dayake da wahalar ji shima dan baya wani magana sosai sbd baida abokin firar yace

"Ina ummah?

Meya faru?

Kuka takeyi sosai ta juya bayanta ta nuna masa hanyar data fito tana cewa

"Umma ta tafi,

Dodo ya bita da gudu ta tafi.....

Wani mummunan yawu me dacin gaske ya hadiye yana daukan ummitan ya nufi hanyar data nuna batareda ya tsaya fahimtar me take fadaba yana jin kaman kansa zai zare.

Duhun magriba yayi amma sam baya ma gani ya doshi hanya yana tafiya yana duba umman kaman zai zai haukace a take yaji yana ji dan haka ummitan dake jikinsa ya sake qamqamewa yana jefa kafarsa duk inda ya samu yana adduar Allah kada ya jarabcesa da wannan jarabawar me girman gaske akan mahaifiyarsa da ita da ummita sune rayuwarsa da hasken dayake gani a wannan rayuwar ko yaya ummansa ta koma yana tsananin buqatanta a hakan.

Tafiya yakeyi harya isa wani kauye duhu yai sosai amma kwata kwata baya hayyacinsa.

Kaf kauyen babu ummansa babu wanda ya ganda dan haka ya juyo ya dawo kauyensu lokacin tini akai ishai amma be zauna ba ya zagaye kauyen tas nanma babu umman ga ummita wahala da zazzabin raunikan jikinta sun saka tayi bacci a jikinsa jikinta zafi sosai.

Bai taba shiga mafi munin tashin hankali da firgici irin daren ba na rashin umman amma bai damu da daren ba haka ya doshi wani kauyen a cikin tsananin duhun dare nemanta idanuwansa sunyi wani irin mummunan jajir.

A cikin dare mafi tashin hankali a rayuwarsa kauyuka uku ya zagaye amma kwata kwata babu ummansa babu wanda ya ganta dan haka ya yanke jiki ya fadi qanqame da ummita zazzabi me mugun karfi ya gama gabalaitar da ita a jikinsa.

Jamaar kauyen daya somen suka yo kansa sbd lokacin har anfito sallan asuba gari ya waye sosai suka yo kansa suna son cire ummita a hannunsa amma yai mata wani irin mugun riqo da dole tana jikinsa aka zuba musu ruwa a tare.

A tare suka sauke ajiyar zuciya sedai kowannensu a galabaice musamman ummita shi kuwa ganin yayi kaman baya ganin komai sbd azaba da wahala tareda galabaita da tsananin tashin hankali.

Tashi zaune yayi yana gyarawa ummita zama a jikinsa yana sake rungumeta da kyau wasu zafafan hawayen daya manta rabonsa daya zubo suka gangaro daga fararen idanuwansa da suka koma jajir ya ambaci sunan umman ahankali yana rokon ALLAH ya kawo masa kowacce irin jarabawa indai ummansa zata dawo garesa zai jure ya runguma kaddarar.

Tausayinsa ne ya rufe jamaar gurin dan haka aka taimaka masa aka tayasa bincika neman umman tasa a kauyen amma har yamma babu labarinta kuma har dayan kauyen suka tayasa nemanta amma babuta.

Kauyensu ya nufo ummita na jikinsa a some sbd ruwan saman da akeyi sosai duk ya qare akansu.

Koda ya dawo kauyensu ana sallan ishai duhu yayi sosai,

Kofar gidan ya shiga wanda ruwan sama ya cika gidan kai tsaye dakinsu ya nufa ya bude ya shiga

Taku daya yayi zuwa biyu kafafunsa suka kasa daukansa ya zube a gurin yana fasa wani irin kuka me karfin gaske Ummita dake jikinsa azaba ta farfado ta bude idanuwanta daqyar batada karfin motsawa anan ta sake lumshe idanuwanta suka rufe jikinta ya sake sakewa alaman ta sake fita hayyacinta.

Kuka yakeyi sosai yana wani irin jijjiga zuciyarsa kaman zata fashe akan abinda yake ji,

Shima zazzabine sosai me karfin gaske a jikinsa amma ya kasa sakin Ummita barema yasan shika halinda yake ciki.

Kuka me yawa sa karfi sosai da idan da ba ruwa akeyib kusan duka makotan dake kusa sai sun jiyosa amma karfin ruwa bai bari anjisu ba.

Ummansa yasan a duk inda take tana cikin wannan ruwan da duhun dare wanda zai firgitata ta qarasa haukacewa mutane su kyareta su qyamacet su hantareta shikenan ta shiga gagarin da babu wani gata ko rufin asiri gareta.....

Wannan ke saka zuciyarsa daukan wani irin nauyi kaman zai haukace shima yakeji ya fasa kukan da babu me jinsa bayan Allah dayake fatan ya kawo masa dauki da sassauci a wannan rayuwar.

Tsakar dare sosai ya dago jajayen idanuwansa da sukai nauyi da kumbura ya kalli ummita datake a sake jikinsa ya miqe ya koma gefen da babu sanyi a adakin ya gyara gurin kwanciyarsu ya kakkabe duk da baya ganin komai ya sauya mata kaya sbd na jikinta akwai sanyi ya kwamtar da ita.

#MAMUH

#BESTSTORY

#BESTLOVE

#BROTHERS LOVE

#LIMBAS

#ZADEENS

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

9

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Tashi yayi ya fito cikin duhun ya sauya kayansa yaje toilet ya fito yayi alwala ya dawo dakin

A gefen ummita yayi sallah yafara sabon kuka yana fadawa Allah ummansa kadai yake fatan Allah yabata kyakkyan kariya tareda fatan dawowa garesa.

Har akai asuba yana fadawa Allah ummansa tareda neman jariya da yadda da duk kaddarar da zata tinkarosa a rayuwa ya basa ikon inganta rayuwar Ummitah har mutuwarsa.

A gida yayi sallar asuba bai fita ba kaman yanda yakeyi a baya,

Yana gamawa ruwan zafi yai dubara ya dora yazo ya gasa ummita dasu sosai ya mayar mata da kayanta ya fita yaje ya samo mata koko da kosai ya dawo ya bata kaman ma dura mata yayi.

Bai gama bata ba tayo masa amansa a jikinsa ya tashi yaje ya gyara mata jikinta ya sakeyi wanka shima ya sauya kaya ya sake bata kokon amma wannan karan batai masa amansa ba dan haka ya kwantar da ita tayi bacci har lokacin jikinta akwai zazzabi.

Basuda wasu kayan dan haka ya wanke musu wainda duka lalace sbd kada su fita dana jikinsu su dawo babu wasu na sakawar dan haka yana gama shanyawa ya dauketa suka fice.

Local government ya nufa acan yakaita wani chemist aka dubata akai mata allura aka basu magani ya siya mata bread sa freshYo na roba shikenan kudin hannunsa suka qare suka zagaya sosai nan ma ya bincika ummansa amma ba labari sai yamma sosai suka dawo gida.

Kwantar da ita yayi ya gyare gidan fes kafin yayi sallan magrib suka shige dakinsu ya rufe.

Yana yin sallan ishai kadan yaci bread din data rage da ruwa ya kwanta gefenta tareda rufesu sai a lokacin wani baccin azaba shima ya daukesa.

Seda aka fito sallah ya farka yayi sallah yayita addua har gari ya waye sosai ya fito baida ko sisin siya mata abinci dan haka ruwan wanka kawai ya samar musu sukai wanka ya dauketa suka fice zuwa gurin aikinsa.

Koda ya isa sbd rashin zuwansa kwana biyu tini aka saka wani a maimakonsa dan haka sedai ya tayasu suka dan hada masa dan abinda ya samu ya siyawa Ummitan Wainar gero taci yabata magani daganan ya nufi shagon dayake aiki a baya ko zai samu a karbesa suma.

Yama xuwa shima ya riga ya samu wani amma dai yace ya tsaya ko miqa abu ne idan an siya ya taya wanda yake shagon yanzu a dan ringa basa wani abin.

Haka ya zauna a bakin shagon da ummita wadda take lafe jikinsa har dare suka kai kafin ya basa 200 ya dawo gida.

Suna dawowa tuwo ya siya mata da 200 din taci kadan tasha magani ya cinye sauran yasha ruwa yai sallah ya kwanta.

Washe gari ma haka ya tafi ya ringa yawo garari da ummita yana dan kama aiki ana basa abinda zai siya mata abinda zataci saita rage yaci wani lokacin kuma ruwa kawai yakesha ya dawo su kwanta.

****rayuwa tai masa tsananin gaske dan kuwa daga shi sai ummita suke rayuwa yayi yawon neman umma har inda bai kamata suje ba sunje ba labari dan haka ya

maida hankali sosai gurin tattalin Ummita wadda ita kadaice hope dinsa na rayuwa a yanxu,sbd ita ya dage yafara gwagwarmaya da rayuwa,

Tin dafe idan suka fita da ita yake yawon aikin wahalar dayake fama dashi se dare suke dawowa su shige su rufe gari na wayewa suke fita sai kuka wani dare.

Wahalar rayuwa yakesha sosai ga kulawa da ummita wadda ya kasa barwa ko mama sakina sbd tsoron bazai iya rayuwa ba ummitan a tareda shi ba dan haka yake gwagwarmayarsa da ita a gefensa duk da tafara qara wayo sosai kuma itama bata iya rabuwa dashi ko nan da can dan hakama sbd bata tsaro da kariya ya aske mata kanta daman batada yan kunne ya siya mata kayan gwanjo na maza ya maidata namiji sunanta kuwa kwata kwata baya fada cikin mutane kaman yanda ya hanata magana a cikin mutane sbd muryanta.

Ana cikin ya fara examsa dinsa dan haka tare suke zuwa makaranta ya zaunar da ita bakin window dayake ganinta har a gama ya fito ya jata su tafiyarsu gurin yawon nema.

Rayuwa tayi musu nauyin da duk kansa yafara neman kuncewa amma ya riqe sbd Ummitah dayayiwa kansa alkawarin inganta rayuwarta bazai bari insha Allah ta taso cikin qunci da azabar daya taso a cikinta ba,

Shine uwa kuma ubanta dan haka ko rayuwarsa zai iya siyarwa dan inganta tata.

***Ummita a tata rayuwar batada wani hasken data sani bayan BAABAH dinta wanda shi kadai ya isheta rayuwa, ya isheta jin nutsuwa da ganin haske arayuwar ba duhu ba,

Shine uwa kuma ubanta wanda take ganin indai gashi bata buqatan komai hakama shi kadai ne abinda take buqata a rayuwarta.

Daqyar ya kammala exams dinsa sbd babu lokacin zuwa aiki dan haka abincin dazai bawa ummita bama kansa ba yake musu wuya dan haka koda aka gama exams din

yayi wani irin rama daga shi har ummitan sun bushe dan haka yana gamawa ya duqufa aikin kamfanin daya sake samu da tsaron shago yana hadawa biyu sai suka fara daidaituwa.

Ahankali abinci yafara wadatarsu kullum sunaci su koshi ya siya mata abubuwan buqata da nasa ma.

Ya siya musu katuwar fitila basa cikin duhu ko kadan yanxu,

Ya siyawa kansa waya yar qarama sbd jamb daya rubuta da kuma jiran kiran fitowar jarabarsu.

Rayuwarsu tafara daidaituwa shine malamin Ummita na karatun addini harma dana bokon dan haka tafara koyan karatu a gunsa kuma tana ganewa sbd yanada qwaqwalwa sosai dan duk tsananin rayuwar da suke ya tsaya ya samarwa kansa ilimi sbd burin dayake dashi akanta.

Mama sakina na cikin tsanani a gidan aurenta sbd baba ila daya tsaneta gaba daya tinda ta kasa cire su abdul a ranta duk ta rame ta qare akan tinaninsu da rayuwar da suke wadda bata cikin nutsuwa da kwanciyar hankali kwata kwata sbd Abdul rayuwarsa ta qare ne akan kulawa da ummita hakama bazai tabbata boyeta a amtsayin namiji na sbd girmanta idan yazo zai nuna hakama tayaya zaici gaba da iya kulawa da ita shi kadai dan haka take cikin damuwa me tsananin gaske da kuma batan Fatima daya tabata itama ta rasa kwanciyar hankali kwata kwata.

Baba ila gaba daya ficewa tai a ransa sbd babu dadin zama da ita tinda ta saka ranta a qunci sbd yayan da ba ita ta haifa ba,uwarsu ta tsallakesu ta gudu sai itace zata kawo masa qunci gidansa sbd su duk tabi ta bushe babu komai a jikinta hatta gatanta jin yayi ya bushe masa dan haka ta fice masa kwata kwata a rai ko abincin ma seya dena bata azaba kawai take sha a gidan da baqin ciki tareda hantara da tsana da gori.

Abdul bai taba zuwa ko sake barin hanyama ta hadasa da yan uwan babansu ba sbd babu abinda yake buqatan dayafi kada Allah ya hadasa dasu harsu bar kauye dan haka kwata kwata baya hulda da mutane ko shiga mutane sosai kaman iyayensa ya

killace kansa daga shi sai kanwarsa wadda itace tafi masa duk wani abu dayake duniyar nan.

A gurin aikinsa ahankali yafara zamowa abin kaunar kowa sbd nutsuwa da kamun kansa da kuma maida hankali kawai akan aikin daya kawosa.

Tamkar yanda mahaifinsa yake da farin jini da kwarjini haka yafara cika idanuwan mutane duk da shine qaraminsu a kaf ma'aikatan gurin hakama sbd rufin asiri daya fara samu da cimar safe rana dare sai yafara zamowa lafiyayyan saurayinsa wanda haskensa na bafulatin asali suka fara fitowa sosai.

****examsa dinsu ce ta fito wadda tayi kyau sosai kusan fiyeda ta kowa a makarantarsu dan haka yake cikin farin ciki.

Rayuwarsa ta qara zamowa akan tsari ne a lokacinda ya samu admission dinsa a university of lagos wadda acan ya cika sbd yanason koyan gwagwarmayan nema,

A daidai wannan lokacin ne baba Ahmed ya kawo musu ziyara sbd rasuwar da me gidansu yayi dan yazo ya tafi dasu da takardar da akai ta kudinsu da zai basu zuwa abuja.

Sam Abdul bai nuna ummita mace bace a haka suka tafi har abuja bayan tafiya me tsayi suna isa aka saukar dasu gidan wani dan uwan baba Ahmed wanda yake gadin wani gida da babu kowa a cikinsa.

Sai washe gari suka isa gidan alh kabeer inda babu wahala bayan sunyi gaisuwa daman ansan da zuwansu babban dan Alhajin ne ya nema Baba Ahmed sbd takardar da dad dinsa ya basa a hannunsa tasu Abdul din dan haka ba wani wahala aka basu dukiya me yawan gaske.

Kafin su tafi kwanansu shida a abuja Alhaji Sa'ad 'dan Alhaji kabir din yaji kaunar Abdul kaman yanda dad dinsa yaji yana kaunar Ayouba a can bayan dan haka bae bari sun tafi ba yai masa tambayoyi yaji yana shaawar sakasa a business dinsu sbd Alhaji Kabir ya rasu bayan doguwar jinya wadda sanadin businesses dinsu ne da sukai qasa sun karye sosai dan haka ciwon zuciya ne da Diabetes ya kwantar da Alhaji wanda sukaita yawon kasashe sauran dukiyar duk ta qare daga qarshe koda ya rasu basuda wani abin daya dage musu bayan gidan da suke ciki a yanzu.

Amma sbd sauke nauyi da biyan haqqi ya sakasu saida duka motocin gidan suka hada kudin da dad dinsu yayi alkawarin bawa su Abdul wanda yake ganin haqqinsu ne dole ya basu suka nemesu dan basu,

Amma ganin nutsuwar Abdul din wanda idan suka basa duka kudin zasu koma ko abinda zasu juya basuda shi gashi shima Saad shi kadaine namiji a gidan sauran kannensa duka mata ne sai mahaifiyarsu dan haka ya gabatarwa Abdul kalar business dinsu na companies din shigowa da manyan qarafunan manyan motoci daga kasar waje da kuma kamfanin Qera nasu da suke dashi tareda bayyana masa komai na business da kuma yanda ake tafiyar da huldodin duka a gaban baba Ahmed da lawyer dinsu.

Abdul daman bai saka kudin a ransa ba bare saka lissafinsu a ransa dan haka yace ya bar musu amma a saka baba Ahmed a cikin huldan ya basa kaso daya a bisa uku na dukiyar shima ayi dashi.

Gabaki daya familyn gidan jin farin ciki da tsananin kaunar ABDULAZIZ sukai musamman Alhaji Saad dayaji ABDULAZIZ ya zama kaman wani savior dinsu.

Baba Ahmed ma jin yayi yana zubarda hawayen farin ciki sbd yana cikin gararin rashin aikin yi shima sai wahalar rayuwa yake sha shiyasa kunyar su Abdul din ta hana ya fito ya taimakawa rayuwarsu.

#MAMUH

#LIMBAS

#ZADEENS

#BESTLOVE

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

10

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Lawyer ne a gaban kowa yayi drafting komai da yawan adadin kudin da date da cikakken sunansa ABDULAZIZ AYOUB LIMBA sai sunan Saad din da baba Ahmed kowa ya saka hannu.

Anan aka saukesu suka baro gidan dan uwan baba Ahmed akai musu Kyakkyawan sauka wanda anan gidan ne aka gane Ummita mace ce dan haka umman gidan taiwa ABDULAZIZ din karfin halin rabasa da Ummitah ta dawo da ita cikin gida gurinsu.

Sosai suka ringa kulawa da Ummitah da tattalinta babu qyama tareda siya mata yan kayan sakawa aka gyara mata hujin kunnanta da harya rufe.

Satinsu hudu a abuja suka tattara suka dawo duk yanda Saad yaso ABDULAZIZ ya zauna anan abuja cewa yayi aa sbd makaranta da zai tafi bazai iya barin ummita anan dinba ya tafi karatu yabarta a gurin wainda bai saniba.

Bayan tafiyarsu suna dawowa gida da kwana biyu yaje ya sanarwa mama sakina karatu zai tafi.

Tashi hankalinta yayi mummunan yi sbd batasan tayaya ABDULAZIZ din zaiyi tinanin tafiya da Ummitah karatu ba har nesa dan ita batama san lagos din ba a baki suke jinta.

Shi kansa ABDULAZIZ din yana cikin tsananin damuwa da tashin hankalin yanda zaiyi sbd shi kansa bazai iya zuwa da ita inda yasan ba tsaro ba gwagwarmaya me kalubalen gaske.

Damuwar hakan ce ta sakosa gaba ya koma kalar tausayi damuwa me karfin gaske ta shigesa,

Daga karshe yafara tinanin fasa tafiya karatun sbd Ummitah sbd ta fi masa karatun zai zauna ya reneta.

Wannan shawaran daya yanke ta fasa karatun ya hakura dashi ya saka mama sakina shiga damuwa me tsananin data sake dagula dan zaman datake a gidan baba ila tsangwamar dayake mata tai yawan data saka ciwo kwantar da ita sedai ta kasa samun Sassaucin damuwar datake ciki na fasa karatun ABDULAZIZ din dan haka dataga babu sauyi ABDULAZIZ din ya hakura da karatunsa harya fara aikinsa kwana tayi tana kukan data kasa riqewa tana tina fatima da gatan da aka haifi a Abdul din a cikinsa har safe tana kukan daya sakata qarasa ficewa hayyacinta karshe ta hakura ta sadaukar da aurenta tayiwa baba ila maganar zata karbo Ummitah ta dawo da ita hannunta ABDULAZIZ zai tafi karatu.

Sadaukarwar datai da shahadar masa magana tasan ta tashin hankalin da zata fuskantace tareda Ummitan a gidan dan ko abincin da zasuci ta sani sedai ta fara nemar musu shi da kuma kaurace mata da kila baba ilan zaiyi gaba daya daman ya dade da kaurace mata kumata shirya hakan dan haka tai sadaukarwartai masa magana sedai babban abinda bata zata ba shine kai tsaye tana kai karshen zancenta yace ya saketa saki uku ta tafi can gaba tayi riqon Ummitan.

Dagowa tayi da jajayen idanuwanta na kukan data kwana yi ta zuba masa tsawon mintina tana kallansa harya wuce daga kofar dakinta ya fice daga gidan.

Wasu hawaye ne masu tsananin zafi da ciwo suka gangaro mata ta rintse idanuwanta tana kasa dagowa saiga wani irin kuka me ciwo ya kufce mata zube a gurin tanayinsa ba sauti.

Ta jima a gurin kafin ta miqe ta shiga dakinta ta tattaro yan kayanta da duka buhu daya ne zai dauke mata su sbd ko katifa batada ta siyar tin gurin taimakawa su fatima dan haka tabarmace kawai tsohuwa sai sanin shimfida daya da kayan sawarta da basu fi kala uku ba sai kwanonin da tini suka mutu tin na aurenta shekaru kusan ashirin harma da dori dan haka tana hada kayanta a buhu ta fito taje kuryan gidan tayiwa yan gidan bankwana ta fito suna gulmanta ta fice.

Kai tsaye gidansu ABDULAZIZ din ta nufa.

Basa nan dan haka tinda gidan ba kofane dashi ba ta shiga ta ajiye kayanta ta nemi guri ta zauna.

Sai yamma sosai suka dawo Ummitah na ganinta tazo gurinta da gudu ta rungumeta tana cewa

"Maama"

ABDULAZIZ kayanta ya kalla ya kalli fuskanta take ya fahimci abinda yake faruwa dan haka baice komaiba sannu da zuwa yai mata yana fada mata abinda suka tsaya yi sukai yamma.

Ummita kallan Maman tayi tana cewa

"Mamah anan zaki kwana??

Murmushin karfin hali da boye damuwa mamah tayi tana cewa

"Eh yanzu na dawo dake zan ringa kwana kullum muna rayuwa sbd Baabanki ya tafi karatunsa,

Ai zaki yadda ya tafi ko??

Juyawa tayi ta kallesa yana alwala a natse kafin ta dawo da kallanta akan maman tace

"Eh zan yadda sbd BAABAH na son karatu ya fada a waya naji"

Ajiyar zuciya maman ta sauke sbd tasani idan Ummitah tace bata yaddaba to har abada yabar karatun.

Yana gama Alwala masallaci ya wuce sbd maman na tareda Ummitah.

Baa cika ganinsa masallaci ba sbd acan gurin aiki yake wuni dan haka a masallacin can suke sallah magriba kuma koda yake isowa gida anyi wani lokacin kuma jam'in waje yakebi sbd Ummitah sallar asuba kuma a gida yake binta sbd ba tsaro ya fita yabar Ummitah sbd akwai bata gari ko barayi.

Ayau ganinsa masallaci ya saka kawunninsa mamaki sedai ko alaman ganinsu baiyiba sbd bayama gane kamanninsu sbd rabonsa da ganinsu yama manta tin yana karaminsa.

Saida yayi ishai ya dawo gida sbd saida yayi karatun qur'ani.

Koda ya dawo maman ta dafa musu shinkafa da mai da yaji dan haka ya zauna a tsakar gidan sukaci suna gamawa yayi kwanciyarsa a kofar dakin da tabarman maman datazo da ita ya kunna maganin sauro guda biyu ya zagaye kansa dashi yabar musu dakin sbd gidan dakin daya ne tini ya rage sauran sun zube.

Washe gari gurin aiki ya tafi yabarsu gida ummita nata murna sbd mama zata zauna dasu.

Se dare ya dawo sbd baya tareda ummita daman sbd ita yake dawowa da wuri.

Tuwo ya samu anyi sbd yanada abinci a gidan sukaci suka koshi a daren ne sukai magana tace ya tafi karatunsa ita kuma zata koma gida gurin innarta da Ummitah sbd idan ma sun zauna anan zaaita tsangwamarsu ne hakama tinda an rena gidan ba kofa a bude yake idan bayanan zaaita musu sata ko wani abin ma dan haka zata koma can garin gashi a hade yake da local government.

Naam yayi da hakan shika tareda samun nutsuwa da zancenta dan haka ya amince sbd yasan kaunar da ummansu zataiwa Ummitah dama wadda batai mataba maman tanai mata dan haka zai tafi yayi karatu da nema dan inganta rayuwarsu su biyun da Ummitah da maman wadda a yanxi itama ta zama tasu nauyinta ya hau kansa kaman yanda na uwar data haifesa zai hau kansa.

Washe gari yafara shirin tafiya makaranta wanda ba wani shiri bane kudadensa dayake tarawane kawai da wanda ya bawa me gidansa na baya ya zuba a shago yaje ya karba ya dan yiwa su Ummitan siyayyar omo da sabulun wanki da mai se panties da vest da brush da macleans daya siya musu sai kuma abimci daya shiya musu me dan dama dama.

Kwana biyu suka gama shirin komai suka nufi garin mahaifiyarsa wanda shine garin mama sakinar.

A gidansu sakina koda suka iso baba ila tini ya kawo zancen tareda duka munanan illoli akan sakina wanda ya saka yam gidansu dayake gidan taro tsanarta tin kafin ta iso ita da 'yartata wanda kowa ya sani ba wanda ya isa ya rabata da ita tinda ansan irin yanda take da fatima dan haka ba wanda ma zaice zai rabata da jinin fatima sedai kuma kwata kwata basuyi maraba da dawowanta ba.

Innarta kuwa da tsufa ya kama sosai kusan batada karfin komai amma ita kam tayi maraba da 'yayan fatima sbd kaunar dake tsakanin fatima da sakina tasan daga Allah ne hakama Allah ne kadai yasan dalilinsa na hanawa sakina haihuwa yabar mata yayan fatima.

Koda suka iso kai tsaye bayan angama gaisawa da jamaa bangaren inna dayake dauke dauke da dan qaramin tsakar gida da daki daya sai bandaki da rumfar girki sai dakin kiwon kaji da yar tinkiyarta suka shige.

Dakin ba tarkace sosai dan haka suka zauna anan suka dawo da zancen komai baya suka tattauna kafin mama tai masa nasihar riqe gaskia da kaucewa haram komai kankantarta idan ya tafi can.

Ummitah tinda suka taho tana jikinsa ta lafe tanajin anfara maganar tafiyarsa tafara hawaye tana qanqamesa.

Jajir idanuwansa sukai shima sbd tinda aka haifeta baitaba rabuwa da ita ba sai yanzu.

Rarrashinta aka fara amma sai hakan yafara tayar mata da hankali tafara rikice musu tana fasa kuka me karfi tana sake riqesa da karfi.

Kasa banbareta daga jikinsa yayi yana kokarin dago fararen idanuwansa da sukai jajir ya zuba mata yana zuciyarsa na nauyi.

Rikicewa tayi gabaki daya tana musu ihu da kukan daya saka duk jamaar gidan fitowa cikin mamaki da tsoro sbd basu saba ganin hakan ba.

Mama sakina ganin yanda Ummitan ta haukace gaba daya ta fice hayyacinta take ya sakata fara kukan itama,

Inna ma kukan ta fara hakama duk yan gidan da suka shigo bangaren sanyi jikinsu yayi sbd kallo daya zakai musu ka tabbatarda wata irin kaune ce tsagwaronta babu sarki.

Rungumeta yayi qam a jikinsa tsawon mintina yana tofa masa addoin samun nutsuwa dana kariya daga sharrin duk wani sharri kafin ya zareta jikinsa da karfi yasakata jikin mama sakina data qanqameta da karfi.

Kudi ya ajiye musu mara wani yawa ya juya ya fice idanuwansa a qasa sbd jan da sukai ya fice gidan.

Se dare ya iso gida ya zauna wasu hawaye masu zafi da radadi sika gangaro masa ya rintse idanuwansa yana adduar Allah ya tsare masa Ummitah daga sharrin komai dayake duniyarnan har lokacinda zai karbeta ta dawo hannunsa.

Tinda dare ya tsala yake zaune akan abin sallah yanawa rayuwar Ummitah da tasa tareda iyayensa wanda mama sakinana ciki addua har asuba.

Wanka ya fara yi kafin yayi alwala yafice masallaci sallah sbd a lolacin aka tada.

A masallaci yana fitowa ya hade da kawunninsa biyu wanda suka kallesa amma sam baima dagoba bare ya kallesu sbd Allah ya haliccesa da wata irin kafiya akan abinda yake qi koya tsana hakama kafiya akan abinda yake tsananin so da kauna dan haka idan ya tsani abu to har abada bayajin zai taba kaunarsa.

Su kansu sunsan yanada kafiya da taurin zuciyar da bazai taba ko kallansu ba.

Yana isa gidan daman ya hada komai nasa dan haka jakarsa daya siya ya saka yan kayansa daya siya ya dauka ya goya a bayansa ya tattara komai nasu ya ajiyegefe ya fito ya rufe dakin ya saka padlock ya rufe ya juya ya fice gidan.

Yana fita ya hau keken wani abokin aikinsa daya hadu dashi a hanya ya kaisa har hanyar mota daga can ya hau mashin zuwa tasha.

Yana isa ba jimawa motarsu ta cika suka daga zuwa abuja inda acan zaibi motar lagos.

Sai dare suka isa abuja dan haka baima bari gidansu Alh Saad suka san yana abuja ba yakwana a tasha karfe dayan dare motarsu ta tashi zuwa lagos.

#MAMUH

#LIMBAS

#AZIZ LIMBA

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

11

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

 ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😊800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

****

A lagos kai tsaye Alh saad yai masa registration daman hardana hostel da komai tini daman aka basa takardun komai suna hannunsa dan haka yana isa wanda Alh saad ya basa numbernsa ya kira suka hade yakaisa har hostel har cikin dakinsa.

Shima students ne wanda aka hadasa dashi dan haka washe gari shiya zo ya jasa suka qarasa sauran registration dinda baa qarasaba da sauran abubuwan.

Kwanaki ya dauka Muhammed yana nuna masa komai na makarantar da yanda zai muamalanci mutane da Guraren lectures da da komai seda ya dan fahimta tukuna Muhammed ya kyalesa duk da kusan kullum suna haduwa.

Karatu da rayuwa a cikik kabila da kuma mutanen da bama ka saba ganin irinsuba abu me tsananin azaba da wuyar gaske tareda gajiyawa musamman dayake akwai kabilanci sosai da banbancin rayuwa sai abin yaso yai masa nauyi,

Amma kasancewansa wanda ya taso gwagwarmaya da tsananin rayuwa tareda rashin sabawa da muaamala da mutane sosai sai hakan bai dade yana wahalar dashiba ya bada himma kawai gurin karatu da dan aikin daya fita da kansa ya nemowa kansa a wani shagon hada lalatattun computers wanda yake samun dama biyu ana biyansa kuma yana koyan computer tareda saninta sosai.

******karatunsa yayi nisa ahankali kaman yanda aikinsa yayi nisa sbd acikin qanqanin lokaci ya zama dan gari ya samu zama babban me kulawa da office din computer din hakama karatunsa sosai yake tafiya yanda yakeso duk da akwai wahala amma ya dage sbd AERONAUTICAL ENGINEERING ne yake karanta wanda karatune dayayi focusing akan development da production of aircraft.

Aiki yake sosai da business tareda karatu wanda ya sakasa sauyawa a kankanin lokaci sbd rufin asiri dayake cikinsa sosai.

Shekara guda ya share cur bai tafi gida ba sbd yanayin aikinsa dayake shine yake kulawa da komai gashi yana karatun sosai harma dana addini dan haka waya kawai yakeyi sosai dasu Ummitah wadda tafara zamowa yan mata.

Koda zai taho ganin gida siyayyar da yayi musu saika dauka shagon sayarda kaya zai bude musu a kauyen dan ko takarman sakawan Ummitah da maman zasu kai kala goma goma koma fiye hakama kayan sakawan ummita da panties ma kadai

dozen uku ya siya mata sai singlet da small small hijabs da kayan shafa da turaruka,

Akwati ma guda biyu ya siyo musu manya na saka kayan,

A taqaice kaman wanda zaiyi aure haka ya hado musu lafiyayyan lefen kaya ya biyo hanya,

Saida ya sauka a local government ya siya abinci shima kaman hauka ya dauki mota guda da kayan ya nufi gidan.

Ummitah na islamiya ya iso dan haka da gudu akaje aka sanar mata

Kallan wadda ta fada mata tayi da kyau da fararen idanuwanta masu shegen kyau da haske wanda suke kama sak da nasa tace

"HAMMAN UMMITAH ne kin tabbata ya dawo?

Idan bashine ba kikasa na tafi fada zamuyi"

Da sauri yarinyar tace

"Eh shine da kaya sosai da mota yazo"

Shiru tayi tana shiga bugawar zuciyar sbd Hamman Ummitah kaman yanda take kiransa yanzu ne to ko sunansa aka fada bugawa zuciyarta takeyi sbd tsananin farin ciki shiyasa ake tsokanarta da cewa yazo.

Allonta dayake hannunta ta ajiye gefenta ta miqe bata tsaya komaiba ta falfala da mugun gudu tabar makarantar.

Tin daga nesa ya hangota a guje tana zuwa daman shima tin dazu ana sauke kayan idanuwansa n hanyar makarantar kaman zuciyarsa zata bude sbd tsananin buqatan ganin hasken idaniyarsa farin cikinsa bugun zuciyarsa kuma.

Dan haka yana hangota idanuwansa sukai wani irin sanyi zuciyarsa na karba itama hakama gangar jikinsa da duminta kawai yake buqata a jikinsa ko zai samu karfin mutuwar da jikinsa yayi na rashin ganinta.

Daidai lokacin mama sakina ta fito daga gida da sauri itama cikin tsananin farin cikinda batasan yaushe ta fara hawayen ganinsa ba.

Hannuwansa ya warewa Ummitah yana tafiya zuwa gareta daidai tana isowa da gudun gaske ta fada kansa yayi sama da ita ya rungume da tsananin karfi yana sauke ajiyar zuciyar dayayi shekara nawa bai saukeba idanuwansa na kadawa zuwa ja.

Itama qanqamesa tayi tana fasa kukan farin ciki tana jin kaman ta bude cikinsa ta shige sbd tsananin kewa da kaunar datake tsakaninsu.

Sun jima a hakan anata kallansu wasu na mamakin irin tsananin so da kaunar dake tsakaninsu wasu kuma na tausaya musu wasu kuma na gulman yanda ya rungumeta.

Kasa sauketa yayi duk da tafara girma ahaka suka juya zuwa cikin gidan bayan angama shigar da kayan mama sakina ma hawayen takeyi ya kama hannunta sukai ciki.

Inna ma duk da idanuwanta basa gani tayi farin ciki da dawowansa sbd kunnuwanta zasu huta da rigimar Ummitah idan taso rashin arzkinta kuka take zaunawa ta ringa musu akan saiya dawo.

Yan gidan ganin tarin kayan arzikin da akazo dasu ya saka suka ringa shigowa yi masa barka da zuwa harda masu kawo lafiyayyar fura dataji madara me tsafta.

Godia yayi musu mama sakina ce ta karba ta ajiye sbd bataga alamar zai iya sha ba sbd ya sauya musu gaba daya ya koma wani ABDULAZIZ din daban.

Ummitah datake jikinsa gyara zamanta tayi a jikinsa yana share mata hawayenta da handkerchief dinsa me qamshi yana kallan idanuwanta da hancinsa dasuke sak nasa kaman shine ya haifeta,

Tayi haske sosai tama kusan kamosa a haske gata fes fes kusan ta banbanta da yan kauyen sosai sbd ya tsaya sosai akansu yana musu aike sam baya wasa da duk abinda ya shafi cinsu da buqatansu.

Mama sakina kuwa sosai take kulawa sa Ummitan harma mantawa takeyi da ba itace ta haifeta ba sbd so da kulawa da tattali dan hakanne ma Ummitah ta banbanta sosai da duk yaran garin ko yayan me gari va abinda suke nuna mata,

A bangaren gata da sakartawa kuwa kusan kaf garin babu kamarta sbd mamah ta sakartata sosai gata take nuna mata sam bata mata fa kuma Allah bai saka tafara lalacewa hakama sam bata barinta wani fita wasa ko yawo koyaushe tana killace daga makarantar boko da aka sakata ABDULAZIZ din na aiko kudin me mashin din dayake zuwa kaita ya daukota wanda shima da maman ake zuwa a kaita a dawo da maman gidan hakama idan zaa daukota sai anzo an dauki maman aje a daukota a dawo dasu tare sbd sam bai yadda a ringa daukanta ita kadaiba sbd tsaro da kiyayewa.

Dan hakan ne daga makarantar bokon sai Islamiya bata zuwa koina,

Kitso da lalle ma idan zaayi mata mamanta ce take kaita ta dawo da ita daga baya ma kudi ABDULAZIZ din yake aikowa idan zaayi sai azo gida ayi mata duk da tana yarinya qarama sai hakan ya saka gaba daya garin Ummitah ta koma kaman wata 'yar sarki.

Fira yakeyi da mama wanda kusan itace da inna masu maganar shi kuma sbd bai cika magana ba sai maganarsa take a taqaice gashi gaba daya hankalinsa yana kan Ummitah sbd wani irin kallan nutsuwa da kiyayewa yakewa koina nata sbd ganin tabon rauni daya a bayan hannunta ya sakasa bin koina nata da kallan nutsuwa a natse batareda kowa ya lura da hakan ba.

Mama ta lura da hakan sedai tasan irin tsananin son dayakewa Ummitah bazai nutsuba ganin rauninta dan haka taji shima ta qara tsananin kaunarsa.

Ummitah ma dogayen yatsin hannuwansa dake farare tas kaman wanda yake cikin tsananun hutu take wasa dasu tana basa labarin duka abubuwan datake da baya nan da yanda mamanta ke sangartata da tsananin sonta.

Inna ce basa shiri sosai sbd yanda Maman ta daurewa Ummitah tana girma amma batada aiki sai kukan banza idan taso dawowan ABDULAZIZ din.

Wani irin sanyi zuciyarsa da jikinsa yayi ya dago idanuwansa da suka dan sauya ya kalli mama wadda tai qasa da kanta cikin taushi da muryansa me nutsuwa yace

"Mama Allah ya saka da mafificin khairi ya saka da gidan Aljannah"

"Amin" inna tace tana jin kaunarsu dukansu kaman jikokinta na jini da sakina ta haifa.

Mamar kuwa ajiyar zuciya ta sauke tana bude baki tace

"ALLAH yai muku albarka ya baku kariya da arzikin da bayajin kashewa yai maka budi ya daukaka rayuwarka ya baka duk abinda kake nema duniyar nan yaji qan iyayenku ya tsareku daga sharrin duk me sharri"

Amin" ya amsa dashi a sanyaye yana dorawa da godia.

Abinci lafiyayye maman tayi masa tabarsa yana fira da Ummitah datake ta faman yamutsashi tana basa labarai kala kala yana saurarenta sbd sautin karatun Al'qurani ne kadai yafi masa dadin muryanta da labaranta dan haka wani sanyayyan murmushi ne da babu me gani a fuskansa yake mata yana kallan

bakinta yana tina ummansu wadda ita mama ta maye mata gurbinta sbd yanda ya lura tsananin so takewa maman nata shi kuwa har abada bayajin gurbin dayake zuciyarsa na kewan ummansa zai cike sbd yanada qawa zucin mahaifiyarsa duk da mama sakina maye gurbi me yawan gaske a rayuwarsu da kusan yake jinta kaman uwar data haifesa.

Kiran magrib da akai ya sakasa fitowa sukai alwala tareda Ummitah tukuna shi ya fice zuwa masallaci ita kuma tayi sallah tareda mamanta.

Yana dawowa aka jere masa abinci a tsaftacen guri tareda sabuwar tabarmar da maman ta siya sbd zuwansa kawai dan haka ya zauna.

Tareda Ummitah yaci abincin kusan ma duk ita ya tsaya kalla tana cin abincin saida ta koshi kafin shima yaci wanda ta rage sbd ragin nata yakeson yaci sbd son dayake mata irin wadda ko qazantarta abar tsananin so ce garesa,

haka kawai wani lokutan idan ya zuba mata ido yana kalla sai yanajin idanuwansa na sauyawa zuciyarsa na sanyi sbd jin kaman ya maidata cikinsa ya adana daga sharrin duniya dana mutane,

Tsananin So ne me tsafta da babu sirki irin wanda uwa da uba kewa 'dan dasuka haifa yake mata sbd jin yake kaman a tsatsansa ta fito tinda shine uba kuma uwarta,

A hannunsa aka haifeta,shine ya reneta,shine wankanta,fitsarinta da kashinta ma,shayarwa ne kadai mahaifiyarta tai mata dan haka bai sauke kansa daga uwa kuma ubanta ba.

Har dare sosai yana gidan saida tayi bacci a jikinsa tukuna yayi musu saida safe yabar gidan yakoma local government da daman yariga ya kama gurin bacci kayansa ma nan dan baima da niyar zuwa garinsu.

Wanka kawai yayi ya sauya kaya ya saka wayarsa caji ya kwanta yana sauke ajiyar zuciya take yayi baccinsa hankali kwance.

#MAMUH

#BESTLOVE

#AY LIMBAS

#UMMITAH LIMBA

#JAN ZADEEN

#DONOR

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

12

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Washe gari bai tafi gurinsu ba sai bayan azahar ya biya ya siya musu kaji lafiyayyu guda biyu da fruits ya taho.

Koda ya iso Ummitah tanata yawon kofar gida da jiransa sbd tana tashi bata gansa ba taso daga musu hankali inna ta tashi tsaye akanta akan karma ta fara musu borin data saba.

Mamanta ce ta ringa lallabata har suka samu ya iso bata rikice musu ba.

Yana zuwa tayi kansa da gudu ta maqale dan ita shi take damuwa dashi ba kayan dayazo dasu ba.

Ciki suka nufa ya miqawa mama kayan hannunsa yana dauke da Ummitan da hannu daya mama na mamakin yanda bayajin nauyinta ko kadan.

Abinci sika ci tare tareda fruits daya saba da cinsu sbd sune suka fara zama abincinsa acan sbd farko farkon zuwansa yayi fama da yunwa da dan rashi kafin ya samu abinyi dan haka su yake siya na kudi kadan yasha ruwa ya kama kansa shikenan shiyasa suka shigesa.

Suna gamawa aka sauya mata kaya tarin kayan daya siyo mata ta saka hijab me kyau da takarmi da turare suka fita.

Suna fita mama sakina ta fidda kayan ta sakawa Ummitah nata a akwati dakyar ya rufe itama nata sakawa tai a akwatinta daya siyo musu ta rufe inna ma takarma da atampa biyi da tirare ya siyo mata dan haka tsofin kayansu da tarin sabulai da omo daya siyo musu ta ringa rabawa yan gidan da moqota tsarabar Hamman Ummitah wanda take aka ringa jin kaunar Ummitah da hamman nata.

Yawo suka tafiyarsu can local government yaje da ita masaukinsa ya siya mata kayan ciye ciye sukaita yawo harda saloon ya kaita akai mata harma da wankin kafa.

Se yamma sosai sika dawo bema zauna ba ya juyo.

Naman kajin ma da mama ta soya tai masa abinci baici ba yace su cinye kawai fresh sabon nono me hade da madaran shanu kawai ya karbo ya tafi dashi ya sha da dare yayi shirin bacci ya kwantawarsa.

****satinsa biyu a garin babu ranar baya fita da Ummitah ya kashe musu kudi sosai ya sake sangartata

Kaf garin babu wanda bai jinjinawa girman kauna da shaquwar dake tsakaninsu dan dole ma aka shafa musu lafiya gashi yanada alkhairi sosai sam baida rowa yan garin sun lasa arzikinsa sosai dan haka kowa yanzu kaunar Ummitah yake sbd farin jinin da ABDULAZIZ din yayi a cikin kwanakin kalilan kowa adduar arziki da budi tareda nasara yake masa.

Da zai tafi saida akai rigima da Ummitah sosai kafin ya tafi cikeda kewanta yabarsu da kewansa suma.

Bayan dawowansa abubuwa sunci gaba da tafiyar masa cikin wani irin nasara da budi dan tini yafara tafiye tafiyen kewayen lagos.

Ahankali rayuwa taci gaba da tafiyar masa hakama karatunsa sosai yake tafiya daidai sai gashi har ghana yafara zuwa harkan business din computers.

Acan ghana ma yayi mutane sosai,

Ta bangaren business dinsu da alhaji saad kuwa komai Allah ya saka musu albarka sosai ake tafiye tafiye kudi na shigowa sosai kuma ganin ABDULAZIZ din yanada wani irin farin jinin aiki ya sakasa fara sakasa a aikin ta can bangaren lagos sai ya zama ABDULAZIZ din baya abuja baya lagos ga karatu da kuma dayan business dinsa dayake habbaka sai ya zama busy sosai bai wani cika zuwa gida ba sai akai akai sedai kullum yana cikin waya dasu dan bai taba bacci ba batareda yayi waya da Ummitah ba wadda itama duk tsananin bacci batayinsa sai lokacin kiransa yayi sunyi waya take bacci.

*****lokacin yaja karatunsa yana gap da kammaluwa hakama zuwa lokacin kudi sun fara zauna masa sbd tako ina kudi shigosa sukeyi business dinsa na tafiya hakama na gurinsu saad na tafiya.

A shekaran daya kammala degree dinsa a lokacin yafara fita qasar waje tareda saad akan harkan business dinsu dayayi wani irin habbaka hakama ga nasa na daban na harkan computers da aircraft dinsa dayake daukaka sosai kaman ma saurayin matashi ba dan kudi kam suna zaunuwa.

Italy suka fara zuwa suka share kusan watanni kafin suka dawo shi ya sauka a ghana shi kuma saad ya wuce abuja.

A ghana saida share tsawon lokaci kafin ya dawo lagos tukuna ya wuce abuja acan yayi service dinsa.

Da yana service ne yake yawan zuwa ganinsu Ummitah daya sauya rayuwarsu a garin suka koma tamkar taurarin dake haske garin.

A garin ABDULAZIZ LIMBA shine tamkar gatansu kuma sarkinsu sbd yansa yake taimakawa kowa yake musu alkhairi dan ya riga ya saba duk abinda zaiyi aike me yawa yake aikowa sbd a rabawa mutane harma da maigari ABDULAZIZ ya zamar masa tamkar wani ginshikin dayake jingina akansa.

Alkhairi yake musu sosai sbd kowa na kaunar Ummitansa duk inda ta wuce kowa sonta yake hakan yasa babu abinda bazai iyawa yan garin ba,

Ya gina musu islamiya da masallaci me kyau hakama gidansu mama ya koma wani tauraro a garin da babu abinda suka rasa a kauyen.

Yana gama service babu bata lokaci ya jona degree na biyu a italy sbd business dinsu dayake tafiya acan sosai dan haka ya tattara yabar kasar ya tafiyarsa.

Yaso dawo dasu Mama abuja sbd karatun Ummitah amma sbd baya zaune a qasar yasa yafi samun nutsuwa dasu zauna acan gida cikin family da tsaro kafin yayi settling tukuna dan ko ya dawo dasu baida nutsuwa tinda bayanan hakama suma

basu saba da nan dinba zasu shiga kadaici da damuwa dan haka tinda shima baida takamaimai inda yake zaune saiya zabi su zauna acan din kafin ya zauna guri daya.

Mashin ya siya aka ajiye na kai Ummitah makaranta me kyau kawai hakama babu abin jin dadin dabai zuba musu ba.

Acan italy yana karatu ne tareda business hankali kwance cikin nutsuwa da ilimi da wayewan data shigesa sedai bai sauyaba daga mara son hulda da mutane sosai da hayaniya yana nan ABDULAZIZ AYOUB LIMBA dinsa HAMMAN UMMITAH.

Bayan halinda da dabiunsa da basu sauya ba babu abinda bai sauyaba daga garesa,

Ya koma wani irin kakkarfan namiji me ji da sabon jini da farin jini da kwarjini me karfin gaske tareda kudi dasuke zauna masa hakama matashin da kyau da nutsuwansa suke sakawa mutane kwarjinsa sosai.

A rayuwarsa bayan bautawa ubangijinsa idan gari ya waye geamin ko jogging yake fita kowace safiya

Daga can kuma yana dawowa yake wanka yayi breakfast ya fice karatu daga can yana dawowa gurin aikinsa yake wucewa,

Wani lokacin kuma aikin yake fara fita kafin ya tafi makaranta daga baya.

4 years ya share a italy ya gama karatunsa tini ya fara aiki me kyau sbd iliminsa dayake fin na abokan karatunsa ko yaushe dan haka yana gamawa ya samu aiki kusan guri hudu masu kyau da girma akaso daukansa aiki amma karshe ya fara aiki a wani babban kamfanin qera jiragen sama kuma a babban matsayin daya sakasa mallakan gidan kansa da motan hawa har biyu.

A farkon fara aikinsa kwata kwata babu wata dama ko kadan ta barin kasar yayi tafiya dan haka duk yanda yaso tafiya gida bai samu damar hakan ba seda maman da kanta ta karfafesa akan babu damuwar komai yayi zamansa tinda suma suna lafiya ba matsala ko damuwar komai.

Ummitah data zama yar budurwa itama karfafasa tayi akan ya vari saiya samu time tinda idan yazo zai daukesu ne yabar qasar dasu gabaki dayansu.

Hakan ya basa qwarin gwiwa da kwanciyan hankali ya nutsu akan aikinsa.

Baai wata shida da fara aikinsa ba sukai tafiyan karatun wani program na wani aircraft dazasu hada a kamfaninsa dayake kokarin budewa shima zuwa Sidney.

Tinda yayi tafiyar su Mama suka dena samunsa shima kwata kwata ya dena samunsu sbd wayarsu da aka sace daga zuwa bikin wata yar gidan da aka aurar aka kai binni sukaje kai amarya.

Sun siya wata wayar amma tsautsayi da kaddara suka hana Ummitah haddace numbernsa sbd kullum cikin yawon kasashe yake numbernsa ba daya bace dan haka bata haddace numbernsa ta Sidney dinba sabanin sauran numbers nasa data haddace dan haka communicating ya yanke a tsakaninsu kwata kwata.

Sun shiga damuwa da tsoro sosai wanda ya saka Ummitah komawa wata sanyi sanyi hakama maman.

Amma dayake sunsan yace yana dawowa zai taho ya tafi dasu sai suka ringa saka idon zuwansa kawai ba waya,

Duk yan gari sunsan wannan karan ABDULAZIZ LIMBA na zuwa tafiya zaiyi da mamansa da Ummitansa dan haka aketa kewansu tin basu tafi ba.

Ummitah karatunta yayi nisa hartana ss1 suna kokarin shiga ss2 amma babu labarin HAMMANTA,

Tin suna saka ran zuwansa har suka cire rai suka ringa adduar idan ba wani abin ne ya samesaba.

Ahankali rayuwa tafara sauya musu gatansu ya fara ragewa sbd duk abinda ya tanadar musu ya qare sun fara shiga damuwa da matsin rayuwa.

Halinda suke ciki ba shine damuwa da quncinsu ba rashin jinsa da ganinsa dan haka suka sake dagewa da addua ba dare ba rana harma da azumi Allah kadai suke roqon ya saka yana lafiya Allah yasa wannan shirun nasarace tafe garesu.

*******Babban tashin hankalin daya riski rayuwarsu shine bayyanar dangin mahaifinsu ABDULAZIZ din garin da babbar maganar data saka mama kusan somewa saida aka riqeta.

Ummitah suke so a basu sbd sun samu labarin ABDULAZIZ yayi kudi zuwa ma zaiyi ya tafi dasu bazaa sake jin labarinsu ba dan haka basu Aminta da hakan ba Aure zasuwa Ummitah anan ta yanda bazai taba barin nan dinba har abada.

Ba mama kadai ba ko inna tana gama jin zancen kuka ta fasa tana rokon ALLAH ya kawo musu ABDULAZIZ kafin a lalata rayuwar Ummitah da suka daukan masa alkawari da rayukansu akan bazasu taba barin rayuwarta ta lalaceba.

Su kawu kuwa acikin kankanin lokaci suka bude wuta akan hakan wanda magana har a gaban me gari dayaqi yadda da maganarsu shima.

Mama kuka ta zube a gabansu tana rokonsu akan kada suyi hakan su bari ABDULAZIZ ya dawo qasar.

Kallanta kawu shehu yayi yanajin wani baqin ciki na taso masa sbd jin wato ma ABDULAZIZ din baya qasar sbd samun daukaka gasunan yaransu sun danqare a kauye basa komai sai aure aure suna tara yara da qananun shekaru.

Tsokin baqin ciki kawu shehun ya sake yana kallan kawu isyaku da shima baqin cikin yake yace

"Wlh bazamu jirasa ba tinda ba shine ubanmu ba,aure kuma wlh babu wanda ya isa ya hanamu yimata aure tinda duka sa'anninta gasunan anmusu aure harda haihuwa wasu ma

Duk kunbi kun mayarda yarinya sakarta shiyasa zaizo ya dauketa yakai qasar turawa ta qarasa lalacewa ko?

To idan shi yafi karfinmu baimasan damu ba to ita kafin tafi karfin namu zamu nuna matsayinmu kanta"

Cikin kuka mama ta dago jajayen idanuwanta zatai magana kawu shehun ya katseta a kufule da cewa

"Ke wlh babu abinda zamuji

Ke wlh ma vazata qara sati a gida ba nan da kwana uku idan bata fidda miji ba aure zamu daura mata da 'dan uwanta 'dan wajen isyaku jibi a daura musu aure mu tafi da ita ta tare ai shikenan idan ya dawo ya ringa kai mata ziyara acan da duk ma abinda ze kai mata ya ringa kai mata acan"

Hawaye masu tsananin zafi ne suka gangarowa mama sbd a bayyane tsananin kwadayi da baqin ciki da hassada ce zata sakasu yin abinda sukeson yi.

Qara mama ta sakasu amma karshe sune aka bawa gaskia sbd sune dangin uba dan haka hankalin mama dana maigari ya tashi sbd bazasu taba bari a iya lalata rayuwar Ummitah ba sbd itace rayuwar ABDULAZIZ kuma kuzarinsa na nan duniya.

#MAMUH

#LIMBAS

#BROTHERS LOVE

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

13

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Kwana biyu daga mama har Ummitah da inna babu me walwala cikin tsananin damuwa suke wanda ya saka inna fara ciwo ahankali dama ga tsufa sosai ya cimmata komai yi mata akeyi ko mama ko Ummitah.

Maigari baba Alhassan ma duk yanda zai samu mafita ya nema babu dan haka ya kira Mama sukai shawara akan kudin dayake ganin shi kadaine mafita garesu dan hanawa su kawu shehu Ummitah.

Shiru mama tayi sbd nauyi da girman zancen amma kuma basuda zabin daya wuce hakan sbd shi kansa ABDULAZIZ zaifi jin sassaucin hakan akan su bari a tafi da Ummitah dan haka ta sauke numfashi ta dago ta kallesa shima shiru yayi sbd SAYYID shine 'dansa tal namiji wanda yake so fiyeda duka yayansa dasuke mata kuma dika dika su hudu ne uku mata sai sayyid din wanda yake qaraminsu hakama duka duka baifi shekara goma sha takwas ba zuwa da sha tara so yake shima yayi karatu ya zama kamar ABDULAZIZ da suke kallo kaman wani taurari dayakeda haske mara dishewa,Amma ayau ya yadda ya dirqushe masa rayuwa ta hanyar daura masa aure da Ummitah dan hanawa dangin ubanta tafiya da ita.

Mama ma ganin kaunar Baba alhassan din dayakewa ABDULAZIZ ya sakata amincewa take gashi Sayyid din ma yanada son koyan karatu shiyasa kullum yake yawo makarantar yan boko yana kallansu yanda suke karatu.

Koda mama ta isa gida da maganar inna jikinta ya rikice wanda ciwon ajali kawai yazo mata ba bata lokaci ta zama wani iri haka suka kwana akanta anata abu daya asubar fari tace ga duniyar nan.

Sabon damuwa da tashin hankalin rashin inna suka shiga itada Ummitah dan haka suka ringa kukansu su kadai.

Rasuwar inna ta saka su kawu daga auren dan haka a kwana biyu Ummitah ta fita hayyacinta 'dan uwanta kawai take tsananin so da buqatan gani.

Mama kuwa rashin inna dana ABDULAZIZ dinne ya ringa zuciyarta itama amma basu janye uzurinsu na aurenba dan haka inna na kwana bakwai da rasuwa aka saka Ummitah a lalle ba sanarwa sedai kawai aka ringa tayasu murnan dole.

Kafin labari yakaiwa su kawu su taho tini baba alhassan yaje gurinsu ya nema aure da dan arzikin daya rage masa duka ya basu sbd zalama suka amince atake ma suka daura auren kafin yan neman auren su tafi.

Mama kuwa duk abinda ya rage musu ta tattara ta siyar tai bikin Ummitan ta siya mata kayan daki da abubuwan buqata aka kaita.

Acan gidan baba alhassan ma gyara musu daki daya yayi lafiyayye da bandaki aka gyarawa amarya ta tare.

Ummitah tayi kuka kaman zata zarewa mamanta hakama maman tayi kuka hadda ciwo amma haka suka rabu.

*****komai ya lafa ankwana biyu kuma Ummitah bata dena zuwa makaranta ba wadda karshe ma itada sayyadin din mijinta sika koma suna zuwa tare daga karshe ma aji daya aka yan dubaru aka sakasu sbd ta dan ringa koya masa abinda bai ganeba tinda ta dade a karatun ita.

Bayan auren shakuwa da kusanci sosai ya shiga tsakanin Ummitah da sayyid suka fara son junansu sosai,

Soyayya me karfin gaske sayyid yake mata kaman yanda itama take masa dan haka hankalin mama dana baba alhassan ya kwanta sukasake duqufa adduar dawowan ABDULAZIZ.

Suna shiga ss3 Ummitah ta samu ciki wanda bayyanar rashin lafiya a tattare da ita ne ya saka aka san da cikin dan haka kulawan da ake bata ya qaru sosai.

Sayyid kuwa dadi ya ringa ji dan baima damu da rashin tsayuwarsa a rayuwa ba sbd tsananin son dayakewa Ummitah da duk abinda ya shafeta.

Bai taba ganin ABDULAZIZ ba amma kaunarsa yake mai tsafta da karfin gaske sbd irin tsananin son da Ummitah ke masa dan haka shima yake shirye daya bisa yayi masa biyayya har inda karfinsa ya qare.

Ahankali ahankali ciwon laulayi ya koma ciwo a jikin Ummitah,

Ga karatu wanda dole ta dena zuwa ga sanyi daya shigeta sosai kwata kwata cikin baizo da saukiba ko kadan dan haka mama taxo ta dawo da ita hannunta tana kulawa da ita.

*******Rashin jinsu kwata kwata tsawon lokaci me tsayin gaske ya saka ya shiga damuwar data taba aikinsa wanda ya saka masa dawowa da abinda yake yi baya dan kuwa lalacewa komai yayi sbd damuwa dan haka dole komai aka dawo farko kuma ba damar tafiya sbd aikine da zai sauya rayuwarsa gaba daya idan yayi nasara dan haka dole ya dage ya tsaya wanda hakan ne ya haddasa masa daukan tswon lokaci meyawa na shekaru bai dawo ba.

A cikin nasara da yardar Allah ya kammala tareda samun zuwa na daya wanda ya janyo masa wata irin suna da daukaka.

Murna da farin cikin mutanensa dasu alh saad suka shiga anata celebrating tareda tayasa murna hakama kamfaninsa take ya samu shiga jerin kamfanin da aka dan san dasu.

A lokacin ne babu bata lokaci ya tattara ya koma Italy daga can ko sati biyu baiyiba ya sauka Nigeria.

Bai kwana a abuja ba ya isa garinsu sbd daukosu kawai yakeda niyar yi su dawo abuja.

Lafiyayyan gida me kyau da tsari dan girma ya mallaka a abujan wanda babu abunda baa sakaba na jin dadin rayuwa wanda tin bai dawoba qasar aka gama komai na gidan da tsarinsa.

Da rana kwatsam ya sauka a garin wanda motarsa ta saka jamaa taruwa a kofar gidansu mama.

Ummitah dake zaune mama da sayyid na gefen suna kokarin ganin taci abinci da lemu da abarban data saka sayyid siyo mata sbd shima gaba daya ya haukace da nema sbd kulawa da ita da Buqatunta gashi kusan ya tare gidan maman shima sbd ita.

Mama na dagowa ta kallesa saida gabanta yayi mummunan faduwa sbd gabaki daya baiyi kama da ABDULAZIZ dintaba

Hawayene suka fara gangarowa daga idanuwanta masu tsananin zafi da batasan ma na menene ba.

Ummitah kuwa qamshinsa daya cike tsakar gidan ta shaqa da kyau har cikin cikinta taji wani irin sanyi na mamaye zuciyarta zuwa gangar jikin.

Itama hawaye ne suka fara gangarowa daga idanuwanta tana kasa dauke idanuwanta daga kansa duk da kuwa tsananin kwarjinin dayake dashi na cikar haiba.

Sayyid hannuwansa biyu ya saka suna rawa yafara goge mata hawaye yana jiyowa yayiwa ABDULAZIZ din kallo daya ya sauke idanuwansa.

Kwata kwata bai lura da cikin dayake jikinta ba sbd abine da bazai taba kawowa akansa ba koda kuwa mafarki fararen idanuwansa masu wani irin kyau ya zuba mata zuciyarsa na samun abincin datai shekaru bata samuba ya ware mata hannuwansa ahankali tareda ambatar sunanta da wani irin sautin daya sakata fasa kuka tana miqewa da karfin da sayyid baitaba sanin ayanzu tanada shi ba sbd rashin lafiya ta tinkaresa da gudun gaske ta fada jikinsa yai wata kyakkywar runguma yana rintes idanuwansa wani irin farin cikim dayafi komai na rayuwarsa na rufesa.

Mintina sukai ahakan yana sauke ajiyan zuciya ita kuma tana kuka sosai tana kankamesa tana ambatar sunansa kaman zata bude masa zuciyarta yaga irin abinda takeji na kewansa datai da tsananin Buqatansa datake.

Mama ma kuka takeyi sosai wanda ya sakasa sassauta riqon da yayiwa Ummitah jin wani wani irin tudu ya dan tokaresa.

Bude idanuwansa yayi ahankali tareda zubawa mama yana kasa sakin Ummita wadda itama ta sake qanqamesa.

Wani irin ciwon kai yaji ya sara masa a tsakiyar gefen kansa ya lumshe idanuwansa da suka dan sauya ya bude yana zare Ummitah a jikinsa ahankali.

A gabansa ya tsayar da ita ya zubawa fuskanta datake sunkuye tana kuka ido yana mata kallan daya saba mata duk yazo na karantar meye ya sauya a tattare da ita.

Tin daga fuskanta yaji zuciyarsa na nauyi yafara gangaro da idanuwansa har zuwa cikinta daya fito qarami dashi.

Kaman cikin haihuwa yake gani a jikinta wanda yasan imaginations nasa kawai dan haka ya dago ya zubawa fuskanta ido yana son ta kallesa amma ta kasa dagowa sai kuka tasake sakarwa.

Mama data kasa dagowa ya mayarwa da kallansa sai lokacin ya lura da sayyid daya taho ya tsaya gefensu yana kallansu cikeda kauna da burgewa tareda rashin son kukan Ummitah.

Mama ce tayi karfin halin dagowa tanai masa sannu da zuwa share hawayenta ta nufi daki dauko masa tabarmarsa da haryanxu bata taba fiddawa wani ya hauba sbd dan shi suka siyeta.

Tana saka kafarta daya daki kafin ta saka dayar ya kasa shiru da muryansa me nutsuwa da taushi yace

"Mama meye wannan a jikin Ummitah??

Cak ta tsaya agurin batareda tayi gababa ko baya tana sauke numfashi da ajiyar xuciya me sanyi kafinta juyowa ahankali kai tsaye tana daukan matsayinta na uwa ba shakka tace

"Juna biyu ne a jikinta ga mijinta nan a tsaye ku gaisa bara na dauko maka gurin zama"

Tana fadar hakan ta qarasa wucewa ciki tana sauke ajiyar zuciya da numfashi sbd ba amfanin boye boye da tashin hankalin abinda ya riga ya faru ba sauyi kaddararsu taxo ahakan.

Shiru gurin yayi wani irin mummunan nauyi kansa yayi da maganar tareda wani irin nauyin kirji daya kusa taba ganinsa dan haka tabarman data shimfida ya qarasa baya gani sosai ya zauna yana kasa kallan maman sai Ummitah da rayuwarta ta riga ta lalace dan haka take idanuwansa sauya zuwa wani irin jajir kaman an zuba musu borkono.

Maganan bayan rabuwa da barka da zuwa mama ke masa amma kwata kwata baya jinta jinsa gava daya ya dauke iska kawai yake ji kaman yana kada masa hakama ganinsa yara rawa dan haka bai fahimci komai sosai ba saida Ummitah ta gama kukanta ta dago ta kallesa ta fahimci kwata kwata baya hayyacinsa ma kuma maganar aure da cikin ne yake neman zarar dashi kuma tasani babu abinda zai hanasa raba auren dan haka cikin sanyin murya ta bude baki tace

"HAMMA inasonsa zanci gaba da zama dashi"

Rintse idanuwansa da suka kusa watse masa yakeji yayi da qarfi wani nauyin gaske na danne kirjinsa.

Sayyid daya shiga damuwa da tsoro numfashi ya sauke me sanyi yana kallan Ummitah da shi gava daya ganin ABDULAZIZ din ya tsinkar dashi.

Mama ma numfashi me sanyi ta sauke sbd a baya kam daya dawo da wuri yace zai raba auren bazata hanaba amma yanxu ga rabo ansamu kuma ace zaa raba auren bame yiyuwa bane.

Mama ce ta karbi zancen kai tsaye da cewa

"Sayyid yaron kirki ne kuma yana kaunar matarsa da abinda yake cikinta dan haka ba abin damuwa bane ga abinda Allah ya kaddaro,

A matsayina na uwa gareku ina umartanka da kada kace komai ka karbi hukuncin Allah da hannu biyu"

Bude idanuwansa yayi suna sake sauyawa kirjinsa na wani irin radadi me ciwon gaske sbd mata uku dayake so fiyeda komai a rayuwarsa da komai daya mallaka ga biyu a gabansa daya tace tana sonsa daya tace bata aminta yace komaiba.

Numfashi ta sauke me sanyin daya sakasa kallanta ta dago da sanyi muryanta na fitowa a tausashe tace

"Hammah ka dawo da wuri sbd inason na haihu kana nan,

Inason kafara daukan abinda zan haifa kaman yanda kaine kafara daukana dana taho duniya..

Shiru yayi yana tino rayuwar azaba da gararin dasukai shida mahaifiyarsa a lokacin renon cikin Ummitah....

Wani irin nauyi da daci kirjinsa ya cikeda dashi jikinsa na mutuwa yana kasa kallan Ummitan data zuba masa ido tana karanto dacin dayake cike zuciyarsa idanuwanta suka ciko da hawayen da suka gangaro gefen idonta.

Ranar haihuwarta ya tina irin ukuba da qangin da mahaifiyarsa ta shiga tareda juyewan hankalinta tareda gararin datai cikin rashin hankali har bacewanta...

Hawayenda tin lokacin batar mahaifiyarsa bai sake sanin ya ake zubdasu ba sbd taurin zuciyar dayake dashi ne suka ciko Kyawawan idanuwansa ya rintse idanuwan yana hadiyesu dan radadin Rashin mahaifiyarsa shine radadi mafi munin dayake yanka zuciyarsa.

Ahankali Ummitah ta kwantar da kanta kafadarsa tana kasa cewa komai sai hawayen da suke gangaro mata tana son ta tambayesa kamannin Mahaifiyarsu da mahaifinsu da bata taba saniba sedai tanajin radadin dayake ji na tinano ranakun quncinsu na baya da suka wuce dan haka bata iya cewa komaiba shiru kawai sukai babu wanda yace komai har kusan dare sosai ta tashi yakaita har dakinta ya kamo hannunta ya saka mata wani tsohon hoton daya tsufa sbd har ruwan sama yasha sosai sbd wahala ya juya ahankali ya wuce bedroom dinsa.

Zaunawa tayi a sanyaye bakin gadon dakinta tareda dago hannunta da yayi mata sanyi ta bude hoton ta zuba masa idanuwanta da suka sauya sbd kukan datai sosai.

Hoton Mahaifinsu ne tareda Hamman yana qarami sanye da uniform din makaranta a ranar daya fara kaisa makaranta a ranar sukai hoton a makarantar me hoto yayi musu shi

Murmushi baban yakeyi fuskansa a sake sosai yan riqe da hannun ABDULAZIZ din shima Murmushin yakeyi na farin cikin zuwansa makaranta.

Wani irin abu takejin yana tasowa a kirjinta me nauyin gaske tsananin son Mahaifinsu na mamaye zuciyarta

kuka mara sauti ya taso mata ta silale a gurin tanayi tana jin tausayin Hammanta wanda ya rasa uwa da uba dan ita kam shine uwa da ubanta.

Sayyid ne ya shigo dakin gabaki daya gidan a sanyaye kowa yake ba walwala sbd Ummitah gaba daya ta sauy kwana biyun bata cikin walwala musamman da tafiyar Hamman gobe ce sai gaba daya yau ta rikice bata jin dadin komai hakama suma duk sun shiga damuwa.

Ko kadan a daren Ummitah bata rintsa ba hakama ABDULAZIZ din kwana yayi yana mata adduar Allah ya saukar da ita lafiya.

Da asuba koda ya dawo sallah wanka kawai yayi ya shirya ya fito dan 7 jirginsa zai tashi,

Sanye da Black UGG knit top da Straight jeans ya fito sai fcap ta balenciaga yana qamshi me sanyi ya fito Sayyid tini yakai kayansa mota ya dawo.

Fuskansa tayi wani irin fresh yayi fayau sbd rashin rintsawar da baiyiba da damuwar datake cin ransa dayake ganin tafiyar da zaiyi ne yabar Ummitah a wannan halin.

Cikin dauriya da danne damuwar ta harma da ciwon datakeji ta fito itama fuskanta tayi fayau ta qarasa har gabansa ta miqa masa hannu tana sakin murmushi me kyau dan kwantar masa da hankali.

Ajiyar zuciya a fili ya sake ahankali yana mata kallan tsafta ya miqa hannu ya kama hannunta data basa sukai musabaha ta sauke ajiyar zuciya tana sake qanqame hannunsa cikin nata tace

"ALLAH ya baka nasara akan abinda zakaje ya baka nasara a duk abinda zaka nema a duniya ya kuma dafa maka ya hanaka damuwa kowace iri ce...

Shiru ta dan yi kafin tace

"Allah kuma ya dawo da kai lafiya Hammah"

"Amin ya furta ahankali yana kallan cikin idanuwanta da ita shi take kalla tana murmushi me kyau da nutsuwa.

Mama ya kalla da sayyid yace

"Idan akwai abinda ya taso a kula sosai a tafi asibiti akirani,a kula"

Addua mama tai masa itama tana masa fatan dawowa lfy.

Hoton daya bata jiyan Ummitah ta fidda a cikin dayan hannunta ta saka masa shima a hannunsa tana cewa

"Nagode Hammah"

Murmushin karfin hali shima yayi mata yana shafa fuskanta ya matso kaman yanda ya saba ya karanta mata adduar dayake mata tin tana yarinya ta neman tsarin ubangijin a kunnenta ya share mata hawayen da suka gangaro mata tana murmushi ya juya ya shige mota yana daga musu hannu.

Sayyid ne ya shiga motar sbd tareda shi zasu Airport din da drivern gidan Alh Saad.

Motarsu na barin gidan gidan ta sauke ajiyan zuciya me karfi tana jin wani abu kamar yabar jikinta dan haka mama ta jata suka koma cikin gida.

Koda Sayyid ya dawo daga Airport bai dameta ba kyaleta kowa yayi sbd ta samu ta warware da kanta sedai hakan bai yiyiba dan kuwa zazzabi me qarfine ya kamata wanda ya sakasu damuwa.

Haka suka wuni da ita har dare batajin dadi sedai tace ba buqatan zuwa asibitin dan haka sai baa takurataba.

Washe gari ma haka ta wuni cikin yanayi na rashin lafiyar datake cinta a hankali,

Fama su mama suka fara da ita sbd gabaki daya lafiyar tana neman gagaranta sbd wani irin silent ciwo take fama dashi wanda ta rasa menene yake damunta itama hakama da kanta ta hana a sanar da Hamman sbd kada ya shiga damuwa tace zata iya daurewa har lokacin haihuwanta ya qara yi tinda ta kusa.

******ciwon kwana daya kwana biyu zai qara gaba yakeyi cikin tsananin azabar da bata taba saniba take a yanzu hakama batasan me zatace yana damunta ba ga damuwar datake damun zuciyarta da kwata kwata bata mata dadi,

Wata irin rama me muni ta fara da wani irin haske dayake bawa mama da sayyid tsoro sosai hankalinsu ya tashi sosai kuma har lokacin sun kasa fadawa ABDULAZIZ din.

Zuwansu asibiti biyu dr yana dubat yana ce musu lafiyarta kalau kawai yanayi ne na haihuwan daya matso.

Dawowa sukai gida suna cigaba da kulawa da ita sedai tashin hankalinsu da tsoronsu tsananta yakeyi sbd qarewa takeyi kamar wadda mayu suka kama takai komai tafara gaza yiwa kanta jinya takeyi sosai wanda ya fara taba lafiyar cikinta.

Dole suka tattara suka sake komawa asibiti gashi anty maryam bata nan su kadai suketa Fama sai drivern da aka samar musu sbd fitarsu.

********Dzad ne a zaune a lafiyayyar office dinsa dayake cikim mansion dinsu ya zare farin glass dinsa yana kallan Ammar wanda Maheer ma shi yake kalla.

Numfashi Ammar din ya sauke cikin samun nutsuwar biyan buqatan shekara da shekaru yace

"Komai na matar da aka samu zuciyarta ya kammala magani ya gama aiki akanta wanda kowane time a wannan stage din datake shine daidai lokacin da zataiwa Jannah donor,

Anyi bincike akanta ba kowa bace daga kauye suka taho suna zama gidan wani relative dinsu ne wanda baima cika zamaba so bandai tsaya nasan sunansa ba kokuma buqatan hotonsa sbd ba buqatan hakan,

Abu daya ne shine lokaci yayi zuwa jibi zaayi aikin wanda muke fatan wannan shine na karshe sbd baa taba samun matching din da ake tinanin yayi 99% ba kuma gashi cikin ya riga yazo lokacin haihuwa so the right and perfect time has come"

Maheer jin yayi wani nauyi da sanyi na cike zuciyarsa lokaci daya

Dad ma jin yayi bayajin komai baya buqatan komai kawai ayi aikin su samu abinda suke so shine burinsu.

Nutsuwa da nauyin daya danne musu zuciya shekara da shekaru ne sukaji dukkaninsu yana fada musu.

Washe gari ranar da zaayi aikin Anny ce ta bawa Jannah maganin data yanke jiki aka kwasheta zuwa asibitin sbd suna buqatan ta kasance a asibitin koda zaa shigo da Fatima Abdulaziz Ayoub din

Wannan shine sunan dayake jikin katinta.

Ummitah kuwa a daren ranar gabaki daya jikinta ya rikice jini ne yake mata zuba ba kakkautawan daya saka a cikin daren mama da sayyid suka kwasheta zuwa asibiti hankali tashe.

Dr ken yana asibitin daman yana jiran zuwansu sbd yasan hakan zata faru,

Dayake ansan shine dr dinta kiransa akai da gaggawa

A rikice cikeda kulawa da tashin hankali yayi kanta yana kiran nurses.

Naquda ce ya tayar mata tareda mata allurar da zata hanata iya haihuwa da kanta dan haka hankalin nurses ya tashi gashi bleeding takeyi sosai gashi tayi wani irin ciwon data jima acikinsa ya bayyana sosai a jikinta.

A cikin daren ganin an kasa shawo kan matsalar take yayi mata transfer zuwa ZADEEN HEALTH CEN.

Su mama da sayyid tinda suka gwada kiran Hamman baa samesa ba sai suka maida hankali kan Jikin Ummitan da aka tabbatar musu ba sauki gashi private hospital ce babu mutane sosai sbd tsadarta da tsarinta.

Dr ken kallansu yayi cikin nuna damuwa da kokarinsa yace

"Haihuwace tazo mata gadan gadan gashi lokacin bai qarasa yiba sbd bata bude ba gashi kuma babyn ruwan dayake rayuwa a cikinsa cikin cikinnata ya tsiyaye dole Aiki zaa mata a cire babyn idan ba hakanba komai zai iya faruwa da ita har babyn dan haka aikin Gaggawa zaa shiga da ita a acikin daren nan anan likitocinmu duka basa nan Nayi muku transfer zuwa qwararriyar asibitin da muke da ita Kusa yanzu can zaa tafi da ita.

Babu abinda mama da sayyid ke nanatawa bayan sunan Allah cikin matsanancin tashin hankali dan haka basuda zabin daya wuce aminta da hakan.

Cikin ambulance da gaggawa akai Asibitin da ita koda suka isa tafara nisa dan haka Hannu kawai sayyid ya saka a takardun komai aka shige tiyata da ita suna kallonta kowannensu idanuwansa na cikowa da hawayen dake zana radadi a zukatansu har aka shige da ita aka rufo kofar wadda ta saka kirjin mama bugawa da wani irin ciwon daya sakata dafa bango tana silalewa qasa ta zauna har lokacin kirjinta na qara ciwo.

Sayyid kuwa sunkuyar da kansa yayi yanajin kaman kunnuwansa da kansa iska na musu yawa.

#MAMUH

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

23

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Wayar hannun sayyid da yayiwa wani irin riqon dayake gap da saka screen din lalacewa batareda ya saniba sbd damketa yayi zuciyarsa najin kamar zata baro kirjinsa sbd abinda yakeji,

Ummitah bayan mahaifinsa a duniya itace abinda yakeso fiyeda komai da kansa sbd baida mahaifiya shima ta rasu,

Ummitah itace wadda baya kaunar gani ko yanayinta kadai ya sauya dako ciwon kai bare damuwa ko wani babban abin,

Ayau gata a gabansu anshiga aiki da ita yankata zaayi a ciro abinda yake cikin amma basuda abin yi sbd Allah yin Allah ne da ikonsa.

Hawaye ne sika cika idanuwansa da sukai jajir amma sun kasa saukowa,

Wayarsa ya kurawa ido yana sake saka kiran Hamman a karo na babu adadi ayau din amma har lokacin bata shiga.

Cigaba yayi da kiransa idanuwansa ko gani basayi sosai hakama hankalinsa da zuciyarsa duk basa aiki daidai kawai hamman yakeson ji dan haka ya kasa dena kira kaman mara hankali hannuwansa har rawa sukeyi.

Mama kuwa kanta yana qasa soke cikin qafafunta tana jin kirjinta na tsananta nauyi dan haka ta daure cikin karfin hali tana tsananta adduarta akan ayi aikin lafiya su samu daga uwar har yar lfy.

Shiru tsit gurin ya dauka kwata kwata babu motsi ko hayaniyar mutane a bangaren da ake aikin wanda guri ne na musamman a asibitin ba kowa yake zuwa ba sbd bangaren masu asibitin ne da babu wanda aka taba kawowa gurin sai wanda zaa illata.

Yanda hannun sayyid ke rawa cikin tashin hankali da fita hayyaci ya kasa dena kiran Hamma kaman zararre ya saka wayar faduwa daga hannunsa ta fadi tana fashewa gurin yana kallo screen yafara wani kyaftawa yana rawa a fashe haryayi duhu gaba daya ya mutu.

Rintse idanuwansa yayi yana silalewa a gurin ya zauna a qasa shima duk da akwai kujera a gurin baya buqata.

Adduar mama ce datake yi cikin dagewa da rashin sanya sautinta yake fita ahankali batareda ta san da hakan ba,

Rintse idanuwansa yayi dake masa radadi yana adduar shima a zuciyarsa.

Babu wanda suka gani babu wanda ya fito ko yazo wucewa ya gansu zaman azabar jira kawai sike tsawon awanni ba labari.

Kiran asuba ake farawa tinda daman a tsakar daren suka iso asibitin,

Kiran farko da aka kwada yayi daidai da bude kofar dakin tiyatar wanda ya saka mama da sayyid din miqewa a tare suna zubawa kofar jajayen idanuwansu zuciyoyinsu na wani irin sanyin da basu iya taku ko daya ba.

Dr Abraham sanye da kayan tiyata da hula ne a gaba sai dr finn a bayansa da wata Nurse wadda ba kowa bace Anny ce wadda take sanyeda face mask fari da kayanta na Nurses.

Ammar ne ya fito karshe shima sanyeda facemask din na likitoci da wularsu ta tiyata akansa baiko kalli inda su maman da Sayyid sukeba ya wuce yana jin jiri da nauyi a kirjinsa na fata da tsoron dacewa a aikin da zasu shiga yanzu na jannah.

Anny ma bata tsaya kallan nasu ba tabi bayan Ammar suka bar gurin zuwa wata kofar dake gurin.

Wata Nurse ce ta sake fitowa dauketa baby nade a cikin farin showel me tsananin taushi da tsadar dasuka taho dashi aka karba tin acan asibitin dr ken.

Tinkarosu Nurse din tayi da babyn wadda take lafe idanuwanta a rufe.

Dr Abraham da dr fin sai wani likitan daya fito baqi ne bahaushe musulmi ma yana zare hular kansa ya wuto gaba yana kallansu suma akansa suka maida kallansu suna kallansu da imaninsu sbd ganin shine nasu tinda su dr Abraham turawa ne bama gane musu zasuyiba.

Nurse ya kalla tana miqawa Sayyid din baby ya miqa hannuwansa cikin wani irin farin ciki dayake saka jikinsa rawa yana kokarin karba Muryan dr ismail wadda take tafe da bayayyanarda radadi da alhinin kai tsaye ta sauka a kunnuwansa....

"Anyi nasarar cire mata abinda yake cikinta cikin koshin lafiya sedai ALLAH YA KARBI RAN UWAR bawa baya wuce lokacinsa ayi haku.....

Sakin jaririyar hannunsa Sayyid yayi cikin mummunan shock din dabai masan yayi hakanba.

Nurse dince tayi saurin zubewa qasa ta tare babyn a hannuwanta cikin ihu.

Wani mugun busashiyar yawu mama take kokarin hadiyewa amma ya kasa wucewa yankar mata maqoshi tanaji yanayi kaman da wuqa dan haka ta kyafta idanuwanta da suka qanqance tana kallansu daya dayan daya kafin ta tsayar da idanuwanta akan dr ismail din da qyar ta tina bakinta zata bude ba hannuwanta datake budewa ba muryanta na yankewa tace

"Kace an sauka lafiya ko?

Ita Ummitan fa?

Numfashi me zafin gaske ya sauke yana kallan Sayyid da yayi mutuwar tsaye yana wani vibrating amma tambayar maman ta sakasa dago jajayen idanuwansa da suke neman fashewa ya kallesa yana son jin amsar tamyar maman dan shima abinda yakeson tambaya amma ya manta yaya ake bude baki ayi magana gaba daya..

Sunkuyar da kai dr ismail din yayi yana kasa kallan idanuwansu da suka zuba masa ya bude baki yana tausasa harshensa yace

"Babu yanda zamu iya dukkaninmu akan hukuncin ubangiji,

Hakuri zamuyi dukkaninmu,

AN RIGA AN RASATA,TA RASU ABINDA TA HAIFA KAWAI AKA SAMU....."

Mama bakinsa take kalla kalaman na fitowa daga bakinsa kafin ta juya ta zubawa kofar dakin idanuwanta kafin ta sake wani yunqurin wani bugu kirjinta yayi so daya ta yanke jiki a gurin ta zube idanuwanta na juyewa gabaki daya.

Sayyid kuwa baya yayi kafafunsa na kasa daukansa ya durqushe a gurin yana fasa wani irin irin ihun daya saka gabaki daya rabin asibin daukan qarar kafin ya fasa wani irin kukan daya saka su dr Abraham yin baya cikin firgita sbd kukane daya zo masa kansa na zarewa gabaki daya yana wata irin jijjigar data saka dr Ismail kasa riqe abinda yakeji ya rungumesa yana jin idanuwansa shima cikowa da hawaye sbd radadin abinda sukai dayake ji a zuciyarsa wanda yayi a bisa rashin zabin dayake dashi.

Riqe sayyid din yayi a cikin jikinsa sbd irin jijjigar dayake zata iya sakasa samun collapse wanda zai iya qin tashi idan hakan ta samesa.

Jijjiga me karfin gaske yakeyi yana wani irin kuka me gunjin daya saka nurses dake kusa tahowa sun kallansa cikeda wani irin tausayi me cikeda tsoro sbd ganin namiji kamarsa yana irin wannan kukan me tada hankali.

Mama kuwa dr Ken ne yace nurses suyi saurin daukanta akaita emergency sbd ita kam kamar raima ya fita a jikinta.

Sayyid ma rikicewa yanayinsa yayi dole cikin tsananin gaggawa dr ismail yasa akai emergency dashi sbd wani irin kumfane ma yake fita bakinsa kaman yana kokarin samun wata matsalar ne suna buqatan gaggawar dawo dashi daidai.

Nurse Latifat aka bari da babynsu a hannunta tana yawo da ita sbd tashin hankali da firgicin ganin su dukan suna neman mutuwa a asibitin tasu.

Dr Abraham da dr finn kuwa Bayansu Dr Ammar suka bi sbd shiga tiyatar Jannah wadda Allah yayi sun samu abinda suke zo ba matsala fatarsu daya yanzu ana sakawa tayi saurin matching da vessels na jikinta batareda tasha wahalar kafin gama sabawa ko binding na komai daga zuciyar zuwa jikinta da jininta.

Duk yanda Su dr ismail da wasu likitocin suka shawo kan Sayyid kasawa sukai gashi sai muni jikinsa yakeyi dole sikai rendering nasa unconscious.

Mama kuwa kaman qaramar coma ta shiga sbd komai nata dena aiki yayi.

Tsit bangaren yayi babu mafitar komai har rana tai daga mama har sayyid babu wanda aka samu kansa bare asan yanda zaayi dasu ga baby ma tafara kuka sosai ga gawar Ummitah a ciki an rasa ya zaayi dasu.

A wannan halin ne Baba alhassan ya iso abuja sbd tin a jiyan Sayyid ya sanar dashi jikin Ummitan aiki zaa mata dan haka jinsu shiru ya iso.

Asibitin dr ken ya isa kai tsaye sbd acan ya taba zuwa dubo Ummitah wani zuwan da yayi kwanaki.

Acan ana kiran dr ken da kansa yaje ya dauko Baban ya kawo Asibitin nan sbd daman neman yan uwansu suke kai tsaye.

Ana kawo baba alhassan kallo daya yayiwa Sayyid yaji tasa zuciyar na neman bugawa sedai ya dauka zai iya riqewa da jarumta seda aka miqa masa baby aka sanar dashi Ummitah ta zama babu ya zube a gurin shima yana qanqame yar a jikinsa yana hada zufa me tsananin yawa da tashin hankalin dabai taba tsammanin samun kansa a ciki ba.

Dr ken da dr ismail ne sukaita kokarin basa hakuri da hanasa shiga wani mummunan halin kamansu Sayyid sbd kada arasa wanda zai karbesu.

Addua yayita yi yana hada zufa harya dawo hayyacinsa yana jan numfashi daqyar sbd take ciwon zuciya me qarfi ya kamasa amma ahakan ya daure yana danne azabar dayake ji a kirjinsa.

Mama da sayyid din kusan a lokaci daya suka farka,

Babu me karfin iya magana ko wani abu,

Idanuwa kadai suke bin baba alhassan dashi wanda yake kokarin hanasu ganin halinda yake ciki ya bude baki daqyar cikin karfin hali ya ringa musu nasiha da adduar data saka Sayyid zuba masa idanuwansa suna rinewa.

Mama kuwa haka suka lallaba bata iya tsayuwa da kanta baba alhassan ya saka hannu suka karbi gawarda basu saka a ido ba saida aka fito da ita a rufe aka saka musu a ambulance din asibitin dr ken wadda zata kaisu har garinsu a kyauta sbd tausayi da kuma yanda dr ken din ya nuna damuwarsa sosai akansu.

Sayyid na ido biyu da gawar Ummitah rasa kansa yayi ya dafe kirjinsa dake tsananin nauyi da azababben ciwo yana kasa tafiya da kansa saida aka taimaka masa ya shiga ambulance din tareda gawar Mama da baba alhassan da baby wadda Sayyid da mama basusan yama kamanninta yake ba suka shiga motar ABDULAZIZ da drivern daya bar musu.

Duk wasu takardu na tafiya da gawa an basu daga asibitin kai tsaye garin abuja suka bari ko gida basu biya ba zuwa garinsu da gawar dan acan zasuyi janazah.

Mummunan tafiya ce ta qunci da dacin zuciya me tsananin gaske na mummunan rashin da sukai wanda ABDULAZIZ ma kadai da mama ke tinawa takejin kirjinta na tsananta ciwon dayake tsananta mata radadin rashin.

Tinda suka hau hanya babu wanda ya bude bakinsa bare ya iya magana a cikin motarsu.

Acan motar gawar kuwa Sayyid qamewa idanuwansa sukai ya zubawa gawar ido kunnuwansa na daukewa daga jin komai hakama zuciyarsa gaba daya mutuwa yakejin kaman tanayi.

Gefen fuskanta dayake dan fitowa sbd iskan dayake kadawa kadan yana saka abinda aka rufeta ruf har fuska ya zubawa ido tayi wani irin haske fayau fatarta ta dan bushe kaman zata tashi tai masa magana kota ambaci sunan Hammanta.

Baisan lokacinda wani irin kuka mai tsananin gaske da radadin dayakejin bazai iya riqewa ba na tasowa daga kirjinsa ya dafe kirjinsa yana durqushewa gaban gawar yanayi hannuwansa dake dafe kirjinsa suna rawa yana dukan kijrinsa sbd azabar radadin dayakeji.

#MAMUH

#AZIZ AY LIMBA

#UMMITAH LIMBA

#FALAQ LIMBA

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

24

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😄🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😉800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Tafiya ce me dan tsayi wadda ta sakasu isowar yamma sosai da mummunan ganin daya daga hankalin dukkanin jamaar garin sbd farin jinin Ummitah da kaunar da kowa ke mata sbd yayanta wanda duk wanda rasuwarta ta shiga kunnuwansa ABDULAZIZ ake fara tambaya sbd firgici.

Tashin hankali iyalan gidan Baba alhassan da gidansu mama suka shiga me girman gaske tareda kukan da basa ma sanin ya kufce musu cikin rikicewa da tsoro me tsanani ganin gawar Ummitah.

Sayyid koda suka iso baya gani kwata kwata makarantar lokaci daya ta kamasa sbd kuka da tsananin ciwon da kirjinsa yakeci mai tsananin gasken da yana buqatan ganin likita amma ba wannan damar.

Mama ma riqota akai aka shiga da ita gidan baba alhassan wanda a gidan zaayi komai.

A dakin Ummitah aka kwantar da maman wadda itama ganinta da jinta yake daukewa ahankali.

Kasancewar yamma tayi sosai ga gawar ta jima dan haka ba bata lokaci aka fara shirin janazarta wanda Mama da Sayyid ne sukai qarfin hali da dauriyar yi mata wankan gawa da shirinta wanda mama bata gani kwata kwata sosai daurewa kawai takeyi sbd yiwa Ummitah wankan karshe da kanta.

Sayyid ma hakan ne daga garesa sedai qaramin dinkin dayake kirjinta ya zubawa ido yana goge mata shi sbd baisan yaushe taji rauni a gurinba sabo hakan,

Fuskanta ya dawo da idanuwansa yana fasa kukan dayake riqewa yana kasa cigaba sbd numfashinsa dayake sarkewa da sauri aka fitar dashi matar Babansa da mama ma datake kasawa suka qarasa shiryata cikin suturarta ta karshe a wannan lokacin ne zuciyar mama ta gasa itama sedai aka fiddo da ita bayan an fice da gawar Ummitah din wanda Hankalin kowa yake qarasa tashi anata kuka da firgicin tareda tsananin tausayin Dan uwanta dako gawarta Allah bai basa ikon gani ba wanda sunsani har abada bazai taba dena fita daga radadin hakan ba,

Mahaifinsa ya rasu batareda yayiwa gawarsa kallan karsheba sbd babu abinda ya rage a gawar mahaifin nasa wuta ta cinye,

Mahaifiyarsa ta tafiyarta tin yanada kuruciya,tana taye ko a mace bai samu ganin gawartaba itama,

A yanzu ya rasa rai mafi soyuwa a rayuwarsa amma bai samu ko sassaucin ganin gawartaba.

Wannan tinanin kadai yake sake saka mama da duk masu kaunarsa shiga mummunan halin dayake hana zuciyarsu samun sauki.

Sayyid ana saka gawar Ummitah kabarinta yaji wani irin Nauyin daya danne kirjinsa da har abada bayajin zai sauka,

Ahankali hawayen idanuwansa sukai gangarowan dayake jin duminsu har a kirjinsa da tafin hannuwansa dasuka Ummitah a kabarinta.

Rufeta aka fara yanaji yana gani har aka gama rufeta akai mata addua mahaifinsa ya kama hannunsa kaman makaho yana jansa suna barin makabartan yanajin duk taku daya yana rasa ruhinsa da ganinsa sbd dishi dishin dayake gani.

Suna isowa gida suka tarar da Alh saad da iyalinsa sun taho gaisuwa wanda shima yayi iya kokarinsa ne ya tarar da jana'izar amma Allah baiyiba.

Tashin hankalin dayake ciki da iyalinsa su kansu bamai faduwa bane sbd ABDULAZIZ din kawai suma suke kasa tinanin ma Halinda zai shiga din gashi suna hanya kira biyu yayi masa yana cewa a aika gidansa yanason magana dasu mama sbd kaf wayoyinsu basa shiga yanata kira tin dazu.

Kasa fada masa Alh saad yayi sbd yasan Komai zai iya faruwa da ABDULAZIZ din a inda baya tareda yan uwansa dan haka ya zabi boye masa saiya dawo.

Mama koda ake shigowa gaisuwa da magriba bata gane kowa da komai yanda ya kamata dan haka anty maryam ta sanar da Alh saad maman na buqatan ganin likita da gaggawa fa.

Daman basuda gurin kwana a gurin dan haka kwanan zaune sukai a garin ana lallabawa da mama wadda take jin kamar itama mutuwar zatai.

Yanda suka ga safe haka sukaga dare a zaune cikin qunci da damuwa da ciwon rayuka.

Ana gama sallar asuba Alh saad yace su shiry karfe goma na safe ayiwa Ummitan addua su tafi sbd akai mama ga likita.

Mama rikicewa tayi tana cewa bazata iya barin garinba har abada sbd Ummitah na garin.

Wannan kalman nata ya daga hankalinsu aka fara rarrashinta amma sam batama san tanayi ba sbd duk ta rikice kaman ta samu juyewan kai.

Baba alhassan ne da kansa ya shigo ya fara bata magana yana tinatar da ita a yanzu ABDULAZIZ ne wanda ya kamata ace duk sun duqufa roqarwa Allah ya basa dangana da ikon daukan kaddara ya samu sassaucin abinda zaiji tin kafin a fada masa,

Shine wanda yake tsananin buqatarta a yanzu fiyeda kowa daya rasa Ummitah sbd ita kadaice zata iya kulawa da shi idan wannan mummunan labarin ya samesa.

Ambatar ABDULAZIZ kadai idan akai saitaji tana neman sake zarewa sbd kunyarsa da shakkar yanda ma zata sanar dashi Ummitah tabarsa har abada ba dawowa sedai a mafarki ko hoto amma tabbas ABDULAZIZ na buqatanta a kusa sbd duniyarsa ce zata rushe da wannan mummunan labarin.

Addua sosai itama Mama da sayyid akai musu ta dangana aka basu suka sha kafin aka samu Maman aka tafi da ita tareda Sayyid wanda shima Saida akai musu nasiha sosai akan zamansu anan bazai taba dawo da Ummitah ba wadda babu kaunar da zasu saka mata dashi bayan Su kaunaci ABDULAZIZ su tsaya akansa batareda sun bari duniyarsa da rayuwarsa ta mutu gabaki daya akan rashintaba.

Wannan tinin da Mahaifinsa yayi masa ya sakasa jin duk wani asalin tsananin so da kaunar dayakewa Ummitah suna komawa akan Hammanta wanda zata iya bada rayuwarta akansa idan tana raye.

Babu zaman gaisuwan da zaayi dan haka Alh saad na barin garin dasu aka watse cikeda radadi da ciwon rashin Ummitah tareda tausayin yanda rayuwa zataiwa ABDULAZIZ a yanxu da babu ta baida jininsa ko daya a duniya sai abinda Ummitah tabar masa.

Tinda aka haifi babyn daga Mama har Sayyid haryanxu babu wanda yasan yanda take sbd kwata kwata sunma manta da ita matar mahaifin sayyid dince take kulawa da ita tinda suka isa .

A hanyar komawan nasu Anty maryam ce take dauke da babyn wadda sai alokacin itama ta budeta ahankali ta zuba mata idanuwanta tana kalla.

Sanyi jikinta yake dauka cikin tsananin tausayi da mutuwar jiki tana kallan kamannin Ummitah da ABDULAZIZ dake shimfide akan fuskan babyn wadda tin a yanzu da kammaninsu ta shigo duniyar wadda babu komai a cikinta sai son kai da son zuciya da gwagwarmaya tareda kaddarori masu kyau da marasa kyau.

Ahankali ta sauke numfashi tana kai hannunta cikin sanyin jikinta daya tsananta ta rufe fuskan babyn sbd sanyin Ac dayake motar duk da an ragesa sosai sbd Babyn.

Yamma sosai suka iso Abuja suka fara sauka gidan ABDULAZIZ din Alh saad yayiwa Mama da sayyid yar nasihar hakuri da dangana kafin suka wuce bayan Anty maryam ta nanatawa fiddausi kulawa da komai na babyn dasu maman da basa cikin walwala da nutsuwarsu.

Suna ficewa Sayyid yashige yayi alwala ya fita sallan magrib bai dawo ba acan ya tsaya yana karatun Alqurani yana kuka kaman zaciyarsa zata fito kozai samu sassaucin abinda yakeji a kirjinsa.

Yana ishai ya dawo gidan ya shige dakinsa bai sake fitowaba saida safe.

Mama ma da daddare bayan Fiddausi ta gama bawa babyn madara ta sauya mata kaya da pamper sbd batai mata sabon wanka ba tinda bata iya wankan jariraiba,

Dakin maman taxo tayi sallama ta bude tashigo rungume da babyn dake bacci cikin nutsuwar maraici da batasaniba.

Dago idanuwanta da sukai laushi sosai mama tayi ta zubawa hannuwan Fiddausin datake tinkarota da babyn ta miqa mata.

Hannuwanta rawa suka fara ta dagosu tana jin rawar zuciya ta karbeta tana dorawa akan kafafunta tareda bude fuskanta dake rufe,

Tana saukar da idanuwanta akan fuskan babyn bata san lokacinda kuka me qarfin gaske ya kufce mataba tana qanqame babyn wanda take sak mahaifiyarta da tana jinjira.

Fiddausi ma hawaye ne suka fara gangaro mata wainda taketa riqewa rashin Ummitah da tausayin megidan da baya nan dana sayyid sai kuma na babyn.

Kuka sosai mama takeyi wanda ya saka Sayyid fitowa sbd yana jiyo kukan sbd kofar dakin a bude suka barta dan haka ahankali ya tako ya nufo dakin.

A kofar dakin ya dakata idanuwansa na sauka akan fuskar 'yarsa wadda yake hango yanayin kamannin matarsa akan fuskanta.

Ja idanuwansa sukai yanajin tsananin sonta dabaisan yaya zaiyi da zuciyarsa da rayuwarsa ma.

Kallanta yakeyi ba tareda ya qarasa ba ya juya yana barin gurin sbd kukan maman dayake qaruwa yana kankaro masa ciwon dayake kokarin daurewa.

Fiddausi ma juyawa tayi ta fice da dakin cikin tsananin tausayin mama dake jin inama fatima da Ummitah suna duniya su tayata kulawa da ABDULAZIZ da tasan zarewa zaiyi.

A daren mama kwana tayi rungume da yar da har lokacin basama tinanin sunan da zaa saka mata huduba ma Baba alhassan ne yayi mata yace sai ABDULAZIZ ya dawo ya saka mata sunan daya dace.

Washe gari da safe su anty maryam suka dawo gidan da mutane tareda maqota dake shigowa gaisuwa anata jajantawa tareda yiwa babyn data bari fatan rayuwa me albarka.

#MAMUH

#AZIZ AY LIMBA

#FALAQ LIMBA

#SAYYEED

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

25

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

*********A ranar da Ummitah tabar duniya ana ficewa da gawarta asibitin a lokacin aka shiga aikin JANNAH ZAADEN wadda aka shiga da ita iyayenta na kofar dakin tiyatar suna hana kunnuwansu daukan sautin ihu da karar kukan yan uwan Ummitah dake cikin tsananin quncin rashinta

Suna maida dukkanin hankalinsu da nutsuwarsu tareda fatarsu akan samun nasarar da zata bawa Jannah sabuwar rayuwar da suketa gwagwarmaya akai.

Dukkaninsu basu taba shiga tsananin lokaci irin wannan ba a rayuwarsu na jiran dayake saka zuciyoyinsu muguwar bugawan da babu wanda jininsa bai iya hawaba a lokacin.

Securities ne a zagaye da gurin amma sam basu bari hakan ya zama obvious ba amma kwata kwata ko motsin komai bakaji a gurin.

DZAD,DADDY MAHMOUD,MIMI,MOMMY(matar daddy Mahmoud),LUBNAH(yar riqon mommy) sai Maheer wanda ya kasa zama time kawai yake calculating yana jin maqoshi nsa na bushewa,sai Saleem wanda shima yake jin kaman ya shiga dakin tiyatar ya ganowa idonsa ko zai samu sassaucin abinda yake ji.

Dukkanin familyn suna zaune ne babu wanda zuciyarsa ba bugawa takeyi ba da sauri da kuma faduwar gaba.

Su mimi basusan meya faruba kawai abinda suka sani shine an samu donor wanda yayi a lokacinda suka cirewa Jannah rai dan haka suke fatar a dace sbd daga baa dace dinba shikenan wannan karan jannah zata zaka tarihi a rayuwarsu sbd ta lokaci da ake tinanin nata yayi yayi din.

Wutar kofar dakin da aka kashe ce ta saka dukkaninsu miqewa tsaye idanuwan Mimin na gangarowa da wasu hawaye masu dumi.

Dzad kuwa jajayen idanuwansa ya dago ya kalli kofar kirjinsa na wani irin nauyin daya sakasa dafe kirjinsa har Maheer na saurin riqesa.

Daddy mahmoud ne yayi karfin halin bude bakinsa yana kallan Ammar daya fara fitowa idanuwansa jajir wasu hawayen farin ciki na gangaro masa,

Kallo daya yayiwa Mimi hawayensa suka qara gudu baice komaiba ya ware Hannuwansa ta fada jikinsa ya rungumeta da Qarfi.

Dr Abraham ne da Anny suka fito a tare tana zare maska dinta tana kallan mijinta itama cikin farin cikinta dayake bayyane.

Dr Abraham cikin sauke numfashin shekarun fama ya zare mask dinsa Yana kallan Dzad yace

"It was a success atlast sir"

Kuka Mimi ta fasa me sauti tan qanqame Ammar wanda shima yake hawaye yana dariyan farin ciki.

Maheer Anny ya warewa hannuwansu ya rungume yana cewa

"ALHAMDULILLAH"

Dad Zuciyarta kusan kasa daukan farin tai ya zame ya zaune kirjinsa na masa nauyi.

Daddy Mahmoud dr Abraham ya miqawa hannu fuskansa cikeda farin ciki yana masa godia tareda kyautar data saka dr Abraham din sake miqa masa hannu cikin farin ciki.

Saleem ma Dad ya rungume yana cewa

"ALHAMDULILLAH Dad"

Dad kasa magana yayi kirjinsa ya riqe dole akai gaggawar nufar dakin hutawa dashi dr Finn zai dubasa.

Fitowa akai da Jannah a gado ana turawa cikin nutsuwa ahankali dukkaninsu suka miqe tsaye yana zuba idanuwansu akanta zuciyoyinsu fal farin ciki da fargaba tinda ba ganinta sukai ta miqe ba.

Kyakkyawan fuskanta data rame sai dogon hancinta dayake a tsaye dukkaninsu suke kalla suna godewa Allah da ganin wannan rana.

Bayanta suka dunguma zuwa private dakin da aka nufa aka kwantar da ita dr Abraham da Ammar suka qarasa dukkanin abinda zasuyi da rubuce rubuce da komai Dr Abraham ya fice shima Ammar wucewa yayi ya nufi gida sbd kwanansa biyu a asibitin bai fitaba.

Gida ya nufa dan wanka da cin abinci da samun nutsuwar dayake jin a shekaru bai samuba.

Suma Mimi godia suka ringa yiwa Allah Mimi nayiwa Wanda zuciyarsa take jikin Jannah din tareda danginsa kaf da fatar zata samu damar saninsu tayi alkhairin da bata taba yiba arayuwarta dan kuwa zata tattara duka gwalagwalanta ta basu koda kuwa sunada arzikin to su qara sbd batada abinda zata biyasu dashi duniya da lahira.

******ABDULAZIZ duk yanda yaso yayi magana dasu Ummitah abin ya gagara sbd wayar Ummitah bata shiga,ta mama tana ringin baa dagawa ta sayyid ma bata shiga,

Alh saad yace masa suna nan lafiya hakama anty maryam idan ya kirata akan yanason magana dasu magana daya take fada masa data Alh saad din.

Kwata kwata yau kwanaki biyar kenan yana wani irin ciwon dabai san meyake damunsa ba haka kawai ciwon kirji da zuciya yake har jiri sai yana dibansa wanda daga karshe dole yaga dr karshe admitting nasa akai likita yace stress ne da damuwa kawai daya sakawa kansa.

Sosai ya kwana asibitin wanda ya saka likita hanasa ko taba wayoyinsa aka kashesu.

Amma hakan kusan hana zuciyarsa samun nutsuwa yayi wanda yake jin yana rasa nutsuwarsa da hankalinsa kwata kwata dole doctors suka basa wayarsa dan yayi magana da familynsa dan samun nutsuwa.

Wayarce gabaki daya ta kasa samuwa yanda yakeso sbd a cikin mutum uku da suke familynsa kwata kwata ya kasa jin ko daya dan haka kai tsaye ya nemo numbern drivernsa Latif wanda yake bayerabe ya saka kira.

Kiran na shigowa wayar latif gabansa yayi mummunan faduwa sbd bai kira yayi masa gaisuwaba sbd tsoro da tausayin halinda yake ciki jin rasuwar Sanyin idaniyarsa dama su gaba daya tinda suna sonsa dole sike kaunar Ummitan sosai.

Tana gap da katsewa ya daga kiran cikin tsananin sanyin muryan data saka ABDULAZIZ din sauke ajiyar zuciya.

Gaidasa Latif ya fara cikeda girmamawa yana rasa ta inda zai fara masa gaisuwa.

Kafin ya amsa gaisuwarsa kai tsaye da muryansa datai kauri kirjinsa a toshe da bacin ran yanda kowa a gida wayarsa ta koma kaman batada amfani a taqaice yacewa latif

"Inason magana da mama,Sayyid or Ummitah ka kaiwa daya daga cikinsu wayar.....

Tsabar rudewa Latif da yarensa yace

"Sir you say???

Cikin hade fushinsa yace

"Do i have to repeat wat i said??

Da sauri latif na qarasa ridewa ya nufi cikin gidan yana hada gumi yace

"Yes,no no sir"

Duk ya rikice ya rasa me zaice jin sunan Ummitah dan haka ya qara sauri zuwa cikin gidan yana godewa Allah dabaiyi saurin yi masa gaisuwaba yafara ji daga bakinsa..

Yana knocking kofa fiddausi dake palo tana hadawa Baby madara tanata kuka me qarfi ga mama tana sallah Sayyid ma yana masallaci ta taso ta bude kofar wanda ya bawa ABDULAZIZ saukan kukan babyn kai tsaye cikin kunnuwansa daya sakasa tashi ahankali daga zaunen dayake zuwa tsaye yana dago wayar daga kunnuwansa ya kalla ya sake mayarwa yayi shiru kukan babyn me qara yana shiga kunnuwansa sbd tana hannun Fiddausi data taso ta bude kofar tana kallan Latif daya miqa mata wayar da sauri muryansa har tana rawa yace

"Sir na son magana da Mama or oga Sayyid and.....

Shiru yayi yana kallan babyn da sai alokacin ya tina da Sir din zaiji kukanta.

Fiddausi na jin abinda ya fada tayi baya tana qin amsar wayar ta juya da sauri dan kiran mama.

Hanata tafiya latif yayi yana gwale mata idon ta karba kada tai masa haka dan yasan yana saka wayar a kunnensa maigidan zai iya jeho masa kowace irin tambaya.

Fitowan mama tana idar da sallah batareda ta tsaya addua ba sbd kukan babyn ya saka latif saurin jeho qafa palon da sauri ya miqawa mama wayar tana amsa ya juya da sauri.

Fiddausi ma barin palon tayi jikinta a sanyaye.

Mama saida wayar ta shiga hannunta ta gane waye akai take qafafunta sukai sanyi daidai lokacin sayyid ya shigo palon hakama Babyn a lokacin ta sake fasa wani kuka me qarfi na jirirai sabuwar haihuwa ba kakkautawa wanda hake shiga kunnuwan ABDULAZIZ direct yana wucewa zuwa zuciyarsa da bugunta ya sauya ya kasa cewa komai sbd yanda yakejin kukan babyn har cikin tsakiyar zuciyarsa ya tabbatar masa da kukan babyn Ummitah ne.

Shiru dukkaninsu sukai har Sayyid wanda yaga sunan SIR LIMBA akan wayar hannun mama ya san shine take jikinsa yayi mugun mutuwa radadin zuciyarsa na dawowa sabo.

Shirun lokaci mai dan tsayi sukai kafin ya iya bude bakinsa da yayi masa nauyi jin bazasu fada masa komaiba bayan sunsan yaji kukan babyn da sauti me tsananin nutsuwa da sanyi yace

"Ummitah ta haihu ne???

Shiru sukai hawaye na gangarowa mama tana qanqame babyn jikinta.

Shiru ya dan yi yana jiran amsarta kafin ya sake cewa

"Ummitah kece?

Kin sauka dinne?

Kukane yake kokarin kwacewa mama ta miqawa Sayyid babyn wanda yaune ranar farko data shiga hannuwansa.

A tsananin taushin sautin dayake sake qara nauyin zuciyarsa yace

"Ummitah??

Kuka me qarfin gaske mama ta fashe dashi tana kasa riqewa sbd yanda yake ambatar Ummitan da bazata amsaba har abada sai lahira kila..

"Mama" ya furta cikin tsananin mamaki da sanyi yana cewa

"Mama kuna lafiya?

Lafiya kuwa?

Meyake faruwa ne wayoyinku basa tafiya?

Ummitah ta haihu dinne mama???

Maganganunsa kashe mama sukeyi kukanta na tsananta ta kasa cewa komai

Jin ya kasa jeho tarin tambayoyin dake kasheta cikin kuka mai ratsa zuciya da kashe jiki tace

"ABDULAZIZ kana buqatan dawowa,

Muna tsananin buqatanka a gida.....

Rintse idanuwansa yayi abinda yake ji yana fara fin karfinsa daga lokacinda take kukan daurewa kawai yakeyi dan haka cikin tsananin karfin hali da dauriya ya bude baki yace

"Mama zan aje duk abinda nake na dawo,

Ina Ummitah?zanyi magana da ita"

Sayyid na jin hakan ya juya yabar gurin rungume da babyn wadda tayi shiru a jikinsa tana sauke numfashin bacci da zata koma.

Mama shiru tayi ta kasa basa amsa kukanta na komawa sbd tsoron abinda batasan me zata fada masa ba.

Ajiyar zuciya me sanyi ya sauke ahankali cikin sake nutsar da kansa yace

"Mama nace insha Allah duk abinda nake nabarsa zan dawo,

A kiramun Ummitah,

Kuma baki ban amsan haihuwan ba,

Ummitan na lafiya?yaya babyn itama lafiyanta kalau?

Ko akwai matsala ne mama??

A cikin wani azababben ciwon daya taso ya danne zuciyarta da sabon kukan data kasa riqewa tace

"ABDULAZIZ MUNYI MUMMUNAN RASHIN DA HAR ABADA BAZAMU WARKEBA DAGA GARESA"

#MAMUH

#AZIZ AY LIMBA

#JANNAH ZAADEN

#ZAADENS

#SAYYEED

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

26

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Shiru yayi yana gama sauroron bayaninta da bai gane inda ya nufa kafin ya sauke ajiyar zuciya ahankali ya bude baki da nutsuwa sautinsa na sanyaya yace

"Mama meya faru?

Me yake faruwa?

Kukan dayafi na baya ratsa zuciya takeyi sosai tana kasa bude idanuwanta kaman yana gabanta tana breaking tace

"Mun rasata gurin haihuwa.....

Wani irin Numfashin daya saka maman kasa qarasawa ya sauke da wani irin sauti me tsananin nutsuwar son fahimtar abinda ya kasa fahimta yace

"Ita Ummitan???

Kasa amsawa tayi sbd kukan dayaci karfinta mara sauti.

Dif taji yaji kashe wayar batareda yace komaiba.

Wani mummunan jiri ne ya dibesa kafafunsa suka sare da karfi gwiwowinsa suka daki qasa da karfi wayar hannunsa na faduwa qasa.

Rawa hannuwansa suka dauka ya miqasu da sauri yana lalubar wayar hannunsa data fadi sbd ganinsa dayake kokarin daukewa da jinsa dab dif yake jin.

Yanda hannuwansa ke rawa sosai yasaka ya kasa samun inda wayar take duk da tana gabansa sam baya gani.

Kokarin kasa bugawa zuciyarsa keyi amma ya kasa barin hakan,

Hannuwansa ya saka ya murza idanuwansa da karfin daya kusan raunana kansa kafin ganinsa kadan ya dawo ya duba wayar da sauri ya dauka hannuwansa na tsananta rawar datake kokarin hana wayar tsayawa hannunsa.

Daqyar ya iya gano sunan Alh saad sbd rashin ganin da yake sake rufe idanuwansa kwata kwata.

Ringing din da wayar keyi duk daya tafiya yake da numfashinsa dayake fara sarkewa yana suffocating.

Alh saad cikin nutsuwa ya dauki wayar tareda sallama cikin mutuwar jiki sbd duk lokacinda Ko sunan ABDULAZIZ din yagani jikinsa ke mutuwa.

"Ummitah ta haihu??

Meya sameta?

Tana ina?

Inason magana da ita,No i want to See her on a Videocall,

Meyake faruwa,

Why are you quite?

Meyasa mama ke kuka?

Ina Ummitah.

Say something.....

Alh Saad bai zubarda hawaye a rasuwar Ummitah ba amma take yaji idanuwansa na kokarin cikowa da hawayen dake girgiza jarumtarsa da manyancinsa sbd yanda Yana jiyo wani irin mummunan breaking da ABDULAZIZ ke kokarin a muryansa,

Gabaki daya tamboyinsa baya hayyacinsa yake jehosu babu abinda yakeson ji bayan amsa daya.

Acan bangaren cikin sautin daya tabbatarwa da Alh saad jikin ABDULAZIZ din yai tsananin sanyi da wata qasqantacciyar murya yace

"Ta haihu?

Is she okay?

I really want to talk to her,

Am coming back tomorrow amma i cant without hearing from her,

Please,

Please.....a cikin wani irin mummunan sauti me tsananin sanyi da rashin kuzari ko kadan ya ringa maimaita pls dinsa data saka Alh saad karasa karyewa ya sunkuyar da kansa yana shanye hawayensa ya bude baki shima a sanyaye cikin tsananin rashin kuzari yace

"ABDULAZIZ karka manta Duk mai zai dandana mutuwa,

Ka rasa iyayenka ka samu dangana a yanzu ma zaka dangana ne sbd Allah ya riga ya karbeta sbd lokacinta ne yayi,

Abinda ta haifa tananan Lafiya kalau ita kam sedai Mu bita da Add.....

Dif yaji wayar batareda ya qarasa maganar dayake ba,

Daga wayar yayi ya kalla yaga tabbas ta yanke,

Saka kiransa yayi da sauri yana miqewa daga zaunen dayake.

Ringing wayar takeyi harta yanke baa dagaba

Sake saka kiran yayi yana fatan ya dauka sedai harta kuma yankewa baa dagaba.

Cigaba yayi da kiran kaman mahaukaci shima yana fatar a daga amma baa daga dinba karshe ma shiru ta dena shiga kwata kwata.

Damuwa yaji duk ta cikasa sbd baisan irin damuwar da ABDULAZIZ din zai shigaba gashi bai tsaya sauraransaba bare ya kwantar masa da hankali duk da yasan babu abinda zai kwantar masa hankali a yanzu idan ba addua zasu duqufa yi masa ba.

Gaba daya zuciyarsa kasa nutsuwa tayi yaji hankalinsa yana kasa kwanciya dan haka ya dauki wayarsa ya kira Sayyid Wanda aka siyawa sabuwar babbar waya dal yana dauka Yace

"Sayyid Kunyi magana ne da ABDULAZIZ?

Numfashi Sayyid ya sauke ahankali kafin yace

"Yayi magana da mama dazu sedai basu gamaba ya kashe tace"

Numfashi Alh saad ya dauke yana sake shiga damuwa yace

"Inata kiransa baa dauka,

Waye ya sanar dashi??

Cikowa idanuwan Sayyid sukai da hawaye masu zafi yana kallan Babyn datake rungume jikinsa tayi bacci a sanyaye yace

"Babyn Ummitansa ce ta sanar dashi da kanta ta iso duniya..... qarasa maganar yayi hawayensa na sauka akan gefen fuskanta har saida ta dan motsa kadan.

Shiru Alh Saad yayi yana sake shiga damuwa da rashin nutsuwar zuciya yace

"Kukanta ya sanar dashi an haihu kenan??

Kasa magana Sayyid yayi sai daga baya yace "Eh"

"Sayyid kuyita kiransa a samu wani yayi magana dashi pls kaji"

"Ok insha Allah" Sayyid ya fada a sanyaye.

Kashe wayar Alh saad yayi take Sayyid din ya saka kiransa sedai ma ko tafiya batayi yana saka kiran kiran yake yankewa da kansa.

Ringa saka kiran yayi ba kakkautawa amma babu alamar ma kiran zai tafi.

Fitowa yayi ya bawa Fiddausi babyn ta goyata shi kuma ya fita yanata sake kiran Hamman zuciyarsa na tsananin jin son magana dashi sbd tinda Akai rasuwar haryanzu bakinsa da nasa bai haduba bayan yana buqatan jin muryan Hamman ko zai samu Sassaucin rashin Jinin Hamman da yayi.

Mama ya dawo ya sanarwa Baa samun ABDULAZIZ din dan haka itama ta dauko wayarta kowannensu yanata kira amma ba saa.

Har dare suna kiransa akai akai amma sam babu sauyi.

Da daddare mama da kanta ta shirya babyn a cikin kayan sanyi masu tsada da kyau ta kwantar da ita gefenta tareda Zuba mata idanuwanta tana tina ranar farkon haduwarta da Fatima Asalin mahaifiyarsu ABDULAZIZ din wanda tin daga lokacin kauna me karfi da tsafta a tsakaninsu.

Fatima ta tafi tabarta,

Inna ma ta tafi tabarta,

Ummitah ta tafi tabarsu itama tabar musu 'ya kaman yanda Fatima ta tafi tabar musu Ummitan tana qarama,

A yanzu batasan yaya zatai da ABDULAZIZ datasan duniyarsa ta rushe gabaki dayanta,

Yaushe zai samu farin Zamowa ahali daya daya rage a zuriar fatima,

A yanzuma zai sadaukar rayuwarsa ne gurin kulawa da tattali tareda ingata rayuwar 'yar da Ummitah tabar masa,

Yaushe zai samu rayuwar farin ciki da walwala kaman kowa??

A yanzu basusan halinda yake cikiba a can qasar dayake daya samu wannan mummunan labarin.

Hawaye ne sike gangaro mata ahankali ta gefen ido suna sauka akan pillon da kanta yake kai batareda ta dauke kallanta daga kan babyn wanda itama Sunan Fatimar ne sunanta sbd Shine Sunan da ABDULAZIZ yakeso fiyeda kowane suna kuma shine sunan dayace zaa sakawa Babyn daman idan an haifeta sbd Ummansa Fatima ce hakama Ummitansa Fatima ce dan haka a yanzu ma ga wata fatimar ya samu wadda tasan zai iya bada rayuwarsa akanta itama.

Sayyid kwana yayi yana kiran Hamman sbd gaba daya yaji shima bayajin nutsuwa tinda baya tareda su yasan yana can cikin mawuyacin mummunan halin dayafi duk wanda suka shiga baida wanda zai rungumesa ya rarrashesa bare quncin rasuwar Ummitah yana ninkuwa ne sbd ko gawarta bai samu gani ba bare janazah dinta wanda har abada bazai dena jin wannan radadinba a zuciyarsaba kuwa.

Shi kansa Alh Saad akai akai ya ringa sake kiran Amma ba bayanin komai.

Washe gari Sayyid duka yan gidan saida ya karbi wayarsu ya ringa kiran Hamman Amma sam duk abu daya ne batama alamar shiga take yankewa.

Haka suka wuni cikin damuwa da sanyin jiki suna nemansa babu haske ko kadan.

Washe gari ma hakan ce ta faru har aka sake kwana suna kan abu daya.

Alh Saad suka kira suka sanar masa ya kwantar musu hankali da cewan ABDULAZIZ din a ranar da sukai magana ya sanar dashi zai dawo a washe gari amma tinda an kwana biyu a sake basa kwana biyu a gani tukuna kila ya daga tafiyar ne sbd shock na rasuwar.

Hakura sukai suka zuba idanuwan dawowan nasa duk da hakan bawai sun dena kiran bane musamman Sayyid dayake jin yana neman sabuwar zarewa

Mama kuma kulawa da babyn yana dan hanata damun lokacin kanta ma sbd ga manyanci ne ga kula da jaririyar 'ya duk da ga Fiddausi tana kama mata sosai danma wani abin bata iyawa sedai Fiddausin tai mata.

Baba alhassan ne ranar da akai bakwai ya iso da manyan ragunansa guda biyu da na yankawa jaririyar suna.

Dayake ba wai hidimar farin ciki akeba yasaka addua kawai akai aka yanka mata Sunan FATIMAH kaman yanda sukasan ABDULAZIZ yakeda buri.

Koda Baba alhassan ya iso shima Alh Saad ya riga ya siya ragunan suna dan haka aka hada duka aka yanka akai sadaka sosai tareda yiwa mahifiyar babyn Addua dashi kansa ABDULAZIZ da basusan halinda yake ciki.

Baba alhassan bai komaba sbd ganin rayuwar qunci da 'dacin dasu Sayyid sukeyi gashi shima ya shiga tsoro da damuwar rashin ABDULAZIZ din dan haka ya fasa tafiya sai ansan halinda yake ciki.

*****Lamarin da tin suna lissafi har suka dena suga shiga mummunan damuwar datake take rashin da sukai sbd kwata kwata ba ABDULAZIZ ba labarinsa sun duqufa rokon Allah da sadaka,

Mama ta rame sosai ciwo yana neman rufe rayuwarta sbd damuwa da tinani,

Sayyid ma ya koma gabaki daya ko magana bayayi sosai daga daki sai masallaci dayake kusan wuni acan yana karatun Alqurani da adduar bayyanar ABDULAZIZ tareda fatar yana cikin koshin lafiya.

Baba alhassan ma gida ya koma aka ringa yiwa ABDULAZIZ din adduar dangana akan rashin da yayi da fatar yana cikin koshin lafiya.

Alh Saad duk inda zai saka a dubo masa ABDULAZIZ a bincika masa shi a italy abin ya gagara sbd dukkanin wasu hanyar communication da zaa iya jinsa ko labarinsa ta toshe musu sbd Alh saad duk wanda ya sani a qasar italy dazai duba masa shi basa qasar daman duka duka mutum biyu ne ya sani acan baida mutane acan ba kamar uk ko Greece ba ko wasu daidaikun qasar.

Dan haka shima hankalinsa ya tashi sosai gashi ana maganar wata uku ba labarin komai,

Su mama sun koma abin tausayi sosai sbd ciwon tsaye takeyi gadan gadan,

Sunso tattarawa su koma gida shikuma Sayyid yana tinanin kota halin yaya zai neme abinda zai kaisa qasar da ABDULAZIZ din yake ya nemesa sbd zuciyarsa radadi takeyi masa sosai yanaji a jikinsa ABDULAZIZ na cikin matsanancin halinda yake buqatansu.

Mama kuwa gaba daya a yanzu tafara gazawa dan haka Alh Saad ya hanasu komawa gida yace su zauna anan Shi zai tafi qasar ya dubo ABDULAZIZ da kansa.

#MAMUH

#AZIZ LIMBA

#FALAQ LIMBA

#SAYYEED LIMBA

#ZAADENS

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

27

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😉🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki.

****

Tafiyar da Alh Saad yace Zaiyi ya saka Maman da Sayyid samun dan sassaucin Halinda suke ciki.

Baba alhassan na jin hakan shima Ya tattara ya koma gida dayake ya sake zuwa sbd Yiwa Sayyid abinda yake tsananin so yana komawa ya saka gonarsa siyarwa da rabin hatsin daya noma a shekarar yayi kwana biyu yana hada kudin ya dawo da kudi me dan yawa kusan miliyan uku ya kawowa Sayyid suka kaiwa Alh Saad akan a tafi da Sayyid din dubo ABDULAZIZ din.

Itama mama jin hakan ta sake samun sanyi a ranta suka ringa rokon Alh ya tafi da Sayyid din.

Sbd kwanciyar hankalinsu ya amince tafiyar dashi batareda ya karbi kudinsu ba sbd yasa aka fara yiwa Sayyid din komai na tafiya wand hakan ya saka tafiyar ta sake samun tsaiko.

Baba alhassan duqufa yayi da addua da fatar komai ya tafi lfy sbd a zuciyarsa tsoro yaji yana shigarsa.

Mama ma adduar ta sake duqufa yi gashi a kwanakin kullum mafarkin ummitah takeyi wanda take ganin ABDULAZIZ ne a cikin wata masifar kila.

Sbd Lokacinda Ummitah zata rasu mafarkin ABDULAZIZ din ta ringa yi a mummunan yanayi sai gashi ashe rasa Ummitah zasuyi.

Sayyid haka ya ringa jin kaman zai zare sbd jiran shirin tafiya ya kammala visa ta fito,

Karatunsa da Alh Saad ya takura masa yaci gaba da zuwa Sosai ya maida hankali kaman zai kwana ya tashi a ace ya kammala sbd tsananin burin da ABDULAZIZ ya dora akan karatunsa tin farko yasa duk masifar da zuciyarsa take ciki ya tsaya ba gardama yana bude kansa sosai akansa.

Baba alhassan kuwa komawa yayi duk bayan lokaci yana hanyar zuwa abujan dubosu.

Baby Fatima kuwa anata renonta cikin koshin lafiyarta tana girmanta duk da bata samu nono ba jikinta nata yin kyau tana yar kibarta,

Anty maryam sbd basada nisa a anguwa daya suke bata tsallake ranar zuwa duba Baby fatiman da Mama wani lokacin kuma zuwa take ta dauketa acan zata wuni sai dare take kawota a mota dan basa bin hanya da ita duk da da nisan da sai anshiga motar.

Wata daya da sati biyu suka dauka kafin tafiyar ta kammalu suka tsayar da rabar tafiya.

Mama Kallan Sayyid tayi ranar da zasu tafin tana rungume da Baby Fatima ta zuba masa ido tana kasa iya cewa komai sbd batama san me zata fadan ba.

Baby fatima ya kalla kafin ya kalli maman yana bude baki Ahankali yace

"Mama nai miki Alqawarin zan dawo miki da ABDULAZIZ LIMBA a gabanki ko a yaya yake insha Allah sannan zan kula dashi fiyeda nawa kan"

Numfashinta ta hidiye cikin sanyi da samun dan sanyi a ranta tace

"Allah ya tsareku gaba daya ya dawo daku lfy yasa shima yana lafiyar"

Alh Saad ta kalla cikin mutuntawa da kulawa tace ta gode.

Baba alhassan ma addua yayi musu yana yiwa Alh Saad godia.

Mota suka shiga drivern gidan Alh Saad dinne zai kaisu Airport su mama na kallo motarsu ta fice daga gidan.

Ajiyar zuciya Baba Alhassan ya sauke ita kuma Mama kasa sauke ajiyar zuciyar tayi ta juya ciki tana sake rufe Fatima dake bacci a jikinta tana dan motsawa ahankali.

Tinda suka isa airport Alh Saad ya kalli Sayyid wanda kai tsaye kallo daya zakai masa kasan ya sauya daga asalin Sayyid dinsa na baya idan ka sansa.

Har a cikin jirgi bayan sun zauna babu walwala a tattareda Sayyid din dan haka bai takurasa ba ya kyalesa dan yasan zuciyarce ba dadi ko kadan.

******

Lafiyayyan toilet ne dayake da girma sosai komai a tsare,

Qamshi ne me sanyin dadi da nutsuwa yake tashi a cikinsa hakama da dan hayaqin zafin ruwan da ake wanka dasu dayake dan gauraya toilet din yana saka koina a toilet din daukan dumi ahankali.

Wanka takeyi a natse qamshin shower gel dinta me kyau da tsada yana sake tashi harta gama wankan ta kashe shower din tareda miqa hann ta janyo towel ta dauro a jikinta ta fito cikin Lafiyayyar jacuzzi din ta nufo gaban mirror daya kusan cike rabin bangon toilet din ta tsaya cak ta zubawa kanta idanuwanta da suka fara sauyawa ahankali.

Hannunta na dama ta dago ahankali ta dora akan kirjinta seti da zuciyarta dake bugawa ahankali cikin cikakkiyar lafiya..

Tabon dinkin gurin ta shafa ahankali tareda lumshe fararen kyawawan idanuwanta tana sauke numfashi ahankali me dumi...

Tin daga lokacinda ta wayi gari ta samu kanta a sabuwar rayuwa daukeda sabuwar zuciyar datake bugawa a kirjinta tasan duniyarta ta sauya ta dawo sabuwa a daidai lokacinda ta cire rai da rayuwa gabaki dayanta,

Allah ya bata damar cigaba da rayuwa a lokacinda take saka ran ta farko ta samu kanta a duniyar barzahu,

Duk wanda zuciyarsa take bugawa a kirjinta tana masa fatar samun rahamar ubangiji dashi da danginsa a duk inda suke,

Harta bar duniya bazata dena yi masa addua ba sbd sadaukarwansa gareta.

Ajiyar zuciya ta sauke ahankali tana lumshe idanuwanta tana sake jin bugun zuciyar wadda take tata ayanzu yana ratsata cikeda shauqi da samun nutsuwa da yanayin da bata saniba a baya na bugawar Lafiyayyar zuciya a kirjinta.

Ayau kusan wata hudu da kwanaki kenan da aikinta amma haryanzu ta kasa sabawa da sabuwar rayuwar data samun koyaushe jinta takeyi kamar sabuwar mutum sedai kauna da tsananin son datakewa yan uwanta familynta babu abinda ya sauya saima qaruwa da yayi sbd jajirwansu gareta.

Kaman yanda samun lafiyarta ya sauya rayuwarsu gaba daya a qanqanin lokaci sbd sabon farin ciki da jin dadine tareda sabuwar rayuwa ta dawo musu sabuwa dan haka komai nasu ya dawo tamkar baya kusan ma fiye dan farin ciki da kwanciyar hankalin dasuke dashi yanzu na tafiyar da komai yafi na bayan.

Ta jima a tsaye kafin ta juya ta fito toilet din.

Qamshin dayake tashi a bedroom din nata ne ya shiga hancinta ta dan Lumshe ido tana jinsa yana ratsata sbd komai a yanzu jinsa take kamar sabo gareta.

Gaban mirror ta nufa bayan ta zaro wani towel din tana goge jikinta a hankali kamar batason taba soft fatarta sosai.

Da kanta ayau ta shirya kanta sabanin tinda suka gama jinya a asibiti suka dawo gida Mimi ke tayata shiri sbd batason tayi aiki da jikinta ta gaji sbd sun saba a lokacin ciwonta abu daya takeyi zuwa biyu ta gaji sosai ba kuzari.

Body milk me kyau da qamshi ta shafa tareda Turare mai sanyin qamshi ta miqe ta nufi closet nata ta saka undies kafin ta saka oversize skirt and shirt na Liliana ta saka hula me laushi da rashin nauyi a kanta ta fito da slippers a kafarta sbd yunwa takeji abinci take buqata.

Anty Anny ce ta nufo palon itama sanye da shaking doguwar riga mara adon komai sai kudi tana qamshi fuskanta fresh dan itama gaba daya yinin ranar bata fito daga bedroom ma bare palonsu harta fito zuwa nan sai yanzu data fito neman abincin da zata dan duk da a familyn kowa da nasa bangaren amma a hade suke guri daya babu wani rarrabewa sosai dan kusan duka a guri daya suke kowa baifi kayi tafiyar corridor ba zuwa palo da bedrooms wani hakama duk yanda kowa yake bangarensa a tare ake cin abinci dining room dinsu daya ne hakama chiefs dinsu da masu aikin.

Rayuwar hutu kawai sukeyi mazan gidan ne suke fita aiki suma bawai sammakoba tinda sune masu companies dinsu amma matan kuwa da saleem ma sai lokacinda suka ga dama suke fitowa idanma ba abinci zasuci ba saika wuni a gidan bakaga ko

dayansuba sai idan dare yayi ake taruwa babban palon ayita fira da yar hayaniya cikin walwala.

Anny na ganin Jannah ta zuba mata idanuwanta tana kallan yanda take sake warwarewa tana komawa lafiyayyar jannah dinta wadda ita bata saniba a baya,

Wani irin sirrin kyau da kwarjini ne da itama duk da bata gama zama cikakkiyar budurwar data amsa sunanta budurwanba amma haka kawai wani lokacin sai take mamakin saa irinta jannah din kowa sonta yake,

Babu abinda ta nema ta rasa,

Kowa zai iya komai dan bata abinda takeso,

A irin wannan gatan da Jannah din take ciki me zata nema a duniyar nan ta rasa?

Duk yanda familyn suke ganin babu abinda bazasu samar mata indai har tanaso akwai abinda yafi karfinsu shine ikon Allah,

Ita kanta zataso Allah ya kawo abinda Jannah zataso fiyeda komai ko buqata fiyema da zuciyar da aka dauki rayuka da dama akanta amma kaf familyn babu wanda zai bata kuma dukiyarsu bazata taba iya siya musu ba,

Zataso taga wannan ranar sedai batajin tana zuwa dan raine kadai bazasu iya siya mata amma ko rai din da zaace musu ana iya sakawa wani ran wani to tabbas zasu iya sedai Allah bai bada damar hakanba.

Isowan Jannah gabanta ya sakata sake murmushi tana sake kallan Jannah da yanayi na tinani kala kala akan fatan zuwan ranar da jannah zata dandana rashin ba komai ake nema a samu ba.

Da murmushi a fuskanta da kulawa tace

"Hey Jan sai yanzu kike fitowa?

Yaya jikinki?

Ya kikeji yanzu?

Karki manta duk abinda kikaji ba daidaiba ki sanar"

Fararen idanuwanta ta kalli Anny din dasu kafin ta saukar da murmushin kwanciyar hankali a fuskanta tana cewa

"Anty Anny karki damu i dont feel any uncomfortable yanayi,

Am all good"

Gaba tayi anty anny din na bin bayanta tana cewa

"Masha Allah"

Mimi ce itama ta fito a lokacin tana waya cikin walwala da annushuwa tabi bayansu dukansu dining room din suka nufa suka zauna daman dining din baa dauki mintina da yawa da gama shiryasa ba sbd ansan lokacin cin abincinsu na rana yayi kowane time zasu iya fitowa.

Suna zama qamshin Ammar ya doso dakin me sanyi da tsadar gaske tareda rashin hawa kai ko kadan.

Jannah ce taji wani sanyi yana ratsa xuciyarta tareda qamshin nasa ta dago idanuwanta tana kallan kofar daidai da shigowansa sanye cikin black thick riga da wando masu laushi fuskansa fresh da alama bai fita koina ba yau din shima yana gida hutu yake sosai haryanxu.

Kyakkyawan fuskansa jannah take kalla tana jin bazaa samu namijin da zai kai Ammar Zad kyau da kwarjini tareda haiba ba a idanuwanta har abada ba,

Ammar Zad shine mafi kyawun namiji data sani wanda shi kadai take zubawa ido bata gajiya da kalla.

Kallan datake masa ya saka Anny sakin murmushi tana kallansa shima kallan Jannah din yayi yana sake murmushi yana kujera ya zauna yana cewa

"Me Jan Zad take kalla??

Mimi ta kalla kafin ta kalli Anty Anny ta rage muryanta tace

"The one and only Ya Ammar Zad"

Mimi na jinsu farin ciki ya sake cikata tai sallama da wayarta ta kashe ta ajiye tana kallan Ammar din daya zauna kusa da ita yana daukan cup din fresh juice da akai na gida ya kai bakinsa yana cewa

"Mimi barka da rana"

Kafin ta amsa Jannah ma tace

"Sannu da fitowa Mimi"

Anny ma gaidata tai ta hada duka gaisuwar tasu tai musu amsawa daya tana cewa aci abincin tukuna wani zancen.

##MAMUH

#JANNAH ZAD

#AZIZ AY LIMBA

#AMMAR ZAD

#BESTLOVE STORY

#CRAZYLOVE

#BILLIONAIRES WAR

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

[27/12/2024, 3:20 pm] MG: *_Arewabooks@Mamuhgee_*

28

*_LADIES COLLECTION AND MORE_*

08169307477

SHIN MATSALARKI RAMA CE KO KINA SO KI GYARA BREAST DINKI NE?

KINA SO KIYI HIPS HAJIYATA KIYI KYAU?

KO KUWA KINA SO KI RAGE KIBARKI KO TUMBINKI?

KINA SON INGANTATTUN MAGANIN MATA NA GARGANIJIYA?

Kinason shape dinki ya fito kamar yanda kowace mace zatai alfaharin ganinki bare ma oga ko saurayinki da kansa,

Shin kinason ko koma yar dagwas dinki batareda kashe kudin surgery ba kokuma hana kanki cima da dama da kikeso sbd kinason jikinki yayi daidai?

To matsalarki tazo karshe indai ingantattu sahihan maganin gargajiya ne da muka san inganci da gaskiyarsane,

MAZA KI ZIYARCI LADYS COLLECTION AND MORE ko ta waya ko ta asalin inda take ki tabbatar da Buqatarki tazo inda zata biya insha Allah,

LADY'S COLLECTION AND MORE

ANAN NE ZAKI SAMU DUKKAN ABUBUWAN DA KIKE SO KAMAR HAKA □□

Zumar kiba

Zumar breast

Zumar hips

Zumar infection

Zumar sliming

Zumar sabon budurci

Back to virgin

Abayas

Atamfa

Less

Hijabs

Supplements

Kitchen items and more Muna maraba da masu siyan Daya ko

08169307477

Address bayan gidan drugs katsina State

Kayan mu masu inganci ne sosae

Muna aika kayanmu a ko Ina ba tare da wata matsala ba□□□□

SIYAN NA GARI MAIDA KUDI GIDA□

****

Da asuba jirginsu ya sauka Sayyid yana a sanyaye baida wani kuzari ko yin abinda ya wuce bin bayan Alh saad sawu kan sawu sbd kansa dayaji yana juyawa samun kansa a baqon guri inda bai taba tinanin zuwaba ko samun kansa ga jajayen fata tako ina suna wuce suna sake saka kansa juyawa amma ya daure babu abinda yake buqata irin ganin ABDULAZIZ LIMBA.

Mota suka hau wadda kai tsaye takaisu train station suka siya ticket din zuwa Milan wanda acan ABDULAZIZ din yake.

A train ma wata sabuwar duniyar Sayyid yake kalla wadda tale sake juyar da kansa sedai ko dagowa bayayi kansa na qasa Allah yasa kayan sanyi ne masu kyau da kauri a jikinsu dagashi har Alh saad dan haka rashin wayewansa da gurin ya boyu shi kuwa Alh Saad dayake gogagge ne a yawon qasashe sam babu abinda ya damesa sajewa ma yayi dasu banda banbancin fatar amma turancinsa dayakeyi hankali kwance cikin qwarewa yana waya da wanda zai kaisa har gidan ABDULAZIZ

Tafiya sukai me dan tsayin data saka Alh saad jin daya sani flight suka sake bi zuwa milan din..

Suna sauka daga train Station daga nan kai tsaye motace ta daukesu zuwa Address din Fash wanda yake abokin karatun ABDULAZIZ tin abaya amma yanzu basa tare amma yasan sabon gurin dayake zama yanzu sbd dukkaninsu sun zama busy kowa ya samu success din dayake nema.

Koda suka isa gidansa cikin sakewa ya tarbesu tareda riqesu sukai sallolin dasuke kansu sukai breakfast wanda daqyar Sayyid ya tura abincin a cikinsa sbd ba cimarsa bace hakama zuciyarsa kwata kwata a sanyaye take ba dadi ko kadan nauyi yakeji a kirjinsa.

Wayar ABDULAZIZ din shima Fash ya ringa kira ko zaa dace amma still bata shiga ba kuma a lokacinda Alh saad ya kirasa baya qasar shima bai dade da dawowa ba dan haka bai samu zuwa ya dubo lfy ba kuma yayi masa gaisuwar babban rashin da yayi wanda duk wanda yasan ABDULAZIZ sanin daya wuce awanni to tabbas zaisan Ummitah itace rayuwarsa,jarumtarsa kuma karfin dayake riqe dashi a duk gwagwarmayar rayuwarsa hakama duk abinda yakeyi a rayuwarsa sbd cigabanta da ingatata yakeyi.

Saida suka nutsu sosai kafin suka fito a motar fash din zuwa gidan ABDULAZIZ.

Tin a mota sukai tsit babu me magana sai fash din dayake dan kokarin ragewa yanayin nasu damuwa da cewa

"Insha Allah lafia kalau sbd LIMBA yana hakan so da dama idan yana son kadaicewa baya son damuwa"

"Ummnh" kadai Alh Saad yace yana kallan hanya sbd baida abin fada.

Sayyid kuwa shiru har lokacin bai iya cewa komaiba hakama ko kallan gari baida Nutsuwar yi.

Shiru Fash yayi ganin yanayin baya buqatan karfafawa shiru kawai kowa yake buqata.

Tafiyar mintina kusan 40 sukai kafin suka isa dogon building din da gidan ABDULAZIZ yake ciki.

Parking fash yayi yana gaisawa da securities din wajen da suka bude musu hanyar shigowa fededen harabar gurin.

Fitowa sukai dukkaninsu fash da Alh saad ne a gaba suna magana

Sayyid dai har lokacin bai iya dago kansa sosai ba bayansu kawai yakebi a natse babu kuzari.

Lift suka shiga zuwa saman Fash na daga wayarsa da ake kiransa.

Suna isa floor din dayake suka fito fash yana kashe wayarsa suka tsaya kofa tareda sauke ajiyar zuciya ya miqa hannunsa ya danna Door bell dake qara mara damuwa da karfi.

Kofar suka zubawa idanuwa dukkaninsu suna jiran fitowansa.

Sake dannawa Fash yayi yana gyara tsayuwarsa.

Shiru babu motsin alamar bude kofar,

Sake dannawa Fash yaci gaba dayi yana shiga mamaki.

Mintina suka dauka a gurin sunata bugawa babu alamar zaa bude din babu ma alamar akwai mutum a ciki.

Saukowa qasa sukai suka nufi gurin receptionist din building din dake qasan

Fash ne ya kalleta yana mata sannu kafin ya sanar da ita gurin wanda suka taho.

Kallansu tayi dukkaninsu da mamaki kafin ta tsayar da kallanta kan fash da shine a gabanta tace

"His family????

"Yes" yafada yana nuna su Alh saad din wanda shima Alh saad din matsowa yayi yana amsa gaisuwarta kafin tace

"Baya nan for morethan 2 month yana asibiti likitansa yazo ya tafi dashi,

Mutuwa yakeyi ciwo yake sosai.....

Kallanta Alh saad yayi da sauri yana juyowa ya kalli Sayyid wanda bayajin abinda suke fada yana dan nesa kadan hakama turancin ba duka ya iyaba.

Fash cikin Yanke zancen yace wane asibiti and the name of the doctor.

Basu tayi cikin sauri sbd basuda tabbacin ko zuwa yanzu LIMBA din ya rasu sbd a yanda aka bar nan dashi batajin ko kwana daya zai qara a duniyar.

*****A ranar kunnuwansa basu gama sauraron maganar Alh Saad ba yaji tsit bayajin komai jinsa na daukewa ahankali,

Ganinsa ma Fara daukewa yayi qafafunsa ma mutuwa suka fara yi suna gaza daukansa hannuwansa da suka dauki rawa suma mutuwa suka farayi harsuna kashe wayar wadda ta zame daga hannunsa ahankali shida wayar suna zubewa agurin paralyse na kamasa a take.

Buguwa kansa yayi da centetable din dayake tsakiyar palon take jini ya feso daga gefen fuskansa datai mugun buguwar idanuwansa da suka mummunan sauyawa a take na kafe akan wayarsa dake gaban fuskansa batareda ya kafta ba.

Zuciyarsa kokarin dena bugawa takeyi sbd mummunan bugun datai wanda ya sakar masa paralys na take,

Wani irin Radadin da baya misaltuwa ne yake ratsa zuciyarsa dake neman bugawa ta dena aiki gaba jininsa na gangarowa daga gefen goshinsa yana shiga har cikin idanuwansa da suka kafe akan waya bai iya motsa ko dan yatsantsa sbd babu abinda yake aiki ajikinsa bayan zuciyarsa datake matsanancin ciwo da radadinsa yake juyar masa da kai kafin ahankali idanuwansa suka rufe ruf ba alamar rai a jikinsa.

A haka ya wuni a gurin kwance babu alamar rai a jikinsa harya kwana a gurin kwance babu taimakon kowa sbd babu wanda yake shigowa building din saida kwakwaran sanin gurin wa akazo hakama ko securities sun san shi kwata kwata baya wani muaamala da mutane hakama baya wani yawo sosai,

A gurin kwance ya farfado sbd sanyin asuba dayake kadowa a hankali daga balcony dinsa dayake bude yana saukar masa..

Jajayen idanuwansa da ganinsu ya dauke ko kadan ya dena ganin komai ya bude suna wani irin radadin da duk azabarsu bayajin komai sbd har Allah ya dauki ransa dayake fata a yanxu bazai taba jin radadin dayake a yanzu yana yanka duk wani tsokar datake kirji da zuciyarsaba azabar daukan raine kadai da baisaniba yake jin zatafi abinda yakeji yana tarwatse zuciyarsa da kwakwalwansa datake dena aiki,

A yanda yaken babu inda yake motsawa a jikinsa har gari yafara haske ya sake somewa a gurin sbd azaba da radadin dayake kirjinsa yayi masa tsananin da baya motsawa amma azabar tayi qarfin datake sumar dashi ya sake ficewa hayyacinsa.

Mai aikinsu shida wanda yake next floor yazo aikinsa aikinsa guraren karfe 9 na safe kai tsaye ya bude kofar sbd yasan code na budewan.

Iskan dayake kadowa daga balcony ne yana ratso palon me tsananin sanyin gaske ya saka Eden nufar hanyar balcony din bayan ya tafi extra room din dayake kaman nasa anan yake ajiye jakarsa da laptop dinsa ta karatu ko kallo ko wani abin idan yazo da ita.

Sauke jakarsa yayi daga bayansa ya ajiye tareda ledar fresh fruits din dayazo dasu me girma wanda Tin jiyan LIMBA ya basa kudin ya siyo idan zai taho yau.

Da ledar ya fito daga dakin ya nufi kitchen ya ajiye ledar ya nufo balcony din dan rufewa sbd sanyin yayi yawa sosai yana mamakin ya akai Mr LIMBA ya bar balcony din a bude sbd bayason sanyi sosai.

Taku biyu yayi idanuwansa suka sauka akan LIMBA din dayake kwance a kife cikin mummunan yanayi ga jini a fuskansa duk ya bushe ba kyan gani babu alamar rai a jikinsa.

Da gudun gaske ya nufesa cikin matsanancin tashin hankali da tsoro yana kiran sunansa.

Birkitosa yayi da karfin gaske sbd nauyin da yay sosai alamar da gasken ba rai a tareda shi.

Ihun gaske ya sake yana sakinsa ya miqe da sauri koina jikinsa na rawar tsoro da firgita,

Kararrawan neman taimakon gaggawa zuwa ga securities da reception na building din ya danna da hannuwansa biyu yana sake daddanawa ba kakkautawa a rikice.

Ganin kaman hakan bazaiyiba sai kawai ya rarumo wayar Limban datake gefe a yashe ta mutu ya nufi gurin caji da sauri yana kokarin sakawa manager da securities suka iso cikin sauri suna buga kofar ya bude da sauri yana jifa da wayar suka shigo da gaggawa suna ganinsa a hakan hankali tashe aka kira ambulance tareda likitansa dayake kamar Abokinsa

Cikin gaggawa Dr Nico yace ayo asibiti dashi.

A cikin nurses da suka taho da ambulance daukansa tin anan aka gane he is paralysed dan haka tin anan suka fara bawa rauninsa taimakon gaggawa aka kwashesa zuwa asibitin.

A asibiti ana isa cikin gaggawa akai cikin emergency dashi sbd zuciyarsa dake bugawa ahankali kaman zata tsaya hakama numfashinsa dan haka hankalin dr Nico ya tashi dan suna buqatan gaggawar dawo da bugun zuciyarsa daidai idan ba hakan ba zaa iya rasashi.

Kamar kar afara basa taimako ya rikice gaba daya kokarin rasashi akeyi dan haka hankalin likitocin gaba daya ya tashi aka saka masa oxygen ana kokarin hana zuciyarsa dena bugawa,

Kokari sukeyi amma kwakwalwansa failing takeyi wanda kwata kwata baa son hakan...

Duk yanda suka ringa kokarinsu babu abinda yake karban kokarin da sukeyi a jikinsa,

Ba yanda suka iya dole aka yaga rigar jikinsa

Dr Nico yace nurses su kawo Defibrillator

Da gaggawa aka kawo tareda sauran abubuwan Dr Nico ya bawa dayar dr din shi ya fara hadawa da sauri

Cikin sauri dr yace su kunna yafara kirga da sauri ya danna a kirjinsa ya basa AED a kirjinsa wanda ya sakasa yowan sama yana komawa ya zube babu alamar rai a tareda shi..

Da sauri ya sake cewa su basa wuta ya sake manna masa yana cewa

"Com on com on com on LIMBA pls pls pls.....

Cikin sauri nurse tace "hes Getting it Doctor"

Cikeda fatan ya tashi ya hada na ukun yana danna masa sbd daga shi idan bai tashiba shikenan.

Danna masa yayi yana daukewa Nurse tace "dr the heart.....

Bata qarasa ba ya juyo da sauri yana cewa a basa sauran alluran da zai masa da gaggawa.

Dr Nico ne yai masa alluran sbd bugun zuciyarsa ya dan samu karfi.

Aden dayake wajen Emergency din yana kaida kawo cikin fargaba da rikicewa ya zauna ya tashi ya rasa ya zaiyi sbd tsananin Tausayin yanda A lokaci daya LIMBA ya koma kalar tausayi.

Dr Nico damuwa ce sosai a tattare dashi sbd Bugun zuciyarsa ya dawo daidai sedai babu inda nasa yake motsi sun bincika sun tabbatarda ya samu paralys din da shock ne me girman gaske ya haifar masa dashi wanda zuciyarsa take kasa dauka.

##MAMUH

#BESTLOVE

#BROTHERS LOVE

#RESTINPEACE UMMITAH LIMBA

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

29

*_LADIES COLLECTION AND MORE_*

08169307477

SHIN MATSALARKI RAMA CE KO KINA SO KI GYARA BREAST DINKI NE?

KINA SO KIYI HIPS HAJIYATA KIYI KYAU?

KO KUWA KINA SO KI RAGE KIBARKI KO TUMBINKI?

KINA SON INGANTATTUN MAGANIN MATA NA GARGANIJIYA?

Kinason shape dinki ya fito kamar yanda kowace mace zatai alfaharin ganinki bare ma oga ko saurayinki da kansa,

Shin kinason ko koma yar dagwas dinki batareda kashe kudin surgery ba kokuma hana kanki cima da dama da kikeso sbd kinason jikinki yayi daidai?

To matsalarki tazo karshe indai ingantattu sahihan maganin gargajiya ne da muka san inganci da gaskiyarsane,

MAZA KI ZIYARCI LADYS COLLECTION AND MORE ko ta waya ko ta asalin inda take ki tabbatar da Buqatarki tazo inda zata biya insha Allah,

LADY'S COLLECTION AND MORE

ANAN NE ZAKI SAMU DUKKAN ABUBUWAN DA KIKE SO KAMAR HAKA □□

Zumar kiba

Zumar breast

Zumar hips

Zumar infection

Zumar sliming

Zumar sabon budurci

Back to virgin

Abayas

Atamfa

Less

Hijabs

Supplements

Kitchen items and more Muna maraba da masu siyan Daya ko

08169307477

Address bayan gidan drugs katsina State

Kayan mu masu inganci ne sosae

Muna aika kayanmu a ko Ina ba tare da wata matsala ba□□□□

SIYAN NA GARI MAIDA KUDI GIDA□

****

Duk yanda Dr Nico ya dage sosai cikin tsananin tausayawa yana neman lafiyar LIMBA sam babu cigaba sbd baya karban treatment da ake basa sbd Zuciyarsa data riqe da abinda yake cikinta sai sauki baya samuwa,

A kwance yake ba motsi ba magana ba kuka ba kowane irin reaction da ake samu daga garesa dan haka jikin nasa yake sake mutuwa,

Manyan likitocin da sukeda su asibitin Dr Nico ya sako a case din ABDULAZIZ suka duqufa amma sam sbd bayason ya tashi duniyar yakeson bari shima sai babu sauki a zuciyarsa ko sassaucin tsananin quncin dayake cikinta sai anata magani amma ba sauki.

Aden ne yake kulawa dashi sbd ABDULAZIZ yayi masa abinda baitaba samu daga kowa ba,

Shine ya dauki nauyin karatunsa dana kanwarsa sbd duk inda yaga yaya yana son kanwarsa jin yake yana kauna da Tausayinsu dan haka babu abinda bazai iya yiwa ABDULAZIZ LIMBA ba dan haka yake jinyarsa.

****lokaci yafara tafiya babu wani sauyi daga lafiyarsa,

Wata rama yakeyi sosai tana cinyesa daga kwance tana busar da fatarsa,

Ya tara suma da gashin fuskan har lokacin babu abinda yake motsi a jikinsa,

Asalin qunci da radadin da babu magani ne yake cin zuciya da ruhinsa ko idanuwansa bai cika budewa a rufe suke kusan koyaushe sbd basuda kyan gani suma sun kode sun jeme radadi da qunci kawai kake hangowa a cikinsu tareda cire rai daga duniya da abinda duka yake cikinta.

Aden ne ke dawainiya dashi komai shine yake masa cikin kulawa da fatan samun lafiyansa gashi duk yanda zasuyi contacting familynsa an rasa sbd wayarsa ya rasa inda ya yarda ita an nema an rasa dan haka suke dawainiya dashi shida dr nico wanda yayi iya kokarinsa akan ABDULAZIZ ya sassautawa zuciyarsa dan saiya sassautawa kansa zasu samu lafiyar da ake nema masa tafara samuwa amma hakan baya samuwa dan haka ya hakura yana cigaba da kulawa dashi sedai ahakan ya sani ABDULAZIZ bazai dade a duniyarba zai iya samun bugawan zuciya daga kwancen.

***Aden ya sadaukar da rayuwarsa a watannin akan ABDULAZIZ din wanda suka hakura suka cire rai daga tashinsa sbd ya koma ba kyan gani

Ahankali ahankali yake rasa sauran ji da ganin daya rage masa....

Kuka sosai Aden yakeyi a lokaci da dama idan ya kalli ABDULAZIZ din idan ya tina asalin kamanninsa da haibarsa tareda wani irin aji da kwarjininsa tareda tsarin rayuwarsa datake cike da Class da burgewa amma ayau gashi a kwance komai sai anmasa.

Ahakan ya dauki watanni koyaushe suna jiran ji daga familynsa tinda su sun kasa samunsu.

****

Motar fash ce tayi parking a asibitin cikin damuwa da shakkar halinda ABDULAZIZ din yake ciki suka qarasa reception suka fadawa nurse din dasuka samu agurin cewa Dr Nicolas sukeson gani.

Kallansu tayi kafin tace dr Nicolas din ya shiga tiyata sedai su jira.

Kallanta Alh saad yayi yana cewa "akwai patient me suna ABDULAZIZ LIMBA mune familynsa"

Kallansa tayi kafin ta kalli Fash da shima itama yake kalla yana jiran amsarta.

Dawo da kallanta tayi kan Alh Saad tana mamakin lokacinda suka dauka basu taho garesa ba duk mummunan halin dayake ciki baida jininsa a kusa.

Numfashi me sanyi ta sauke tana cewa

"AZIZ AY LIMBA?????

yes" suka ce mata dukkaninsu cikin sauri.

Kallan nurse din kusa da ita tayi ta fada mata familyn Patient din dr Nicolas ne LIMBA.

Itama nurse din kallansu tayi d sauri tana ajiye Wayar datake amsawa da mamaki tace amma basusan halinda yake ciki ba ko?

Yes sukace suna cewa ganinsu kawai suke tsananin so a yanzu.

Room number aka fada musu bayan an duba id cards nasu an dauki sunan da sauran bayanai se dayar nurse din datake kulawa dashi wani lokacin cewa tai su biyota takaisu.

Bin bayanta sukai Banda Fash da akaiwa kiran gaggawa kuma mahaifiyarsa ce dan haka su kadai suka nufi dakin ya juya da niyar zai dawo anjima.

Tinda suka kama hanyar dakin dayake bugun zuciyar Sayyid ya tsananta yana jin jikinsa na sanyi yana jin ciwon lokacinda suka dauka batareda an taho duba lafiya ba jinsa shiru wanda da Ummitah na raye bazata ji dadin hakanba....

A kofar dakin nurse ta tsaya tareda nuna musu su shiga ta juya tabar gurin zuwa aikin gabanta..

Alh Saad ne ya miqa hannunsa ya bude dakin tareda turawa ya shiga kai tsaye yana Jefa idanuwansa

Ko taku biyu baiba ya tsaya cak yana kallan Abinda yake gabansa cikin wani irin tashin hankali da tsoro zuciyarsa na cika da tsoron Allah mai tsananin gaske na ganin ABDULAZIZ yanda koma dan ma kasa gasgata idanuwansa yayi ya juyo da sauri ya kalli Sayyid wanda ya kasa qara taku ko daya daga inda yake yana kallan Hamman Ummitah wanda yake zaune kan kujera an dauresa sa belt sbd baya iya zama kamanninsa kaf sun sunya zuwa wani quncin da kansa,

Tea me kauri Aden ke basa amma baya shiga dawowa yakeyi yana saka tissue me yawa yana goge masa.....

Wani irin kukan dayake tafe da tsananin qunci da radadin zuciya ya kufcewa Sayyid yana tahowa da sauri ya rungume ABDULAZIZ din wanda ya rintse jajayen jemammun idanuwansa a karon farko hawaye masu tsananin dumi na biyowa gefen idanuwansa suna gangarowa.

Kuka sosai Sayyid keyi yana jijjiga ABDULAZIZ din zuciyarsa na radadin dayake jinsa har cikin kansa yana kasa cewa komai,

Kukansa ne yake ratsa zuciyar ABDULAZIZ da babu komai a cikinta empty take yana zana masa mutuwar yar uwarsa a zuciyar....

Zuciyarsa Alh saad ma kasa riqe jarumta yayi hawayene suke gangaro masa yana kallan hawayen dake gangarowa gefen idon ABDULAZIZ idanuwan a rufe.

Tsit dakin yayi kukan Sayyid me wani irin ciwo ne ke ratsa dakin cikin sauti me ratsa zuciya da sake dawo musu da mutuwar sabuwa.

Aden ma kukan yakeyi sbd ganin se yau hawaye ya sauko daga idanuwan ABDULAZIZ wanda zafinsu yake tabbatar da tsananin radadi da ciwon dayake zuciyarsa.

Sun jima a wannan yanayin me kashe jiki da quncin daya dawowa kowa sabo sai ga dr Nicolas daya taho da sauri jin familyn LIMBA din sun zo.

Hawayen daya tarar sun sauko daga idon ABDULAZIZ ya sakasa jin wani relief sbd zuciyarsa ta fara dawowa da feelings din daya rasa.

Kallansu yayi yaga irin yanda Sayyid ke kuka idanuwansa sunyi jajir ya dawo sa kallansa akan Alh Saad suka gaisa yana musu barka da zuwa tareda fara masa bayani akan ciwon nasa.

Numfashi me zafi Alh saad ya sauke tareda yiwa dr din godia mai tsananin gaske kafin ya kalli ABDULAZIZ din wanda idanuwansa suke rife yafara fadawa dr din qanwarsa ce ta rasu gurin haihuwa..

A kunnuwansa yakejin Ana fadar rasuwar Ummitah amma baya iya ko motsawa bare nuna quncinsa dan ya sake rintse idanuwansa radadin kirjinsa na qaruwa wasu sabbin hawayen suka sake gangaro masa yana jin karban ciwo da radadin da zuciyarsa ke masa.

Rasuwar Ummitah ta girgiza dr Nico din sbd yasan kaunar da limba kewa sister dinsa wanda kaunarta kamar dabiace kokuka ace kamar sunansa ne dayake yawo dashi dan haka ya tausayawa ABDULAZIZ tareda tabbatar musu da insha Allah Zai warke amma saiya bawa zuciyarta sassauci.

Duk yanda sukaso magana da ABDULAZIZ babu damar hakan sbd dai ba alamar ma yanaji din duk da yana jin amma basusan da hakan ba,

Sayyid sunkuyar da kansa yayi a gaban ABDULAZIZ daya kasa tashi ciwo kirjinsa yake masa mai tsananin gaske na ganin ABDULAZIZ hakan.

Shi kansa ABDULAZIZ din bai bude idanuwansa ya kallesaba tinda ya rufe dan haka a haka sukai shiru babu wanda ransa ba cike yake da damuwa da qunciba..

Aden ne ya fita dakin ya basu guri bayan ya qarasa goge masa jikinsa.

A asibitin suka wuni sai dare Aden ya tafi dasu gidan ABDULAZIZ din wanda yake fes cikin tsari me kyau da jin dadin rayuwa.

Alh Saad Sayyid kawai ya bari a gidan wani lafiyayyan lodge ya sauka sbd bazai yiyu ya zauna gidan ABDULAZIZ dinba sbd komai na ABDULAZIZ din akan tsari yake hakama ya wuce wani ya zauna gidansa sbd privacy nasa amma Sayyid qaninsa ne ba damuwa bane.

Shi kansa Sayyid bayan tafiyar Alh saad kasa zama yayi yafadawa Aden shima zai bisa ya kwana asibitin.

Dayake basa wani gane zancen juna amma ya gane dan haka bai musa masa ba suka koma tare.

A asibitin a wannan daren Sayyid ne yake kamawa Aden kulawa da ABDULAZIZ wanda tinda suka taho bai sake bude idanuwansaba.

Washe gari Alh saad yazo ya sake tattaunawa da Dr Nico akan ciwon.

Sayyid kuwa hankali ya maida kawai akan lura da komai na kulawa da Hamman sbd ya karbi kulawan dashi da kansa.

A ranar ma a asibitin Sayyid ya kwana tareda aden sai gashi cikin kwanaki kadan ya karbi ragamar kulawa da ABDULAZIZ din Aden ya samu ya maida hankali akan karatunsa.

****Sabon treatment aka fara yiwa ABDULAZIZ LIMBA wanda shima sam baya karba amma dagewan Sayyid daya fara taimakawa gurin dawo masa sa emotions dinsa da zancen Ummitah da fada masa yanda tayi rayuwa a kwanakin datake gaf da barin duniya da irin ciwon data ringa ahankali da yanda take maganarsa sai hakan yake motsasa hawayensa masu tsananin radadi koyaushe cikin gangarowa suke daga idanuwansa.

Kusan wata daya Alh saad ya share a garin anata fama kafin yafara shirye shiyen tafiya bayan an sallamo ABDULAZIZ din sunso dawowa Nigeria dashi doctors suka bada shawarar kada ai hakan su bari ayi treating nasa anan dan haka dole yabarsa tareda Sayyid wanda gaba daya ya koma baida hidima saita ABDULAZIZ din wanda ko idanuwansa bai cika budewa.

Bayan tafiyar Alh saad Aden ya dawo gidan sbd Fita siyayyar abubuwan buqatan gidan da sauran abubuwan da sayyid bai saniba shi kuma Sayyid rayuwarsa ta koma ABDULAZIZ kawai.

****jinya sukeyi me wahala sbd babu alamar sauki har lokacin hakama shi kansa Sayyid din ya koma kalar tausayi sbd yanzu wani lokacin idan trauma din ABDULAZIZ din ta tashi haka zai rintse idanuwansa ya wuni ya kwana bai budesu ba hawayene kawai ke fitowa acikinsu suna gangarowa masu zafi..

A duk lokacinda ya shiga wannan halin Sayyid damuwa yake shiga sosai idanuwansa suyi jajir sbd shi a zuwa lokacin zuciyarsa ta fara bushewa sam baida wasu emotions din yakeji shima.

Lokaci yafara tafiya kwatsam saiga Alh saad da mama da baby fatima ya kawosu sbd Mama dake neman mutuwa itama da damuwa da kunci ga jaririyar da takasa bawa anty maryam kuma ita bazata iyaba sosai sbd ciwo da manyanci dan haka ta koyaushe rokonta yakaita taga ABDULAZIZ kafin tabar duniya hakama akai masa 'yarsa yagani kila ya samu qwarin gwiwan da aketa son ya samu.

Zuwan mama da baby fatima ya qarasa rikita jikin ABDULAZIZ din gaba daya wanda komai ya dawo musu baya sedai kuma a ranar da aka ajiye masa Baby fatiman a kan jikinsa har an cire rai daga samunsa sai gashi Allah yasa yanada sauran kwana gaba dan haka likitoci suka ce a ringa kowota gabansa koyaushe.

Alh Saad ganin rayuwar Sayyid na neman mutuwa ya saka ya yanke shawarar sakasa makaranta yafara zuwa yana kulawa da ABDULAZIZ kuma dan haka ya zama baida ma lokacin kansa koyaushe busy yake.

Mama ganin ABDULAZIZ yasaka nata ciwon warkewa dan haka da ita suke jinyar abinsu wanda cikin ikon Allah aka fara samun yanda akeso sedai babu alamar zai taba komawa ABDULAZIZ dinsa na baya idan ya miqe.

#MAMUH

#THE NEW AZIZ LIMBA

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

30

ZUZEAM VENTURES

Best APHRODISIAC

08144015291

Aslm barkanmu da wannan lokaci

Ina Mai farin cikin sanar daku cewa Zuzeam ventures takawo maku ingantattun magunguna masu inganci cikin Aminci Muna da kaya kamar haka

Mallaka Maganin sanyi

Maganin cire tumbiMaganin farin jini

Maganin matsiMaganin mata

Maganin sa ni’ima da dandano

Dulka Amare Set na gyran jiki

Set na amarya

Tabaje tsumin Gomba

Xuma kiba ta hips and Brest

Magungunan gyran Brest

Magungunan Karin hips

Maganin sliming

Muna da kaya masu inganci cikin sauki da rahusa

Ina wadda keneman mallaka sahihiya quaranty wlh hajiya kixo ga zuzeam ventures xakiji ddin mallaka duk fadin ran ogah duk fadansa wlh sai yyi sanyi 08144015291

Idan maganin mata kikeso akwai

Idan gyran jiki kikeso gyran fata gyran Brest magungunan sa kiba da hips

DOMIN samunta Kai tsaye kira wannan no 08144015291 DOMIN mgn da ita whatapp 08144015291muna tura kayanmu ko ina cikin iKon allah □□□

Bononza Bononza Tsimin mangoro 1k□ Tsimin dabino 1k Gumba ukku balai 700 Gumba aya da nonon rakumi 700 Garin kafi ciccibi 500

Garin bata gaban kishiya 500

Matsin mallaka tada zaune tsaye 2500

Turaren mallaka ba aba mai kishiya 2500 Total kayan 9500

Za a bakisu akan 3800

Kuma mutun goman farko nadakyautar Abun 2k

ASSALAMU ALAIKUM ALHAMDULILLAH YAN UWA NEW PROMO YA KAMMALA□□□□□ □😁😁😁 da 5k dinki ki kwashi kayan 12k hajiyata □□□□□□😄🙃Kazar gadali ta mallara Rabi 3500 Tsimin gam gam 1500 Ruwan kara zunzurutun dadı😋800 Garin 7in1 1k Gumba 3 balai 500 Gumba kwakwa da dabino 500 Infection ruwan tsarki 1k Garin zunzurutun dadi 1200 Matsin ba a fira d wando 500 Matsin infection mai matse mace gam 500 12k All at 5k kedai dannan link dinnan don samun naki ki maza kiyi bucking koda kudinki saida Rabonki

****

Baby Fatima ce ta zamo sabuwar hasken idaniyar data farfado da rayuwarsa daga mutuwar datake wadda baitaba fatar ya tashi ba,

Fatarsa Allah ya dauki rayuwarsa batareda ya warke ba sedai a duk lokacinda ya kalli Fuskan babyn data dauko kamminsa da mamanta fuskan Ummitah yake gani a cikin tata dan haka ta zama hasken zuciya da rayuwarsa da bazai iya ba dan haka tinda tasa kaddarar ahakan tazo itama zai reneta kamar mahaifiyarta ya inganta rayuwarta ya bata gatan da tarbiyar da zata rage masa filin da Ummitah tabar masa dan har abada wannan filin bazai taba cikewaba harya bar duniya sbd Ummitah itace rabin ABDULAZIZ AYOUB LIMBA kuma ta tafi dan haka ta tafi da dukkanin emotions da feelings nasa babu abinda ya rage masa bayan fili a zuciya.

Lokaci na tafiya lafiya tana samuwa garesa amma duk wannan lokacin bai taba bude bakinsa yayi magana suma tin suna jiran maganarsa har suka hakura suna fatar samun lafiyansa tukuna.

A ranar daya fara karban baby fatima da hannuwansa biyu a ranar ne ya bude bakinsa ya fasa wani irin kuka mara sautin daya girgiza mama da sayyid suka shiga tashin hankali gidan yayi tsit a ranar babu wanda ko ruwan gidan yasha da dadin zuciya daci da qunci ne ya cike koina na cikin gidan har dare bai fitoba.

Ranar a gurinsa Baby fatiman ta kwana wadda itama tafara sabo dashi dan bataima wayon sanin waye babanta a tsakaninsu ba duk da Sayyid ya sadaukar nuna mata yakeyi ABDULAZIZ dinne mahaifinta tinda tafara wayo da girma sbd shekara biyu cikin ta uku ake magana.

******Sayyid da rayuwarsa sun sauya sosai acikin shekarun sbd dawainiya da zamowa kaman shine shugaba a familyn yanzu hakama ga huldodin ABDULAZIZ da abokan aikinsa suke tafiyar dasu sosai shine mai bibiyarsu tin bai sababa harya saba ga karatunsa dayake masa wuya sbd rashin qarfin turancinsa ahaka yayita fama harya tsayu ya zama dan qasa ya goge ya wanke ya koma SAYD yanda suke kiransa,

Mama ta dade da dawowa hayyacinta sbd ganin zasu rasa ABDULAZIZ dan haka ta miqe tsaye sukai gwagwarmaya harya dawo kan kafafunsa y dawo ABDULAZIZ wanda ya tashi daga wanda suka sani,

Tinda ya warke bai taba bude bakinsa yai maganar rasuwar Ummitah ba suma sbd gudun janyo masa wani radadin dayake kokarin boyesa aransa yasa basu tada maganar komaiba sbd tin yana ciwo Sayyid yasha fada masa yanda ta rasu da inda take a rufe da janazah da akai da komai.

Bai fara fita aiki ba bare yawon business a gida yake aikinsa da laptop irinsu conference calls da meetings da sauransu.

Jinyarsa bata saka arzikinsa baya ba sbd babu abinda ya tsaya a ciwonsa cigaba akai da business kawai dan haka arzikin yanzu yake take na bayan dan haka yafara kokarin fitowa karban ragamar komai tareda sayyid daya goge a harkan business

da computer daya yiwa karatun qurulla sbd kusan maye ne shi akan duk abinda ya sakawa ran sani dan haka yake kamar wani maye akan karatunsa da aikin da duk ya shafi ABDULAZIZ LIMBA.

**FALAQ AZIZ LIMBA shine Sunan dayake kiran 'yarsa yar kamannin shekara 6 zuwa 7 wadda ta taso cikin gatan daya wuce misali hakama batasan tanada wani ubanba a duniya kaf bayan Daddyn nata wanda take cewa BESTDADDY,

***Sayd ya zama cikakken matashin dayake ji da Ilimi da tsari tareda da Zama final say din AZIZ AY LIMBA sbd zamansa personal person dinsa.,

A lokacinda baby Falak ta cika shekara bakwai a lokacin suka bar italy suka koma United States Sbd sabuwar duniyar datazowa ABDULAZIZ LIMBA ta wani irin kudin dayake tashensu wanda yake zamowa abokin manyan mutane dake ruling qasashe masu powers da iko,

Sayd sake kutsawa yayi a cikin karatun dayake sake sauya rayuwarsa gabaki daya yana komawa kaman black American,

Daga ita har Daddynta Sayd bai taba wasa da duk lamarin daya shafi buqatarsu ko kulawa ba musamman shi din sbd hakan ne ma yasa babu wanda yasansa duk duniya irin Sayd,

Lafiyayyar tanti da a wadace da nutsuwa aka hada masa shida Falaq din dan haka ba damuwa ko wani rashin jin dadi tayi baccinta shi kuwa bai wani yi baccin ba.

Sayd kuwa nasa tantin daban,

Daurewa sukai washe gari aka qarasa sauran activities din aka sake kwan suka tattaro suka dawo cikin farin ta samu abinda takeso karan farko da daddynta yabarta ta shiga irin wannan activities din kuma ya tafi da itan dan haka koda suka dawo bayan gama gaisawa da mama bai tsaya komaiba ba ya shige bangarensa dan yana buqatan hutawa.

Sayd ma hutun yake buqata dan haka abinci kadai yaci ya shige shima.

Ita kam sbd murna yau shirin takeji da mama dan haka a jikin maman ta kwanta tana bata labari kala kala hardana Kyakkyawar lady din data hadu da ita.

Yanda take yawan fadar Kyau da class din Ladyn ya saka Mama tsokanarta da cewa

"To kodai Wannan karan Falaq Aziz taga wadda zata iya bari uban nata ya aura??

Shiru tayi tana sake tino Fuskan jannah din da yanda take magana muryanta ba hayaniya amma kuma tace wani yafi daddynta kyau dan haka ta girgiza kai sa sauri tana bata fuska tace

"She's good amma No daddyna bazai aureta,baya sonta tace wani yafisa kyau kuma tamun tsawa kuma daddyna yafita komai,bana sonta kwata kwata ma"

Fiddausi dake son shan labarin tace

"To inda batai miki tsawan bafa ai da kilan tanada chance ko??

"Kallan Fiddausin tayi tana jikin maman har lokacin tace

"Eh kila,amma dai No"

Mama da zancen ya fara isarta tace

"To indai kin fara tinanin zaki bari uban naki yai auren ai anyi arziki tinda haka ya zaba na biye shirmen banza da tinanin wadda bama hankalin ne da ita cikakke ba"

Falaq bata fuska tayi tana kokarin tashi ta kalli maman tayi magana

Maman ta hanata tashin tana cewa

"Kina cemun witch ko oldLady zanyiwa bakinki mugun dukan da saiya fashe yayi tsawonda sbd muninsa ma ko Babanki bazai ganeki ba"

Shiru tayi tana sake bata fuska qasa qasa tace

"Cewa fa kikai banda hankali kwata kwata kuma kice zaki fasa mun baki,to ni ya zanyi"

Fiddausi dake hana dariyarta fita tace

"Mudai tinda an samu wadda ta burge Falaq Aziz a hakanma munyi arziki,

Kuma zan so na ga wannan din data burge ki"

Murmushi tayi tana cewa

"Banfa nuna mata hakan ba sbd kada taji dadi so kar kiyita fada ma taji"

"To ni ina zan ganta ma bare na fada taji amma dai zamu so ganinta ni da mama"

"Ku cireni a shirmenku bana ciki" mama ta fada tana zare qaramar veil din datake nade da kan Falaq din da ganin kanta daya isa sabon gyara.

Firarsu sukaci gaba da yi itada Fiddausi dake biye mata kamar qaramar yarinya suyita shirme da muguwan wasa shiyasa Fiddausin ta samu matsayi me kyau a familyn sbd yanda take saka Falaq nishadi hakama Falaq din tana sonta sosai.

Da daddare bai fito cin abincin dare ba acan aka kai masa fruits kawai da dabino masu kyau da baa rabo dasu a gidan sbd shi yana cinsu sosai musammam da black tea yake cinsu masu kyan da tsafta sosai.

Babu wanda ya sake ganinsa sai washe gari daya fito breakfast sanye cikin kyan sanyi sbd mura ce tai masa kamu me kyau sbd kwanan sararin da yayi a tafiyar tasu dan hakan nema ya dakatar da komai baya buqatan komai sbd ciwon kai ta sakar masa sosai.

Suna gama breakfast ya nufi office din gidan da Sayd dayaketa kulawa da schedules dinsa.

Zaunawa yayi yana sauraron bayanan Sayd dayake masa akan Sabon sakon ZAADENs daya taho na wannan karan Maheer Zadeen ne ya nemesa da kansa yanason zuwa da kansa dan ganinsa.

Numfashi me sanyi da nutsuwa ya sauke yana cewa

"Zuwa nxt month ka duba menene suke nema,

Yanzu banda time na hakan.

Yaya result da Baba Alhassan sun shigo?

A sauya masa likita.

"Ok insha Allah,

Zaadens dinma already na gama bincika komai akansu tin lokacinda suka fara turo request dinsu and they seems to be clean"

Batareda ya dena karanta abinda yake karantawa na report din wani project dinsu yace

"Zuwa nxt month sai muyi maganar amma yanzu inda abinda yafi koma me sukeso mahimmanci"

Tattaunawa sukaci gaba da yi har tsawon lokaci kafin suka fito.

Da yamma fita yayi tareda falaq din sai dare suka dawo,

Koda suka dawo dr na gidan yana jiransu Sayd ya riga ya kirasa.

Shi aka fara dubawa kafin aka duba falaq din dan itama yasan ta debo sanyi duk da bata mura amma dai ya saba sam baya wasa da lafiyarta.

Kwana biyu ya bawa falaq dasu mama time dinsa sosai kafin yayi tafiya tareda Sayd dan haka Dole mama da falaq din aka koma shiri tinda baya nan maman ce yanzu me lallabata.

Kullum Fiddausi ke tayata shirin school driver ya kaita ya dawo da ita

Da rana islamic/Arabic teacher dinta tazo suyi karatu har yamma kafin ta zauna waya da daddynta dare na yi suci abinci suyi dan hayaniya da Fiddausi tukuna tai bacci.

Haka rayuwarta ta taso haka take dan hakanne ta saba daga ita sai familynta take rayuwa ba wani shiga mutane sosai.

Duk sati biyu ake kaita gyaran kai saloon dan haka wannan satin ma shiryawa sukai Fiddausi ta fito a shirye dan itace me kaita suka nufi mota suka shiga mama tai musu a dawo lfy.

Driver ke jansu suna baya suna kallan wani abu a wayar Fiddausi

Falaq din na kwance jikinta suna dariya kamar daga sama sikaji wani irin qara tareda wani burki me karfin gaske daya saka falaq din samu wani irin firgita.

Cikin sauri Fiddausi ta rungumeta tana kallan gabansu.

Cikin sauri shima drivern ya juyo yana kallan falaq yana cewa suyi hakuri accident ne suka tashi yi amma Allah ya tsare.

Falaq shiru tayi zuciyarta na bugawa da karfi sedai bata iya cewa komaiba ta lafe a jikin Fiddausi wadda itama ta tsorata sosai.

Qarasawa sukai saloon din yayi parking suka fito suka qarasa ciki daidai Jannah itama tai parking a gurin ta fito sanyeda doguwar maroon arabian gown da silk scarf a kanta sai handbag dinta da wayarta dake hannunta ta nufi ciki suka shigo kusan a tare.

Itace ta fara ganin falaq ta miqa hannunta zata tabota sedai hannun nata bai qarasa sauka akan falaq din ba falaq ta yanke jiki a gurin ta zube qasa.

Cikin matsanancin tashin hankalin da Fiddausi bata taba shiga ba ta zube qasa tana kamo falaq din wadda idanuwanta basu rufe ba sedai kokarin rufewan suke tana qanqame hannun Jannah data kama hannuwanta itama cikin tsananin tashin hankali da tsoro.

#MAMUH

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

35

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/JMSe2The4Q2F5tLdzGduyC

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

Fiddausi ce take kiran sunanta da karfi jikinta na daukan rawa sosai tana rikicewa sbd abu ne da bai taba faruwaba tinda falaq din tazo duniya hakama tsoro da tashin hankalin fuskantar AZIZ LIMBA ne yake neman zautata dan haka ta qarasa rikicewa tana girgiza falaq din koina tana kiran sunanta.

Jannah ma sosai ta shiga tashin hankalin sbd itama kwata kwata bata saba da ganin irin wannan rikicewan lokaci daya ba da kuma ganin falaq din a zube.

Kokarin fara kwantarwa da Fiddausi hankali tayi tana cewa ta nutsu tukuna.

Ma'aikatan gurin da suka san falaq sosai tini sukai saurin fara kiran ambulance dan bata taimakon gaggawa.

Jannah ce ta zare hannunta cikin na falaq din da kamar rai ya fita a jikinta ta kamota daga jikin Fiddausi dake neman kamuwa da ciwon zuciya sbd tashin hankali da tsoro.

Jikinta ta kwantar da ita tana shafa fuskanta tana karanto mata adduoi tana kallan kofa da fatar Ambulance din tazo kan lokaci.

Fiddausi data kasa hakura a rikice ta miqe tana cewa

"Bazan iya jiraba muje asibitin kawai,

Muje,muje asibitin i can't take the risk na jiran se lokacinda ambulance tazo,

Pls pls mu tafi nidai...

Yanda take magana a rikice bata tsayawa jin komai ya saka Jannah daukanta cak gaba daya duk da tai mata nauyi.

Fitowa sukai driver dake zaman jiran gamawansu yana ganin fitowarsu da falaq din kamar ba rai a jikinta mugun faduwa shima gabansa yayi ya taso daga inda yake zaune da sauri yana nufosu ko isowa baiyiba Fiddausi data kasa magana da hannu ta nuna masa mota ya juya da gudu ya taho da motar gabansu suka fada dukansu har jannah din wadda Fiddausi ta riqeta tana rokon kada ta tafi sbd tsoro takeji kar abarta da Falaq din ita kadai zuciyarta zata iya bugawa sbd tashin hankali da fargaba.

Yanda ta roketa da yanda itama zuciyarta ta kasa barin Falaq din wannan halin ya sakata binsu suka nufi asibiti tana goga tafin hannun falaq din da sauri sauri ko zata farfado amma sam ko zuciyar falaq din bata bugawa ko kadan.

Kafin su isa asibiti hannuwan Fiddausi rawa sukeyi sosai tana kokarin controlling kanta ta ciro wayarta a jaka ta nemo sunan Mama ta saka kiranta tana sauke numfashi me karfi dayake dan yankewa.

Mama na daga wayar kannewa tayi tace

"Mama muna hanyar asibiti falaq ce,

Bansan meya sameta ba ta fadi bata motsi,bansan meya faruba,bansan yaya akaiba....

Kasa riqe jarumtar tayi ta qarasa zancen muryanta na karyewa da yanayi me damuwa sosai.

Mama ma kanta ne taji ya sara ta zauna daga tsayen datake tana cewa

"Innalillahi wainnna ilayhi rajiun,

Ita falaq din?

Kuna isa ki turomun location ganinan tafe yanxu kuma karki sanar da Sayd sbd kada AZIZ ya sani tukuna"

Kashe wayar Fiddausi tayi sbd sun iso asibitin.

Ciki akai da ita da sauri sukuma suka zauna waiting area bayan ta turawa mama location din tana kai da kawo kama zata shiga taji menene ya sameta.

Jannah kuwa jin tayi itama fargaba da tsoro haka kawai yana shigarta,

Jin take kaman wanzuwarta a gurin bai kamata ba amma kuma ta kasa tafiya sbd haka kawai tausayin yarinyar ke rufeta sbd tana tinawa da lokacin da kuruciyanta take gaba daya a yawon asibiti ta qareta.

Kanta taji yana neman juyawa sbd tinanin halinda ta taso rayuwarta da babu komai a cikinta sai ciwo da kadaici da qunci,

Dafe kirjinsa tayi sbd bugawan da zuciyarta tafara da karfi tana harbawa.

Jakarta ta bude ta ciro maganinta ta bude tayi saurin sakawa a bakinta ta hadiye tana rufe idanuwanta da suka fara cikowa da hawaye sbd itama ciwonta data fito ya zamar mata tamkar trauman da bata iya tinawa sai ta shiga wani hali.

Hankalin Fiddausi bai tashi ba saida aka dauki lokaci baa samu falaq ta farfado ba doctors na shiga serious bincike akanta.

Mama ma data iso samun ba wani bayani akan hakan hankali tashi yayi.

Muryan data sakata juyowa ne ya sauka kunnenta ana cewa

"Ina wuni"

Jannah din ta zubawa ido tana jin yanayi kaman na sani akan jannah din sedai kuma bata taba ganin fuskanba dan haka jikinta na sanyi ta amsa gaisuwan tana mata godia akan kawo falaq din asibitin.

Jannah dataji tsananin tausayi da mutuncin Dattijuwar ya shigeta girgiza kai tayi ahankali tana sunkuyar da kanta daga kallan fuskan maman data cika mata ido da yanayi me sanyi da kauna haka kawai idanuwanta na cikowa da hawaye ta juya da sauri tana maidasu.

Acan gida mama na fita motar data daukosa daga airport tana shigowa dan haka suna shiga securities suka sanar dashi maman ce ta fita yanzu da mota.

Shiru yayi batareda ya dagoba daga wayar dayake dubawa sedai ya dakata daga abinda yake.

Sayd ne ya kalli gurin ajiye motacin gidan yaga babu motar Falaq da ake fita da ita yace

"Falaq fa?

"Ms Falaq sun dade da fita itada Fid"

Sai a lokacin LIMBAn ya dago idanuwansa ya kalli Sayd wanda take ya ciro wayarsa ya saka kiran wayar mama wadda taketa ringin bata daukaba.

Ciki sika qarasa kai tsaye bangarensa ya nufa ya ajiye wayoyinsa ya fada wanka dan sauya kayan jikinsa.

Bai jima ba ya fito sanye da sweatset Off-white na Prada qamshinsa na na tashi a hankali ya dauki wayarsa ya saka kiran maman da kansa.

Ringing ta fara harta yanke baa daukaba.

Ajiyar zuciya me dumi ya sauke ahankali yana kallan time idanuwansa na sauyawa a natse.

Rayuwarsa abu dayane kowa ya sani ya tsana kuma yakewa tsananin qi wato ya kira na gida aki daukan wayansa sbd da hakanne aka boye masa ciwon Ummitah data rasu batareda yazo ya ganta ba,

Ummitah ta dade tana ciwon da aka boye masa wanda ya saka idan ya kira baa dauka sbd kada ya sani,

Hakama Ummitah ta rasu kowa ya dena daukan wayarsa sbd kada a sanar masa har Ummitah tai kwanaki da rasuwa yana duniya da rai da lafiya amma bai taho ga koda gawarta bane duk akan rashin daukan wayansa hakanne ya saka duk duniya baida abin qi da mafi tsana irin ya kira aqi daukan waya sai kuma Nigeria daya yanke zuwa gaba daya sbd baida komai da kowa a cikinta.

Dan hakanne ya saka kwata kwata duk wanda ya sansa baya wasa da rashin daukan wayarsa,

Business koda na billions ne idan ya kira kaki dauka to ko waye kai ya gama Business dakai koda zai rasa billions din shima kuwa shiyasama kwata kwata bai cika kiran mutane ba sedai a kirasa kokuma Sayd da kusan shine yake kulawa da duka calls dinsa sbd sunsha rasa manyan kudaden gaske akan wannan akidar tasa da kuma dole kowa yake binta.

Kaf duniya mama ce kadai take masa rashin daukan waya batateda fushi ko bacin ransa ya bayyana sbd kasancewanta uwa dan haka yanxu dinma bai sake kiranta ba

Wayar Sayd ya saka kira.

Sayd dayake fitowa wanka yana ganin kiransa ya daga yace

"Yes"

"Ina buqatan location na inda Falaq Aziz take zan daukota da kaina" ya fada a taqaice yana kashe wayar ya ajiye gefensa.

"Ok yes" sayd ya fada yana nemo numbern Fiddausi ya saka kira.

Fiddausi na ganin kiransa kanta y sara ta dafe goshinta jikinta na sanyi ta daga kiran sbd bata isa qin daukan wayarsa ba tana aiki a karkashinsu kuma kiransa kaman kiran LIMBA ne da kansa dan shine yake isar da sakon duniya kowanne iri ne na LIMBA.

Tana dauka ta bude baki zatai magana ya katseta da cewa

"Turomun location naku right now LIMBA is coming"

Dago jajayen idanuwanta tai ta kalli mama wadda take zaune ta zubawa jannah idanuwanta cikin nutsuwa tana kallanta sedai damuwa ce a zuciyarta fal gashi tana kallan kiran AZIZ ta kasa dauka sbd batasan ta sakasa damuwa kuma tasan rashin daukan waya shine babban asalin bacin ransa.

Kashe wayar sayd ya saka dukkanin jikim Fiddausi sanyi ta tura masa location din sbd batada yanda zatai kuma dai ciwon Allah ne ya kawo kaddarars koma menene daman tsoronta kada ace ganganci tai bata iya bawa falaq din kulawaba.

Tana tura masa ta kashe wayarta ta ajiye gefe tana dafe goshinta tareda sauke numfashi da ajiyar zuciya a tare.

Sayd na samun location din cikin mintina kadan ya shirya ya fito qamshinsa me tsada yana tashi sanye da three quarter da riga na Burberry milk da key a hannunsa da wayarsa.

Fcap LIMBA ya fito da ita sanye yana kashe wayarsa gida dan bawa falaq time dinsa a hanyar dawowansu gidan duk da zuciyarsa gaba daya tana karban rashin nutsuwa ne da falaq din kawai yake buqatan gani.

Sayd sam bai lura da location dinba saida suka shiga mota ya tayar yana budewa yaga asibiti ne.

Shiru yayi tareda juyowa ya kalli AY dayake shigowa a natse ya zauna.

Jan motar yayi baice komaiba suka nufi asibitin.

Saida suka shiga asibitin yayi parking tukuna AY ya dago ya kalli asibitin kafin ya kalli Sayd kafin yayi magana idanuwansa suka sauka akan motar Falaq sai kuma ta mama duk a guri daya.

Baici komaiba aka bude masa motar cikeda girmamawa ana cewa

"Welcome boss"

Ryan ne drivern Falaq din dayake zaune a cikin damuwa shima yana ganin motar ya taso.

Kafafunsa ya ziro waje yana fitowa Sayd ma fitowan yayi yana rufe motar suka nufi ciki Ryan na cewa

"Ms Falaq Aziz is...

Bai fada abinda zai fadaba Sayd yayi masa alamar yayi shiru kawai sbd LIMBAn da yasan a yanzu daya riga ya gama sanin Falaq ce a asibiti baya buqatan jin bayanin kowa saina likitoci kawai.

Fiddausi da mama ne suka juyo a tare suna kallan hanyar daya sako kai sbd qamshin BLACK VIOLET daya ratso gurin cikin sanyi take suka san shine yake tahowa

a natse ya tinkarosu sayd na gefensa Ryan ba bayansa.

Sunkuyar da kai Fiddausi tayi cikin girmmawa tana bude bakinta a natse tai masa barka da dawowa.

Mama fuskansa da kowannensu ya kasa karantar halinda take ciki ta kalla tana cewa

"Barka da dawowa,

Sayd ta kalla dayake gaidata ta amsa gaisuwansa tana maida kallanta akan AZIZ din daya gaidata kai tsaye ba tareda bayyanar da yanayin komai da komai dagewanka bazaka iya cewa ga yanayinda yake ciki ba ya wuce kai tsaye gurin likitan daya bude kofar emergency room din yana fitowa

Nufarsa kofar yayi daidai da juyowan Jannah dake waya tin dazu a natse da murynata mara hayaniya.

Tana juyowa yana kawowa gefenta wanda qamshinsa ne ya fara shiga hancinta daya sakata dagowa daidai isowansa gap da ita sedai ko alaman yasan da mutum a gurin baiba sbd fararen idanuwansa dake akan dr din daya fito ya rabeta ya wuce.

#MAMUH

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

36

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/JMSe2The4Q2F5tLdzGduyC

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

Kasa motsawa tai daga inda take tsayen hakama iskan qurin ta sauya gabaki daya da qamshin data tabbatarda nasa ne sbd shine ya doki hanci da fuskanta a lokacinda ya wuceta batareda yasan da akwaita bama,

A rayuwarta kaf tinda ta taso bata samun kanta a inda aka taba nuna baasan da existence nataba,

Idan baa kulata da bata kulawa tareda nuna mata mahimmanci ba sbd Sunan familynta to zaayi sbd dukiyar datake dashi kokuma sbd kyau da daukan ido datake dashi amma a karo na biyu an nuna baama san da matsayinta n yar adamba kuma duka daga mutum daya.

Tsananta bugawa zuciyarta keyi hakama ta kasa juyowa ta kalli bayanta da dukkaninsu suka nufa dan bin bayansa zuwa ga doctor.

Muryansa daya ambaci sunan doctor dashine a wani irin nutsuwa ya saka numfashinta fita da wani irin tsananin sanyi daya sakata juyowa ahankali sedai ta kasa kallansa sbd yanda zuciyarta ke bugawa.

Juyawa tayi tabar gurin tana fitowa harabar gurin sbd jin tai tana suffocating.

Tana ji wayarta na ringing kuma tasan Ammar Zad ne amma bata iya dauka sbd nunfashinta toshewa yake haka kawai sbd bugawan da zuciyarta keyi.

Ringing wayar taci gaba dayi amma sam bata iya ko dauko wayar daga handbag dinta.

Taxi ta tare ta fada tabar asibitin ta koma saloon sbd motarta nacan ta baro.

Doctor kuwa kallan AZIZ din yayi yana sauke ajiyar zuciya me tsananin sanyi da nutsuwar abinda yake son fada masa kafin ya bude baki yace

"Muna saka ran zata farfado kowane time sedai a abinda muka bincika ya kawo mata collapsing shine ta samu bugawan zuciyan da yayi triggering matsalan datake dashi a zuciyanta wanda muna jiran fitowan sakamakon duka binciken da muka fara yi mata na dan abinda muka gani tukuna.""

Shiru gurin ya dauka sbd babu wanda ya motsa a cikinsu kallan likitan suke kamar basu fahimci abinda ya fadan ba dan haka ya kallesu shima likitan daya bayan daya tukuna ya tsayar da kallansa akan AZIZ da shima bayanin yake buqatan sake ji sbd a lamarin daya shafi iyalinsa yanason a ringa masa dalla dalla.

Ganin hakan dr ya sauke ajiyar zuciya yace

"Mun dan gano tanada matsala a zuciyarta sbd yanayin bugun zuciyar nata da muka duba vayan dawowansa ba bugun zuciya bane na cikakkiyar lafiyayya,

Bai taba bayyana va sai yanzu data samu bugun zuciyan dayayi munin daya bayyanarda ciwon gaba daya,

Amma muna jiran sauran result da kuma wainda zamuyi mata dan tabbatarda komai"

Hawaye ne masu tsananin zafi suka tsinkewa Fiddausi suna gangarowa akan fuskanta tayi baya tana komawa nesa dasu ta zauna tana cusa kanta cikin kafafunta.

Mama kuwa gaba daya bata gane turancinba dan haka sayd da AY din take kalla tana jiran reaction dinsu ya bayyanar mata lafiya ko ba lafiya ba.

Sayd wani irin nauyi ne ya danne kirjinsa da daci dayake gauraye bakinsa gaba daya idanuwansa na sauyawa sedai bai bari hakan ya bayyanaba ya danne tareda dagowa ya kalli AZIZ AY LIMBA wanda kafafunsa suka so kasa daukansa duk jarumtarsa.

Saurin taresa mama da sayd din sukai tare ya kasa dago idanuwansa ya kalli ko dayansu sbd yanda sukai jajir a take cikeda mafi girman 'dacin zuciya da wani irin

nauyin daya danne kirjinsa da babu komai a cikinsa sai fili da tarin quncin daya taso a cikinsa.

Kujeran aka kawo masa da sauri ya zauna har lokacin bai iya dagowa ba bare iya cewa komai.

Sayd ne ya kalli dr din da jajayen idanuwansa da suka sauya sosai shima sbd su bazaka iya controlling nasu ba ya bude baki yana kokarin daidaita kansa yace

"Ok dr zamu jira results din da duka sauran bayanan,thank you"

Juyawa dr yayi ya koma ciki tareda nurse data fito kiransa.

Shiru gurin yayi babu wanda ya iya magana sai sayd da mama take sake tambayar ayi mata bayanin meya samu Falaq din sbd itama tin bata jiba ganin yanayinsu ya sakata jin ciwon zuciyarta na neman tasowa dan kirjinta toshewa yafara yi fargaba na shigarta me girma.

A taqaice sayd yayi mata bayanin abinda aka fadan yana dorawa da kada ta damu insha Allah khairan.

Duk yanda taso daurewa kasawa tayi kirjinta ciwo yake mata dan haka Fiddausi dake kuka sayd ya saka ta kawowa maman ruwa ya bata yana cewa nurses su kira doctor ya dubata.

Yanda ya zauna baice komaiba shiru yayi sukaci gaba da zaman jira.

Sallah sukaje sukai suka dawo cigaba da jira amma ba wani zance karshe dai an fito da falaq din zuwa vip room dayake can sama dan haka suka koma can.

Shiru dakin babu maganar komai sbd uban gayyar baicewa kowa komaiba har lokacin

farfadowan falaq din yake jiran gani tukuna har doctors din ya samu magana dasu kafin su wainda suke tareda ita da abinda ya faru.

Mama dai dole aka maidata gida sbd duk ta rikice jikin nata ya tashi dan haka gida aka maidata gida tareda Fiddausi ma da nurse da sayd ya daukan mata.

AZIZ dinne ya kwana a asibitin a zaune sai sayd da shi duk inda ko inuwar AZIZ take yana nan.

Guraren 8 na safe ta farka cikin tsananin sanyi da rashin walwala ta ciwon daya sauyata a lokaci daya.

Tana bude idanuwanta akan Daddynta ta fara saukesu hawaye masu dumi suka gangaro mata ta gefen fuskanta ta bude baki Ahankali tace

"BestDaddy"

Har cikin ransa yaji saukan sanyin muryanta wani irin daci da qunci yafara cike koina a zuciyarsa ya bude idanuwansa da suka kasa komawa daidai ya zuba mata yana tayar da ita zaune ahankali yana dora hannunsa akan fuskanta ya shafa ya bude baki da muryansa me nutsuwa yace

"Hey Falaq Aziz limba,how are you feeling?

Wasu hawayen ne suka gangaro mata ya ciro handkerchief dinsa yana goge mata ahankali yace

"Yaya dai?kina jin ciwo ne?

Where?a aina?

Kwantawa tayi jikinsa tana girgiza masa kai alaman batajin ciwo koina.

Dr ne ya shigo ya qara dubata dakyau kafin yace zuwa anjima ma zasu iya tafiya gida ba damuwa ko matsala bane.

Angama dube dube da sauran duka test da full checkup da AZIZ yace ayi mata sbd yanason a bayyane masa komai daya danganci abinda yake damunta komai yanason a bincika a sanar masa zai nema mata lafiya indai Allah ya yadda ta samu lafiyar koda zai rasa komai daya mallaka.

Koda suka dawo gida gabaki daya babu wata walwala ko haske ko kadan a tattare dashi suma duka gidan jikin kowa a mace yake sedai sbd falaq din su Fiddausi da mama suka sake sunata kulawa da ita da wasa dan ta sake kuma tafara sakewan sbd rashin qarfine kawai na wuni da kwana a kwance yake Damunta sai kuma asalin weakness da ciwon yake sakarwa meshi datake ji.

Doctors sun sanar dashi results da binciken duka suna kammaluwa zasu kirasa yazo ayi masa bayanin komai dan haka duka schedules da ayyukansa na wannan lokacin ya saka sayd yayi cancelling nasu ya bawa falaq time dinsa sosai wanda hakan ya sakata komawa daidai rigimarta da komai ya dawo musamman dataga mama ta dena mata fada dan haka murna ta ringa yi da ciwon datai.

Ryan kuwa tini ya sallamesa aka daukan mata wani drivern bayan an sanar dashi daga lokacinda yayi wani gangancin da ita a mota ya gama aikin.

Shi da Sayd ne a cikin damuwa sosai akan tinanin ciwon nata wanda basu gama sanin yaya yakeba dan haka koyaushe cikin jiran kiran doctors yake hakama sayd

Ciwone yake cinsa na tsakanin Uba da 'ya tinda aka fada ciwon sedai kawaicinsa da yanda yabarwa AY ita bai nuna damuwarsa a fili ba dan haka ya fara bibiyan bayanan ciwon zuciya da matsalolinta.

Ganin hakan sai mama ma suka nuna mata ba wani damuwa bane falaq will be ok insha Allah,

Da wannan maman ta sake itama ta koma yanda take.

Tinda ya taso bayan rasuwar mahaifinsa zuciyarsa tafara bushewa daga mutane da lamarin duniya,

Ya rasa Mahaifiyarsa zuciyarsa ta karbi hakan cikeda jarumta da taurin zuciyar daya reni qanwarsa dashi,

Ya rasa Ummitah dayafi so a duniyarsa fiyeda komai da kowa zuciyarsa ta rasa duk wani emotions daya wuce na falaq,

Ba masu fada ba shi kansa yasan zuciyarsa a bushe take shiyasa a duniyar tycoons ake kiransa da monster amma baisan meyasa yakejin zuciyarsa na neman karyewa akan ciwon dayake tafe ga 'yarsa daya tak da itace kuzarin datake riqesa daga collapsing a duk lokacinda rashin Mahaifiyarta ke neman illata kwakwalwa da tinaninsa tareda jinsa da ganinsa.

Rufe idanuwansa yayi Ahankali yana hadiye abinda yake cikeda zuciya da kirjinsa.

Sayd ne yai knocking ya bude kofar palon y shigo a natse yazo gabansa ya tsaya cikin girmamawa da nutsuwa yace

"Hospital sun kira the results are out da komaima"

Bude idanuwan yayi Ahankali tareda zubasu akan sayd din wanda ya sauke nasa idanuwan.

Shiru gurin y dauk kafin ya miqe yana daukan wayarsa dake gefensa yana cewa

"Lets go"

Bayansa sayd yabiyo yana zuwa inda keys din motocin gidan yake ya dauko key yana biyosa da sauri.

Mota suka shiga zuwa asibitin batareda kowa yayi magana a motarba har suka isa.

Suna isa kai tsaye office din dr A Raheem suka nufa wanda shine babba gaba daya a asibitin suna isowa shine da kansa ya budewa AZIZ din kofar shiga yana masa barka da zuwa.

Amsawa yayi yana gaisawa da doctors biyu dake dakin wainda manyan neurologist ne wanda sune zasuyi masa bayanin duk abinda ya shafi ciwon yarsa.

Shiru office din yayi bayan Dr Raheem ya gabatar masa dasu fara koro bayaninsa yayi cikin tsananin nutsuwa.

"Mr LIMBA kaman yanda aka fara sanar da kai tabbas 'yarka na dauke da ciwon rashin qwarin zuciya wanda dashi tazo duniya sedai baya nunawa sbd the more tana girma the more yake kokarin fara bayyanarda kansa,

A yanzu ya bayyana ne sakamakon shock ko mummunan bugawan zuciyar data samu,

Ciwone chances din warkewansa yake 20%

Zaici gaba ahankali ahankali zuwa lokacinda zuciyarta zata buqaci heart transplant maana dashen zuciya kafin tata ta iya dakatawa,

Ciwon wasu yakan zo musu da rami ne a zuciya kaman hole haka".... ya fada yana kunna musu qatuwar screen din dake office din yana nuna musu yanda ciwon yake.

#MAMUH

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

37

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/JMSe2The4Q2F5tLdzGduyC

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

Screen Sayd ya zubawa idanuwansa yana kallan yanda ake nuna musu cutar take a zuciyar dan adam.

AY idanuwansa da sukai jajir har suna radadi ya zubawa dr din kunnuwansa na ji masa mummunan labarin dayafi rasa komai da komai daya mallaka muni.

Dr kuwa cigaba yayi da cewa

"Zaa dorata akan activities da zaa fara kiyayewa da dorata akai tin yanzu batareda an daga mata hankali tasan meyake damuntaba dan tayi qanqanta data san hakan kuma sbd Nata baiyi nisan da zaa cire rai ba sedai kuma bamusan abinda gaba zatai ba wadda idan har ankai stage din da baaso to sai anyi mata heart transplant din wanda samun donor shine abinda yakeda wuyar datafi komai a duniyar nan"

Hotuna da videos na yanda ake heart transplant ya kunna yana cigaba da musu bayani cikin kwantar musu da hankali da kokarin ganin ya fahimci komai tareda sanin ba wani abu ne me mugun tashin hankaliba sbd ciwonta baiyi nisa ko girman da zai gagaresuba insha Allah.

Sayd dagowa yai ahankali daga jinginen dayake yana saukar da idonsa da kyau akan hotinan dake yawo akan babban screen din na heart transplant da asalin tabon dayake bari a kirjin da duk aka cire zuciyar ko dasata.

Kasa dauke idanuwansa yayi daga hoton wanda ya saka kunnuwansa daukewa daga jin sautin bayanin da doctors keyi sbd mamaki me tsananin gaske da shock dayake neman shigarsa sbd sanin wannan shine irinsa sak a kirjin Ummitah wanda bai taba saninta dashi ba dan ko ranar da zaa kaita asibitin haihuwa shine ya saka mata kaya da kansa dan bazata iya ba kuma babu wannan dinkin a kirjinta sai bayan rasuwarta ya gansa.

Juyawa kansa ya farayi sedai kuka Cs akai mata aka ciro Falaq,

Ana cs na haihuwa a kirji ne??

Girgiza kansa yayi idanuwansa na sauyawa yana kokarin tina babu dinkin cs da akai mata a mararta.

Jin yayi ya dena gane komai kansa na yin dum..

Jajayen idanuwansa da suka sauya gaba daya a take ya kalli dr Raheem ya bude bakinsa muryansa a shaqe yace

"Dr a wane gefe na kirjin ake aikin?

A jikin dan adam akwai inda zaa iya masa tiyata a cire 'da bayan cikin?

Meye dinki a kirji kuma a bangaren hagu yake nufi??

Kallansa dr yayi yana mamakin tambayarsa

AY kuwa sam bayama cikin cikakkiyar hayyacinsa na fahimtar me Sayd din yake tambaya yana zaune shiru idanuwansa sunyi laushinda ayau zaka gane rauninsa a bayyane.

Cikin bude masa komai da kyau dr yace

"Babu inda ake iya cirewa mace baby bayan cikinta maana qasan cikinta wanda wasu ana yankan tsaye wasu kuma na kwance,amma idan har kana magana ne akan wannan yankan na setin zuciya wanda ya tafi daidai irin wannan da kake gani to idan a jikin rayayye ne akwai tabbacin antaba masa aiki a zuciyar, idan kuma matacce ne to tabbas shima anyi masa aikin ne a zuciya kokuma ma an cire zuciyarne tinda a macen yake"

Jiri ne ya dauki Sayd daga zaunen da yake sbd kansa kasa gane komai yai

Jin yake kamar bai taba zama aji karatu ba sbd jin yayi turancin ma kamar ya dena ganewa dan haka ya juyo idanuwansa da sukai nauyi sosai ya kalli AZIZ wanda shima kwata kwata jinsa yai qasa akan bayanan likitocin gameda ciwon daya bayyana lokaci daya a tattareda rayuwar yarsa wadda bayan kuruciya ma yanzu babu abinda zata gane a ciwon ko anmata bayani.....

"Innalillahi wainnna ilayhi rajiun,Ya salam"

Ya fada yana tallafe goshinsa da hannuwansa biyu idanuwansa na rufewa ya budesu tareda jimawa shiru kafin ya dago ya kalli kowannensu ya bude baki baki yayi musu godia tareda miqewa.

Sayd ma miqewan yayi baa hayyacinsa ba sbd yayi mugun zurfi da nisa da tinanin dayake sake toshe kansa.

Ta email akaiwa Sayd forwarding copies na results dinta da sauransu sbd duk inda zasu sauya ganin likita ko qasar ma zai zamana sunada record dinta.

Tafiya suke babu me magana hakama babu wanda yake cikin cikakkiyar hayyacinsa har suka isa mota suka shiga kowannensu yayi shiru.

Sayd kasa tada motar yayi sbd bayajin zai iya driving cikin daurewa ta juyo ya kalli LIMBA da babu abinda yake iya cewa sai yaji tsananin tausayinsa dan ganin rauninsa da karyan kowa ne yace ya gani.

Jin yayi jarumtarsa ta dawo dan shine tamkar bangon dayake taresa a duk lokacinda rauninsa ya taso dan haka yake koyaushe a shirye daya basa kariya koda shi zai rasa nasa ran sbd kaunar Ummitah data hadasu haduwa ta har abada.

Numfashi me sanyi da ciwo ya sauke yana dora hannunsa ya tada motar yana tattaro nutsuwa da karfin hali ya hau hanyar gida.

Tafiya ce ta damuwa da rashin haske ko kadan a cikinta sukai har suka isa gida..

Suna isa kai tsaye babu wanda ya gansa ya shige bangarensa ya rufe kansa sai alokacin yaji kirjinsa nai masa radadi da ciwon daya sakasa zubewa palo qasa yana dafe kirjinsa yana lumshe ido yana karban radadin sbd babu yanda zai iya dauresa.

Yana jiyo ihun falaq din da Fiddausi da dayar me aikinsu a baya suna wasan daya sakasa rintse idanuwansa yana jin inama shi Allah ya kaddarowa wannan ciwon ba Falaq ba sbd harko yaushe yana fatar kasancewa da Ummitah koda a fatalwa ne idan har zasu hadu.

Falaq ce jinin Ummitah daya rage masa a duniyar,

Falaq itace take rage ciwon radadin rashin mahaifiyarta daya bar zuciyarsa empty idan har ciwonta barazana ce ga rayuwarta da zata iya rasa zuciyar da itace rayuwar yaya zaiyi da wannan kaddarar da Allah daya kaddaro masa shi kadai ne zai kawo masa dauki...

Zuciya ce zata buqata idan lokaci yayi wanda ba aba bace da tarin dukiyarsa zata siya,

Meye amfanin kaf abinda ya mallaka idan har bazasu nemo masa abinda zai buqatan ba?

Falaq dake wasan ruwa da water guns dasu Fiddausi farin ciki kawai take jin kanta yana ciketa wasa sukeyi sosai batama san daddynta ya dawo ba kuma yana jiyota radadin zuciyarsa na qaruwa duk dariyarta ta shiga kunnuwansa sbd ahankali ahankali wannan farin cikin da dariyar zasu disashe daga rayuwarsu kenan.

Sai magrib suka dena wasan suka dawo ciki Fiddausi na janta daki ta sakar mata ruwan zafi sosai sbd sanyin da sukai wasa dashi karya kamata.

Cikin jallabiya milk me tsadar gaske ya fito fuskansa tayi fresh sbd wankan da yayi ya fiton,.

Fuskansa babu walwala ko kadan sedai sam fuskansa bata bayyanarda fushi,

Sayd ne shima ya fito sanyeda riga da wandon fendi masu haske suka nufi masallaci wanda saima anyi tafiya da mota ake zuwa.

Koda sukai sallan magrib basu dawoba a masallacin suka tsaya AZIZ din karatun AlQuran ya ringa yi har lokacin isha yayi akai sallah suka fito suka kamo hanyar zuwa gida.

A hanyar ne ya dan kalli Sayd din a natse kafin ya maida kallansa kan Wayarsa yace

"Kafin gobe a saka binciken qwararrun manyan likitocin zuciya na duniya gaba daya zan gansu"

"Yes AY" Sayd ya fada yana ciro wayarsa dan fara saka binciken.

Suna isowa gida ya nufo ciki yana sako kai falaq dake fitowa hanyar bedroom din mama da gudu tayo kansa tana murmushin farin cikin ganin halittar datafi mata kowa da komai tana cewa

"BestDaddy"

Rungumeta yayi yana sauke boyayyar ajiyar zuciya da wani lafiyayyar murmushi daya sakawa fuskansa wani irin sabon nutsuwa da kwarjinin gaske.

Sayd bai qaraso ba bedroom dinsa ya nufa yana wayoyi..

Yana gama wayar ipad dinsa da tinda suka dawo asibiti yake kai yana wani irin binciken dayake neman juyar masa da kai,

Gaba daya zarewa yake neman yi kawai daurewa yake sbd kada AZIZ yasan komai akan abinda baida tabbaci amma kuma ya tabbatarda dinkin kirjin Ummitah sabo ne kuma a asibitin data haihu ta samesa sbd ya sake tabbatar da cewan ranar da zasu tafi da ita koda ya saka mata kaya a jikinta babu raunin komai a jikinta bare dinki,

Kuma a yanzu bayan dawowansu ya rufe kansa a daki ya kira likitocin duniya sunfi goma zance daya suke basa akan abinda dr Raheem ya fada baa taba aikin komai a kirji kuma bangaren hagu saina zuciya hakama indai mace ta haihu babu alamar tiyata a qasan cikinta koda daga gefe ne to da kanta ta haihu ba cs akai mataba.

Dafe kansa yayi dayake juyawa yana neman zare masa idanuwansa sukai jajir,

A ranar da aka shiga cs da Ummitah babu kowa a bangaren kaman yanda babu ko hayaniya alamar kebantaccen guri ne dayake nuna alama da vip area ne na asibitin,

AZIZ baisan suna meyake faruwa ba bare yasan asibitin dasuke bare yasa a basu special treatment hakama Alh Saad baisan suna asibiti a lokacin ba sbd basu tsaya sanar da kowa ba sbd tashin hankali,,,,to meyesa aka kaisu Vip area din????

Ko sisinsu baa karba ba idan ya tina harsuka bar asibitin da gawar Ummitah.....

Miqewa yai da sauri ya nufi windon dakinsa ya bude iska ta daki fuskansa ya rintse idanuwansa sbd sarqewa numfashinsa keyi yana neman zaucewa...

Iska ya shaqa numfashinsa ya dan dawo daidai ya dawo da sauri ya wafci ipad dinsa yana sake bin bincikensa daki daki sedai yasan shedan ne kawai keson illata zuciyarsa da tinaninsa dan babu yanda zaayi ace anyiwa Ummitah aikin zuciya basu saniba,

Kodai dataje rasuwa ne sukai kokarin hana zuciyarsa dena aiki sukai mata aikin zuciyar??

Me wannan tinanin yakeyi a kansane??

Menene yake damunsa?

Wane irin jahilin tinani ne wannan yake yawo akansa??

Laptop dinsa dake bude itama yana binciken da ita ya duk ya rikice yayi da wayarsa yayi da ipad yayi Laptop ya kira waya duk ya neman haukacewa yake neman yi.....

Cikin wani irin zafi ya dauki Laptop din ya bugata da qasa yana yana dafe kansa tareda zubewa a couch yana rintse idanuwansa hannuwansa na dan rawa.

Numfashi yake saukewa da karfi karfi yana sauka ahankali yana kokarin dawowa daidai hayyacinsa.

Bude idanuwansa da sukai ja yayi Ahankali yana dawowa da tinaninsa daidai..

Akan tinanin Abinda yake shirin faruwa tinaninsa ya tsaya da hankalinsa..

"Bayyanar ciwon falaq na Bayyanar musu abinda basu sani bane ko me?

Kaddara ce ko Haske ne yake buduwa a garesu??

Numfashi ya sauke tareda miqewa ya fada toilet yayi wanka kansa ya dan sake alokacin ne ya shirya ya fito sallan magrib da suka fita da LIMBA.

A yanzu da suka dawo kaman yanda AZIZ ya saka a binciko masa qwararrun doctors din zuciya shima zaiso ganawar dasu dan tabbatarwan karshe dan haka a cikin daren ya saka babban Pa dinsa da kusan daga shi sai Fahad din a kusanci da kulawa da duk kadarorin LIMBA yace zuwa gobe a hado masa list na best qwararrun cardiologist da bayanansu ya tiro masa.

"Yes boss by tomorrow insha Allah komai zai iso gareka"

Kashe wayarsa yayi yana kokarin daidaita kansa ya fito.

AZIZ na babban palon har lokacin zaune tareda Falaq dake jikinsa tana masa labari kala kala hadda na Ladyn datake ta magana akanta duk kwanakin wadda take cewa bata burgeta ko kadan amma ta kasa dena maganarta.

Tana ganin sayd gurinsa ta dawo tana fesa masa labarai kala kala yana biye mata shida mama sbd Daddynta kwata kwata baya cikin yanayi na iya biye mata sbd abinda yake cin zuciyarsa.

Abinci suka ci banda AY din wanda tea da dabino kawai yaci ya shige bayan Falaq tayi bacci ta shige kenan.

#MAMUH

#REVENGE

#LOVEANDHATRED

#LIMBAS

#ZADS

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

38

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/JMSe2The4Q2F5tLdzGduyC

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

Koda ya shige bayan yayi shirin bacci cikin kayan bacci masu santsi zaunawa yayi yana lumshe idanuwansa Sanyin Ac na ratsasa ahankali sbd babu alamar bacci a tareda dashi tinani me zurfi da mutuwar jiki ya rufesa duk da bazai taba sakin kari ba akan ciwon nata zaiyi yawon duniya ya nema mata lafia sedai idan Allah yayi itama barinsa zatai tukuna amma yana roko da fatar Allah yasa ya fara barin duniya idan har Ciwon nan mai dauketa ne daga duniyar karta barsa..

Sayd kuwa saida yasha magani me karfin gaske kafin gaske kafin bacci ya iya daukansa.

Da asuba bayan sunyi sallah kowa ya koma bacci

Guraren 8 na safe wayar Sayd ta tadasa bacci kansa da yayi masa nauyi sosai sbd maganin daya sha ya daga yana bude idanuwansa daqyar ya kai hannu ya dauki wayar yana dorawa a kunnensa.

Fahad ne cikin girmmawa yace

"Goodmorning Boss,

Duka bayanan daka nema an hada na turo maka ka duba hotinansu da bayanansu tareda sunayensu suna nan"

"Ok,thanks zan duba yanzun nan,i will get back to you akan sauran bayanin"

Ok boss"

Kashe wayar yayi yana komawa bacci sbd koya duba babu abinda zai gane yanzu dan maganin dayasha bai sakasa ba ko kadan.

**********Ahankali ta tashi daga kwancen datake idanuwanta biyu ba bacci take ba ta jima da farkawa kawai tashin ne ta kasa sbd a macen da jikinta yake da tinanin fuskan data kasa gogewa daga idanuwanta,

Tinda ta dawo Nigeria ta rasa gane kanta da abinda ya maqale mata a tinani da ido wanda take ganin Shedan ne hakama tsananin ciwo da zafin hakan takeji sbd zuciyarta kwata kwata bata yadda tayi tinanin kowane namijin ba bayan Ammar Zad.

Numfashi me sanyi ta sauke ahankali tareda lumshe fararen idanuwanta ta budesu tana daukan wayarta ta qurawa hoton Ammar dayake gaban wayarta ido tareda Ambatar sunansa ahankali tace

"Ammar zad kai kadaine wanda zuciyar Jannah Zad ke so,

Kaine mijina,kaine farin ciki na,kaine abinda kawai nake buqata zuciyata ta kammala"

Rufe idanuwanta tayi ta bude tana ajiye wayar tareda ziro kafafunta qasa tana miqewa tsaye sanye da kayan bacci riga da wando masu kauri ta nufi toilet tana dafe zuciyarta dake bugawa ahankali tana jin kaman kalamanta ba daga zuciyar taya suka fito ba iya bakinta ne.

Numfashi me qarfi ta sauke tana qarasa shigewa toilet din dan fitar da tinanin komai a zuciyarta.

Brush tayi tana kallan fuskanta a jikin mirror wanda tayi fayau sbd tashinta kenan.

Tana gamawa zare kayan jikinta tayi tana qarasawa bathtub ta kunna ruwan dumi ta shige.

Ta jima kafin ta fito daure da blue towel ta nufi wayarta dake ringing ta duba taga sunan MAN dinta ne dan haka ta dauka tana zaunawa gaban mirror da wata muryan data sakasa ajiye Ipad din datake hannunsa yana duba sako ya ajiye akan table dayake gabansa na bedroom dinsa yana jinginar da bayansa muryan na kashe kowane irin kuzarin jikinsa da zuciyarsa yace

"How are you Love??

Kin tashi?

Numfashi me sanyi ta sauke tana kallan fuskanta tace

"Goodmorning Love,

Na tashi ina shiryawa am coming out for breakfast"

"Ok take your time and kinsha maganinki kuwa?

"Yes love" tafada tana kallan drawer din da maganinta suke ciki.

Aje wayar sukai yana cewa ta kula gurin shiryawa kada ta wahalar da kanta.

Shiryawa ta fara yi a natse tana gamawa ta saka free skirt da riga na Dior da scarf ta ziro flat versace ta fito riqe da wayarta wani lafiyayyan qamshi na tashi a jikinta na woodyLeather.

Kai tsaye palon Dad ta nufa wanda yake palon zaune yana waya cikin nutsuwa da kwanciyar hankali tareda manyanci da Duniya data gama tsaya masa.

Yana ganinta ya bude mata hannunsa daya ta qaraso ta zauna kusa dashi tana rungume hannunsa a jikinta ta bude baki cikin tsananin kaunarsa da sakewan datake tsakaninsu duka familyn tace

"Goodmorning BestDad" (hakan itama take kiransa tin tana qaramarta)

Murmushin farin cikin ganinta kafai da yayi ya fara sakewa kafin ya kashe wayar dayake yace

"Morning My Angel,

Kin tashi lafiya?

Yaya maganinki kinsha kuwa?

"Nasha kaima kasha naka Bdad?

Amsawa yayi da cewa yasha yana murmushin jin dadi..

Shigowan Mimi ne ya sakata sake lafewa gefensa tana murmushi tace

"Goodmorning Mimi,

Kin tashi lfy?

Qarasowa tayi tana zaunawa gefen dad din tace

"Lfy kalau,kinsha maganinki?

Yes" tace sbd tasan kowa a familyn babu ranar da babu wanda baya tambayar tasha maganinta.

Ko gama magana da Mimi bataiba qamshin Ammar yafara shiga hancinta ta dago idanuwanta ta zubawa kofar sai gashi ya sako kai cikin wani irin class da nutsuwa sanyeda Ash balmains.

Maheer ne shima ya sako kai tareda Anny tana gafensa kowannensu yana fidda nasa kalan qamshin na shegun designer Turaren dasuke amfani dasu masu tsadan gaske.

Akan Ammar idanuwanta suke tana jifansa da kallan daya sakasa zuba mata nasa idanuwan yana jin idan da ya rasata a bayan da yanzu baya duniyar dan wlh bazai iya rayuwa babuta,

Wani irin masifaffen sonta ne Allah ya halitta masa a zuciya da kirjinsa da ko tinanin rasata kadai idan yayi yake qarewa a hannun therapist dinsa sbd zarewa yakeyi gaba daya da iya wannan tunanin dan hakanne yasa yariga yasan babu rashinta a kundinsa saidai idan karshen tasa rayuwar ne yazo dan hakan ne bai taba jin komaiba a rayukan da suka hallakar dan nema mata zuciyar datake bugawa a kirjinta hakama da yau zaa ce wannan dinma ta gaza to tabbas zai koma farautan zuciyoyin mutane matacci da rayayyu dan nema mata lafiya kawai.

Gefen Miminsa ya qarasa ya zauna yana kallan dad da murmushi da farin ciki a fuskansa yace

"Goodmorning Dad"

Amsawa dad yayi yana amsa gaisuwan Maheer shima kafin ta Anny wadda itama ta zauna gefen mijinta.

Saleem ne ya shigo karshe yana waya fuskansa gabaki daya ba walwala.

Kallansa sukai ganin yanayinsa ya saka yana gama wayar Maheer ya kallesa yace

"Issue din Approval na wanda kakeson ne ko yaya??

Wayarsa ga ajiye gefensa yana sauke numfashi me zafin gaske yace

"Yes,sunata rejecting din proposal dina batareda ma an tsaya andubaba"

Da mamaki gabaki dayansu suka kallesa sbd jin wai rejection ga ZAADENs.

Cikin rashin Bawa zancen mahimmanci sbd yasan bama abu bane me yiyuwa rejecting zaadens dad ya kalli Maheer yace

"Handle the situation,koma waye ka tabbatar masa da yasan Zaadens ne zasuyi masa alfarma"

Maheer saleem din ya kalla shima cikin hana ransa baci sbd baya buqatan sakawa kansa ciwo akan mutanen da basuda mahimmanci a taqaice yace

"Wats the name???

"LIMBAs EMwrld"

Ammar ne ya dago ahankali ya kalli saleem din hakama Dad da shi kansa Maheer din sbd sun san Kamfanin A suna sbd kusan duka abokan businesses nasu suna Yi dashi sosai hakama yana cikin masu kudin dasuke gogawa dasu duk da basu taba sanin junaba amma sunsan sunan hakama shima dole yasan sunansu.

"AZIZ AY LIMBA the lucky Monster" Maheer ya fada yana kallan Saleem din.

Yes" ya fada yana jin daci sbd LIMBAn kadaine wanda zai basu abinda sukeso a sabon business din nasu wanda yanaqi dole sedai suyi da qananun kamfani wanda ba girmasu bane hakama ci bayane garesu da kuma bazasu habbaku akaiba yanda sukeso.

Ammar dayaji sunan Har cikin zuciyarsa kallan Maheer yayi yace

"Banajin business dashi zaiyi amfani sbd yafara da zafin kai,

Waye shi?" Ya tambaya yana kallan Saleem wanda ya dauki wayarsa daya ajiye gefensa ya nemo bayanin komai akan AY din dayake dashi sbd sosai yake bibiyarsa sbd shi ba qaramin aiki yakeson yayi a tareda Limban ba tamkar burine dayakeson cikawa na aiki dashi.

Horonsa ne yana sanye da Fararen kaya da fcap zaune a kujera da qaramin table gefensa Asalin kyansa da kwarjininsa me tsanani a bayyane suke ko a hoton da alama gurin golf ne yake sbd kayan dayake jikiksa ya nuna hakan.

Maheer kallo daya yayi masa ya karanto izzar data sakasa rejecting Zadeens dan haka ko bayanin komai bai tsaya karantawa ba yace da kansa zai gansa.

Dad kuwa kallo daya yayi masa ya dauke kai sbd maheer zaiji da komai sedai yana hango zafin kai a tattarda da aura dinsa.

Ammar ne ya zubawa AY din idanuwansa yana kallansa...

Wani irin yanayi na qi da makamancinsa yaji yana shigarsa akansa,

Dauke idanuwansa yayi akai yana sake qaramin tsokin inda AY din ya samu guts na rejecting dinsu.

Jannah kuwa bisa ga rashin sani idanuwanta suka sauka akan fuskansa wani irin sanyi taji yana sauka jikinta tana zuba masa idanuwa zuciyar na harbawa ahankali cikin sanyi da nutsuwa.

"AZIZ LIMBA" sunan ya sake shiga kanta ahankali tana sauke numfashi tareda dauke idanuwanta daga fuskansa tana maidawa kan Ammar ta zuba masa ido tana kalla jikinta na mutuwa.

Jin idanuwansa akanta suna magana dasu dad ya sanyashi kallanta

Murmushi me sanyi da kyau ta sakar masa tana bude bakinta batareda sautiba ta motsasu da cewa

"My love"

Murmushi ya sakar mata zuciyarsa na wankewa daga duka takaicin Limban daya cikesa.

Basu fito breakfast ba sai bayan kusan mintina suka nufi dining room tana gefen Dad ammar na gefen Mimi Anny kuwa tana gefen mijinta tana tinanin inda ta taba ganin fuskan AZIZ AY LIMBA dinnan dasuka gani yanzu,

Tabbas ta taba ganinsa ko wani me kama dashi duk da kamannin suna bace mata amma dai tasan ta taba gani sedai kuma ta manta kokuma kila shi dinne ta taba ganin hotonsa a media ko tv.

Makeken dining me kujeru da yawa an cikesa da abinci kusan kala hudu sbd kowa da abinda yafi buqatan breakfast dashi.

Maheer sun rigasa zama sbd saida yayi waya da PA dinsa akan yanason bayanin komai akan AZIZ AY LIMBA kuma yana son shi da shi su hadu akan business din Zadeens.

Angama yace masa yana fara abinda aka sakasa,

Shi kuma Maheer wayar ya kashe yana zaunawa dining sbd tabbas yanason haduwa da AZIZ LIMBA sbd yaga iya power din dayake dashi dan su sune power din da kansu.

****

Sayd sai karfe goma da mintina ya farka daga baccinsa kansa yayi masa tsananin nauyi ya bude idanuwansa yana tashi zaune kansa na sake masa nauyi sosai.

Time ya kalla ya sauke ajiyar zuciya tareda miqa hannunsa ya dauki wayarsa yaga misscalls da yawa dan haka ya miqe da sauri duk da AY bazai fita aiki ba hutu yake amma shi akwai abubuwa da yawa dazai handling ciki harda top qwararrun cardiologist da aka hado zai gabatarwa AZIZ din.

Ipad dinsa ya dauka dan duba sakon da Fahad ya turo akan binciken..

Kunnawa yayi tareda shiga sakon kai tsaye..

Hoton DR ABRAHAM SMITH ne abu na farko daya fara bayyana akan screen din tareda sunansa da manyan baqi tareda bayaninsa da qwarewansa.....

Kansa da bai gama warwarewa bane yaji yayi masa dum kafafunsa suka kasa daukansa ya zube qasa a gurfane yana riqe ipad din datake kokarin subuce masa yana qura idanuwansa da suka bude gaba daya baccin cikinsu na fita sbd Shin babban Likitan da yayi aikin Ummitah dan bazai manta fuskansa ba abada dashi da sauran likitocin biyu daya dr Nicolas dayan dr ismail.....

Rawa hannuwansa suka fara yana kasa riqe Ipad din ya lalubo wayarsa ya saka kiran Fahad.

Yana dauka ya jefa masa tambayar

"DR ABRAHAM SMITH likitan zuciya ne kokuwa gynecologist?????

"Babban likitan Zuciya ne kuma kwararre shine top a list dinmu,

Yayi aiki a Nigeria tsawon lokaci kafin ya koma Greece,bai taba zama gynecologist ba akwai dansa Dr Nico yana cikin list din shima cardiologist ne kwararre so.....

Datse wayar Sayd yayi wayar na subuce masa daga hannu kansa na juyawa hakama zuciyarsa bugawa takeyi kaman zata faso kirjinsa ta fito.....

Fuskan Dr Abraham ya qurawa idanuwansa da ganinsu ke ragewa yana fara ganin dishi dishi harya dena ganin komai ya zube a gurin.

#MAMUH

#THE ZAADENS

#THE LIMBA

#BILLIONAIRESWAR/REVENGE

#CRAZYLOVE

#HEARTACHE

#AZIZ LIMBA

#JANNAH ZAD

#AMMAR ZAD

#FALAQ

#LOVE AND HATRED

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

39

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/IyDlSVdw1rDIlCNNQMeI68

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

Neman toshewa kirjinsa yakeyi yana jin numfashinsa na neman yankewa idanuwansa sukai jajir ya daga hannunsa daqyar baya gani sosai ya kamo wayarsa dake yashe a qasa ya saka kiran fahad sedai kafin fahad din ya dauka numfashinsa ya sarke a gurin.

Fahad na dauka cikin girmmawa ya fara magana yaji shiru.

Cire wayar yayi daga kunnensa ya duba yaga kiran na tafiya ya sake dorawa kan kunnensa yana ambatar sunansa da girmamawa.

Jin shiru saiya kashe ya saka kiransa tafara ringing harta katse baa dagaba

Sake saka kiran yayi yana kallan time kafin ya juya kan motarsa kawai zuwa LIMBAs din batareda ya dena kiran wayar ba.

Koda ya iso Babu wanda ya fito gidan tsit hakama baa zuwa bangaren AY sbd a ciki yake sosai bare yaje yafara kai masa gaisuwa dan haka Fiddausi da masu aiki ne sukai masa barka da zuwa dayake shima kowa a gidan ya sansa tinda duka yaran Limban ne.

Amsawa kawai yayi ya nufi bangaren Sayd

yana isa so daya yayi knocking kafin ya bude kofar bedroom din nasa.

Abinda ransa ya basa na cewan ba lafiya ba ne yaci karo dashi sbd a kwance Sayd din yake a qasa yana kokarin samun attack sbd numfashinsa dake kokarin yankewa sbd shock.

Da saurin gaske Fahad yayi kansa yana ambatar sunansa tareda basa taimakon gaggawa sbd kada numfashin nasa ya yanke sedai kaman hakan bazaiyiba dan

haka da sauri ya kamasa ya maidasa kan lafiyayyan gadonsa dake dakin ya daga wayarsa da sauri yana kiran dr.

Yana samun likita da sauri ya sanar dashi suna buqatan taimakon gaggawa a gidan.

Yana kashe wayar kansa ya koma yana kokarin taimaka masa gurin saisaituwan numfashin yana miqewa da sauri ya dauko abu yana fifita masa sbd ya samu iskan shaqar sbd kamanma suffocating yake.

Andauki mintina sosai kafin dr Raheem ya iso gidan wanda zuwansa ne yasa mutan gidan suka san abinda yake faruwa dan haka cikin tashin hankali mama da Fiddausi sukayo dakin bayan maman ta kira wayar AZIZ ta sanar dashi Sayd ba lafiya.

Kansa dr Raheem yayi da sauri yana kallansa yasan attack ne ya samu...

AZIZ dinne shima ya iso dakin a natse babu walwala a fuskansa Kallansa mama tayi cikin kulawa da damuwa tace

"Kaima kaman bakada lafiyar AZIZ,

Lafiya kuwa?

Jamaa meyake faruwa?

Baice komaiba ya nufi Sayd din wanda Dr Raheem ke dubawa yana ambatar sunansa cikeda kulawa.

Gefe Fahad ya matsa cikeda girmamawa yana masa barka da fitowa.

Amsawa yayi yana kallan Sayd din ya jefawa Fahad tambayar

"Me faru?

Meya samesa?"

Dagowa Fahad yayi yana kasa kallan AZIZ din dika yace

"Bansaniba,mungama waya dashi akan reports da profiles na Doctors da aka buqata ne dana turo masa,

Sai kuma daga baya ya sake kira ya tambayeni qarin bayani akan daya daga cikinsu na fada masa abinda na sani akai wanda it seems like ya sansa kokuma makamancin hakan sai kuka gashi ya sake kirana banaji koda na iso na samesa ya samu attack so i called Dr Raheem"

Shiru AZIZ din yai yana sake maida idanuwansa akan Sayd da idanuwansa sukai jajir numfashinsa ya fara daidaituwa sedai yaqi dago kansa ya kalli AZIZ din wanda yake nazartan yanayinsa sbd kaf duniya a yanzu bayajin akwai abinda zai saka Sayd din samun attack yanda zuciyarsa ta kangare ya zama wani irin me tsananin karfin hali dan haka koma menene akwai abinda ya sakasa samun attack din lokaci daya.

Kan Dr Raheem ya maida idanuwansa dake juyawa ahankali ya bude baki a natse yace

"Yaya?All good,right Dr?

Juyowa Dr Yayi ya kalli AZIZ din yana dan sauke numfashi yace

"Yes attack ne due to shock kawai ba komaiba amma yanzu insha Allah zai daidaita tinda numfashinsa ya dawo daidai"

Numfashi me sanyi da nutsuwa ya sauke yana kallan Sayd din yace

"Ka kashe wayoyinka ka huta dakyau coz lafiyanka na gaban komai ka kula,Allah ya tsare gaba"

Gyada kai sayd yayi yana kasa dagowa sbd sam baya iya ko hada ido da AZIZ din sbd tsoro ma yakejin yana rufesa da wata irin tashin hankali na fargaban abinda zai iya biyowa baya idan abinda yake gani yana shirin zama gaskia

Juyawa sukai kowa ya fice daga dakin dan barinsa ya huta ko zai sake warwarewa.

Fahad kadai aka bari wanda Sayd ya dago jajayen idanuwansa ya kalla yana sauke wani nannauyan numfashi mara karfi sbd karfinsa da yayi kasa sbd attack din.

Fahad ma kallansa yayi cikin kulawa yana sake masa sannu ya tattara ipad dij sayd din da qasu abubuwan da suka zube ya sauke ya dauka a table dayake tsakiyar dakin yana kallan time yace zai tafi yaji da office tinda yau daga shi har Ogan kwata kwata bame shiga office din.

Cikin nauyin muryansa datai kauri sosai sbd nauyin dayakeji a kirjinsa na tsoro da tashin hankali tareda wani irin masifaffen tiriri da zafi ya bude baki yakira Fahad din.

Dakatawa yayi tareda juyowa yana dawowa cikin girmmawa ya bude baki zaiyi magana Sayd ya katsesa da cewa

"Dr Abraham a wane asibiti yai aiki a Nigeria??

Ipad dinsa ya koma motarsa ya dauko ya dawo yana bude duka bayanan daya samu akansa na fili dana boye ya fara karanto masa

"ZAADEN HLTH CEN/SPEACIALIST,

Yayi aiki tareda Dansa kaman yanda na fada maka,

Yanada kusanci da ZAADENs sosai coz sun zama tamkar family"

Shiru Sayd yayi yana shiga tinani kafin ya sake bude baki yace

"Alaqar menene a tsakaninsa dasu da suka samu kusanci? I mean wane hulda ne tsakaninsu?

Is he a business man apart from being a Doc??"

"Nope" fahad ya fada yana sake duba profile din Dr Abraham din dakyau wanda aka hada aka turo masa.

Dagowa Sayd yayi ya kalli fahad yana sake shiga tinanin dayake nauyaya kansa ya bude baki yace

"Shine family doctor na ZAADENs kenan?

Yes"

"Meya hadasu da likitan zuciya da iya aikin zuciyar ya sani dazai zama family doc dinsu wanda har suka taho dashi qasarsu?

"I don't know that Boss Amma akwai yiyuwar sunada patient me heart problem din shiyasa ya zama family but.....

Katsesa Sayd yayi cikin Wani irin sautin daya saka fahad din kallansa da sauri..

"Inason full background details na ZAADENs tin daga Kakansu asalin Zad din har zuwa yanzu,

Inason medical history da health status dinsu da komai,

Idan nace komai ina nufin har wanda bai kamata a saniba inason full dets,

Ko nawa zaa kashe ina son samun wannan bayanin komai kada a bari kota yaya koda hakan na nufin kidnapping wani ne i mst get the dets"

Shiru Fahad yayi sedai kuma yasan komai zaiyi saiyayi ya samo bayanan da Sayd din ya fada sbd AZIZ LIMBA idan yace yanason details to yana nufin yana sonsu by all means dan haka tinda ya fara aiki dasu babu wani details na sirri da wanda bana sirrinba da baya iya bi ya binciko sbd Allah ya basa wata irin naci da baiwan iya bin sirri ya nemota.

"Yes boss insha Allah zan hada duka bayanan"

Gyada kai sayd yayi yana rufe idanuwansa sbd nauyin da kansa keyi sbd tinanin dayake sake rikita kansa.

Fitowa fahad yayi yana daga wayarsa dan kira yafara bincikensa ayau din duk da ayyukan sun masa yawa ga office ma ana jiransa.

Harabar gida ya fito yana nufar motarsa bayan ya kashe wayar dayayi yana kokarin bude motar sako ya shigo wayarsa.

Saida ya shiga motar ya zauna zai tada motar yaga sunan SIR LIMBA ne ya turo sakon.

Saurin bude dakon yayi yana karanta layi daya daya rubuto masa.

"In my office"

Kashe wayar yayi ya bude motar yana fitowa dauke da ipad dinsa da wayarsa sbd yasan aikine so dole kila akwai yiyuwar buqatar ipad din tinda komai na ayyukansu da ita sukeyi.

Office dinsa na cikin gidan ya nufa yana dan daidaita nutsuwarsa.

Knocking yayi a natse so daya kafin ya bude kofar office din wadda qamshin AZIZ dinne ya fara kado masa cikin sanyi da nutsuwa,

Yana zaune akan sofa ta hutawa dake office din wayarsa na kan table din gabansa fuskansa fresh ba yanayin komai akanta sai aura dinsa data cike gurin ba hayaniya.

Qarasowa fahad yayi yana dan kallan AZIZ din cikin girmmawa da tsananin kaunarsa dayake.

Cikin girmmawa yace

"Gani"

Idanuwansa ya dago ya kalli fahad din dasu ya sake dan karantar yanayinsa kafin ya bude baki yace

"Meyake faruwa?

Wane doc ne Sayd yake neman qarin bayani akansa?

Ipad dinsa ya dago ya nemo profile din Dr Abraham da komai daya hada yake ciki ya qaraso gaban AY din ya basa cikeda girmama yana cewa

"Dr Abraham,daya daga cikin manyan kwararrun likitocin Zuciya da muka binciko sbd Matsalar Falaq Aziz,

Yayi aiki a Nigeria dan lokaci kafin ya baro,

Close family friend ne na ZAADENs wanda kuma a Nigeria dinma a asibitinsu yayi aiki,

A yanzu cikakkiyar bincike da bayanin asalin alaqar data tsakaninsa da ZAADENs Sir Sayd yace a binciko masa,sai kuma idan ya taba zama gynecology doc wanda kuma tin a gurin binciken namu babu inda ya taba zama gynecologist.....

Dagowa AZIZ yayi da fararen idanuwansa daya zubawa Dr Abraham din ya kalli Fahad a natse yace

"Gynecology Doc??

Meyasa yake son sanin hakan?

"I don't know Sir but yanason sanin Medical history na familyn zadeens gaba daya wanda inaga kaman yana tinanin akwai me ciwon zuciya a cikin familyn shiyasa suke tareda dr Abraham din kuma ya dage yanason sanin Meya hada likitan zuciya dana mata"

Shiru AZIZ yayi yana sauraron bayanan suna shiga kansa daki daki yana tinani akansu sbd sanin Sayd baya binciken abinda baida tsananin mahimmanci hakama tareda boye masa wanda hakan ne ya saka tinaninsa tsayuwa akan koma menene yanason confirming nasa ne kafin fada masa,

Idan har sai yayi confirming kafin ya sanar dashi to tabbas mahimmancin abin na tattareda hadarin dayake gudin basa false bayani...

Shiru gurin ya sake dauka kafin Wayarsa dake gabansa ya miqa hannunsa ya dauka batareda yace komaiba ya nemo Numbern Alh Saad ya saka kira kai tsaye.

Ringing uku tayi aka dauki wayar

Cikin kwanciyar hankali a natse suka gaisa tareda tambayar su Falaq dasu mama yace duk suna lafiya shima ya tambaya su anty maryam da sauran yaransa da suka zama yan mata duk suna university.

Kai tsaye bayan gaisuwar ya jefa masa tambayar data saka Alh Saad din Ajiye cup Tea dayake hannunsa yana sha a natse cikim lafiyayyan palonsa dayake katafen gidansa.

"Wane Asibiti ne Ummitah ta haihu???"

"ZAADEN" Alh Saad ya fada cikin tsananin mamakin tambayar sbd tinda akai rasuwar yayi jinya ya warke har yau bai taba tambaya ko fadar magana ko daya akan ciwon datai da rasuwarba shiyasa suma sukai shiru babu wanda ya fada masa irin yanda taita jinya kafin haihuwar sbd ya zabi danne ciwon rashinta a ransa ya mutu dashi batareda yaji azabar ciwon datasha ba wanda zai qarasa dagargaza karfin zuciyar daya sakawa kansa ne.

#MAMUH

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

40

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/IyDlSVdw1rDIlCNNQMeI68

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

"Thank you" AZIZ yace yana kashe wayarsa ya ajiye gefensa ya dago ya kalli fahad dayake jiran umarninsa bude baki yace

"Dukkanin Abinda ka sani na bayanin daya buqata ka hadosa cikin gaggawa inason sanin koma menene daya shafi wannan maganar"

Cikin tabbatarwa Fahad yace

"Angama Sir"

Harya juya zai fice AZIZ din ya kirasa ahankali

yana juyowa yace masa yanason Ipad din Sayd a hannunsa yanzu.

Ficewa fahad yayi ya koma dakin Sayd wanda yake toilet yana sakarwa kansa ruwan dumi sbd sake samun karfi.

Baima tsaya komaiba daukanta kawai yayi ya fice ya kaiwa AZIZ wanda yana karba mai tsaye history na browsers dinsa ya ringa shiga.

Shiru yayi yana bin duka histories din wainda duka bincike ne kawai yake akan Masu ciki da yanda ake cire zuciyar dan adam sai kuma bincike akan scar din da aikin zuciya yake bari wanda kusan shine yafi yawa.

Shiru yayi yana ajiye ipad din gefensa tareda dan rufe idanuwansa yana hana kansa tinanin komai dan baisan me sayd zaiyi da wannan binciken ba seda kuma binciken da zaayi akan zaadens ne yake buqatan sanin dalili ga kuma dr Abraham da shima yake nacin neman bayanin komai akansa wanda duka idan aka hada link daya ne asibiti tinda shima Sayd idan har yasan Abraham a asibitin ne wanda duka kuma dai haihuwan Ummitah ce takaisu asibitin da har akai haduwar.

Nunfashi mara sauti ya sauke yan bude idanuwansa ya dauki wayarsa ya miqe yabar office din zuwa cikin gida.

Kai tsaye dakin Sayd din ya sake zuwa ya dubasa ya tararda ya kwanta bacci ma ya daukesa dan haka ya wuce nasa bangaren bayan ya sanarwa mama ta kwantar da hankalinta b damuwar komai bane may be ma stress ne na aiki da zaman da basu cika yiba.

Yadda mama tayi ta dan kwantar da hankalinta sbd Sayd shima 'da ne gareta tana kaunarsa sosai da sosai.

Falaq bata gida tana school shiyasa gidan yake tsit sai data dawo hayaniyar gidan ta dawo.

Abincin rana gabaki dayansu gidan sukaci a dining kaman yanda suka saba

Sayd ma ya fito dashi akaci abincin sbd bayason yabar kofar da AZIZ zaisan akwai abinda bayason ya sani dan haka ya sake.

AZIZ din kuwa ganin ya sake batareda ya sanar dashi komaiba ya sakasa tabbatarda abinda yake binciken ba alkhairi bane tinda yake kokarin boye masa.

Da daddare da kansa ya raka Falaq dakinta sai datai bacci ya fito ya wuce bedroom dinsa yana kashe wayoyinsa,

Wanka kawai yai yayi shirin bacci ya kwanta yana rufe idanuwansa batareda bacci yazo masa ba sbd abubuwa da yawa ne a zuciyarsa da kansa wanda duk dare kafin ya kwanta kewar yar uwarsa ce take zuwar masa wadda yakewa fata da adduar tana cikin rahamar ubangiji.

**Washe gari ma basu fita aiki ba a gida suka wuni Sayd din ya sake warwarewa shima kuma hutu da kadaici yake so dan haka ko fitowa baiyiba abincinsa ma sedai aka kai masa palonsa aka jera masa acan yaci.

Sayd kuwa Fita yayi sbd tsananta bincikensa da ayanzu shine abinda yake tsananin buqata.

Wayar Latif Sayd ya kira wanda yake cikin yan Amanar maaikatan AZIZ kuma duk da basa kasar haryanzu LIMBA na biyansa Albashi hakama shine drivern da duk yawon asibitin da sukai harma da ranar haihuwa shine yake yawo dasu har suka baro Nigeria shine drivernsu.

Latif dayake Shagonsa daya bude yana business dinsa yana ganin kiran ya daga cikeda girmamawa yana cewa

"Oga Sayd"

Gaisawa sukai Sayd din ya gyara zamansa yana sauke numfashi me sanyi kafin ya bude baki cikin bayyanarda Buqatan abinda zai tambaya batareda delay ba

Shima Latif din Nutsuwa yayi yana aje abinda yake tareda wucewa kurya inda baa shiga saishi kadai ya zauna dan jin abinda Sayd din zai fada.

"Latif ka tina a ranar da Ummitah ta rasu akwai Dr da shine yayi mana bayani kuma shine ya kula damu a wannan lokacin???

Cikin nazari Latif ya dan shiga tinani yana kokarin tinawa da lokacin sbd dashi suke tare a asibitin.

Cikin rashin tabbatarwa yace

"Eh wani black haka naji suna kiransa da kaman Dr samail ne ko yaya ma suna.....katsesa Sayd yayi da sauri da cewa

"Yes,yes yes Dr Ismail,yes thats the name"

Jin yayi wani abu daya danne zuciyarsa ya dan fada ya sauke numfashi yana miqewa tsaye yana jin sassauci a ransa yace

"Latif inason kaje asibitin ka bincikamun Dr Ismail din,

Inason sanin bayanai akansa,

Waye shi,

Familynsa,

Aikinsa,

Yana ina yanzu?

Da address dinsa, No i want to know every single abu akan rayuwarsa cikin gaggawa"

Shiru Latif yayi kafin ya sauke numfashi yace

"Angama Oga Sayd sbd babu abinda bazan iya yiwa Familyn Sir AZIZ ba,

Ayau zan ziyarci asibitin na fara sanin Full name nasa da idan yana nan kafin sauran binciken zuwa gobe da kwana biyu zan hado maka komai"

"Thanks" sayd yace yana kashe wayarsa ya wurgar a kujera yana dafe kansa tareda lumshe idanuwansa.

Falaq data kasa gane kan daddynta kwana biyu damuwa ta shiga tafara dagawasu mama hankali wadda itama tane kasa gane kan AZIZ din da kuma sayd da shima duk ya kasa zama kwana biyu

Magana tai musu wanda ya saka Falaq dawo da Daddynta daidai shima sayd ganin AZIZ baice masa komaiba kuma yasan yanda AZIZ din yake da karantar abu da ilimin gane abu atake ya sakasa dawowa daidai sbd tsaro.

********cikin kwana biyu Fahad da Latif suka duqufa da mugun bincike da bin duk wata hanyar samo bayanan da suke nema baji ba gani,

Shi kuma Sayd jin yake kaman zai zare sbd jiransu Amma ya boye yana ayyukansa hankali kwance sbd AZIZ daya fara fita office dan haka ya dan zama busy da ayyuka da kuma handling abubuwa.

Latif ne yafara hada bincikensa dan haka ya kira Sayd din kai tsaye wanda a lokacinda kiran ya shigo yana gaban AZIZ LIMBA yana karanto masa bayanan Report da aka aiko musu daga Italy.

Sunan Latif ne ya bayyana Akan screen din wayar Sayd din datake ajiye a gabansu.

Hannu Sayd ya miqa ahankali ya dauki wayar tareda kashewa ya ajiye gefensa yana cigaba da bayanin da AZIZ ke sauraronsa hankali kwance cikin nutsuwa.

Yana gama bayanansa juyawa yayi ya fice yana amsa wayar Pa din Maheer Zad data shigo wayarsa akan haduwarsu da haryanzu baa san lokacin ba..

Sayd na fita kai tsaye ya katse wayar dayake ya nufi office dinsa yana saka kiran Latif wanda ya dauka take.

"Oga Sayd I've Send you every information daka buqata,

Cikakken Sunansa Dr Ismail Saraki,

Yana Nigeria haryanzu sedai yana jinya haka kawai aka wayi gari ya samu stroke baya iya magana baya iya komai yana gida yana jinya tareda familynsa a Jos,

Likitan zuciya ne shima kuma bai taba aiki a kowane asibiti ba Nigeria sai zaaden sbd baa Nigeria din yake aikiba saida Zaadens suka basa babban matsayi a asibitinsu ya dawo Nigeria,

Address da duka sauran bayanin na turo maka komai"

Katsesa Sayd yayi da cewa

"Idan yana aiki a Zaadens a babban matsayi meyasa basu tsaya masa gurin neman lafiyarsa ba ya koma gida??

"Ba shine abin tambayarba Abin mamakin shine Duk wani hanyoyin samunsa sun datse hakama komai ya rasa a qanqanin lokaci wanda kaman ana kokarin hanasa wani abun ne kokuma akwai abinda yayiwa Zaadens din nake ganin"

Ajiyar zuciya Sayd ya sauke yana cewa

"Ngd Latif zan sake nemanka sbd Zuwa jos zai kamaka"

"Ok Thank you Oga Sayd"

Yana kashe wayar ya miqe yana sauke ajiyar zuciya akai akai sbd komai ya fara fito masa sedai tsoron qarasa bincikawan yake ma dan abinda zai binciko kada ya kashe AZIZ.

Sai yamma suka dawo gida suna isowa AZIZ kai tsaye bangarensa ya nufa yai wanka ya shiryo ya fito suka zauna cin abinci a dining falaq nata masa labarai kala kala wadda a duniya ita kadaice take ajiyesa tayita basa labarai da surutai kala kala ya bata kunnuwansa yana saurara batareda yace komaiba.

Suna gamawa suka wuce sallah

Saida sukai ishai suka dawo,

Motarsu na shigowa harabar gidan motar Fahad na shigowa bayansu dan haka a tare sukai parking.

Fahad dinne ya rigasu fitowa sanye cikin three quarter da farar sweatshirt ya nufo motarsu ya budewa AZIZ motar yana masa barka da dawowa.

Amsawa yayi yana kallansa a taqaice ya nufu hanyar studyroom dinsa suka nufi bayansa.

Yana shiga zaunawa yayi tareda ajiye wayarsa gefensa ya dago a natse ya kalli Sayd wanda yake kallan Fahad kafin ya maida kallansa kan Fahad din ya bude bakinsa yace

"Yes,the dets???

Kallansa Sayd yayi da sauri yana matsowa zaiyi magana AZIZ din ya dago manyan fararen idanuwansa yai masa kallo daya take ta dakata yana komawa baya ya saukar da kansa zuciyarsa na tsananin nauyi da tashin hankalin abinda fahad ya samo akan binciken.

Fahad da shima yake a natse sbd a gaban AZIZ din suke ipad dinsa ya daga ya fara budo bayanan yana cewa

"Babu Alaqar kowane business dake tsakanin Zaadens da dr Abraham saina likitanci wanda kaman yanda muka zarga akwai me ciwon Zuciya a familyn sunanta ZEYNAB ZAD sedai kuma ta rasu da dadewa,

Bayan rasuwarta Zadeens sun sake samun mace a familyn wadda duniya ta sheda yanda suke tsananin sonta amma kuma tana tsaka da karatu kawai aka nemeta aka rasa baa sake samun labarinta ba tsawon shekaru sun boyeta batareda an sake taba ganintaba wanda babu wanda yasan dalilin hakan amma kuma a yanzu tana wannan qasar tana karatu sedai ta koma gida a yanzu batanan,

A familyn kowa mun samu bayanin cikakkiyar lafiyarsu banda JANNAH ZAD wadda babu wanda a iya binciken danai babu likitan daya taba ganinta bayan Dr Abraham....."

Dan shiru yayi yana tinani da shakkar abinda zai fada kafin ya dago ya kalli sayd wanda shima shi yake kalla da dukkanin imaninsa kafin ya juyo ya saci kallan AZIZ da yayi shiru yana sauraronsa da dan sassauta murya yace

"A yanda na tabbatar sbd bamu san health status din JANNAH ZAD ba a cikin familyn kuma dr Abraham ne kadai likitanta kuma Shi din likitan zuciya ne Tabbas itace takeda matsalan Zuciyar datake cikin zaadens,

Dr Abraham ya samu zomowa babban likitan dayake cikin manyan doctors na duniya tareda tarin dukiya me yawan gaske daya zamo babba sbd zaadens da suka tsaya masa,

Jannah Zad itace rai da Zad sukafi so fiyeda komai da suka mallaka a duniya...

Dago idanuwansa yayi Ahankali ya saukesu akan Sayd sbd a duka bayanin baiji wani abin daya shafesu ba bayan maganar ciwon zuciyar datai kama data tasa 'yar dan haka ya zubawa sayd idanuwansa yana jiran bayaninsa wanda bayani kawai yakeso gamsashe batareda wani kwana ko daya ba.

#MAMUH

#BEST REVENGE

#BEST LOVE

#CRAZY LOVERS

#SELFMADE BILLIONAIRE

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899

*_Arewabooks@Mamuhgee_*

41

KALPANAH COLLECTION

08105064494

Shin ke daliba ce ko kuma uwa wadda har yanzu bata daina rokon urgent 2k a wurin yan uwa da kawaye ba,tou nesa tazo kusa domin kuwa na kawo miki maganin matsalarki,domin kuwa *Kalphanah Collection* ta shirya tsaf domin taimaka wa duk wani dan kasuwa ko kuma wanda yake son fara kasuwanci.A *Kalphanah Collection* muna saida kaya kama daga Jaka,Takalmi,Atamfa,Laces,Kayan yara da kuma kayan kitchen.Wani abun mamakin ma muna saida kayan mu ga masu siyen daya ko kuma sari,ga waenda basuda jari ma mun tanadar masu hanyoyi daban daban da zasu fara neman na kansu.Hajiya kina gida kwace zaki dinga jin saukar kudi a asusun bankin ki.Ga musu fuskantar qalubale a kasuwancin su kuma an kawo muku sauqi domin kuwa an bude muku group dinku da zaku dinga tattauna matsalolin ku.

https://chat.whatsapp.com/IyDlSVdw1rDIlCNNQMeI68

Kedai idan kin shirya ki dannan link din nan na kasa domin shiga group dinmu ki ganewa idonki kunsan ance gani ya kore JI

Karki yadda ki wuce bakiyi joining group din nan ba domin kuwa yanzu sallah tana qaratowa ko bakiyi kasuwanci ba zaki siya domin amfanin ki na yau da kullun kuma ko baku buqata yanzu nan gaba zaku iya neman ta.

Siyen na gari maida kudi gida.

08105064494

****

Sayd daya cikin tsananin shock da mamaki da sauri ya karbi ipad din ya zubawa hoton Jannah idanuwansa wadda shekarunta suke kusan daya dana Ummitah..

Hannuwansa na rawa ya ciro wayarsa cikin jikinsa ya saka kiran Latif wanda a cikin bayaninsa yace masa a ranar da akai aikin Ummitah doctors din hudu ne ba uku ba kuma yaga dayan bayan ya fice daga gurin yana cire facemask kuma yaji nurse data biyo bayansa ta kirasa da Dr Zad sedai baiga fuskansa ba.

Cikin sauri yacewa fahad

"Turawa Latif hotunan familyn Zaadens gava dayansu yanzu"

Daukan wayar Latif yayi take sayd yace masa

"Duba ga sako nan fahad ya turo mata kaga idan akwai dr Zad din ranar haihuwan Ummitah"

Kalman data saka AZIZ rufe idanuwansa kenan yana hadiye shirunsa gaba daya tareda wani irin ciwo da radadi suka gama shigewa cikinsa ya bude baki da fushi yace

"Meyake faruwa nake tambaya anan"

Bude baki Sayd yayi zaiyi magana Latif ya kira AZIZ yace ya ajiye wayar ya saka handsfree.

Cikin tabbatarwa Latif yace

"Tabbas naji an ambaci dr Zad amma wlh banga fuskanba sedai koma waye a cikinsu ne sbd su kadaine Zad"

Kashe wayar sayd yayi yana jin kaman zai fasa wayar hannunsa sbd rashin samun tabbacin ganin fuskan.

Cikin wani irin matsanancin ciwo da radadin zuciya ya dago ya kalli AZIZ AY LIMBA ya bude baki da tsananin rauni yace

"A ranar da Ummitah ta rasu gurin wankanta akwai dinki a kirjinta setin zuciyarta sabo wanda a ranar ta samesa sbd koda muka kaita asibiti nine nai shirinta na tabbatarda babu wannan dinkin a kirjinta,

A cikin likitocin da sukai mata aikin haihuwan babu gynecology doc ko daya a cikinsu,

Babu aikin haihuwa a cikinta wanda shima na bincika idan har babu aiki a ciki to tabbas da kanta ta haihu ba aiki akai mata ba,to amma bayyanar aiki a kirjinta shine abinda nakeson sani,

A asibitin zadeens akai mata a aikin,

Likitocinsu ne,

A familyn a akwai me ciwon zuciyar da bamu san waye ba,

Meyesa suka dauki nauyin kai mata gawarta kyauta har gida?

Meya hada haihuwanta da likitocin zuciya?????.....

Tsit gurin ya dauka sbd mutuwar tsayen da fahad yayi da fahimtar inda zancen ya dosa,

AY din kuwa ajiyan zuciya ya sauke me sanyi kansa na kwakwalwansa na kasa daukan me Sayd din ke kokarin fada sbd bame yiyiwa bane har abada hakan sedai kuma baya wasa ko kadan da abinda aka ambaci sunan Ummitah a cikinsa koda kuwa bata raye dan haka ya kallesa a natse yace

"Ina dayan dr din da kake maganar?

"Yana jos"

"A shirya tickets zamu kai masa ziyara lokaci yayi da zansan a hannun waye UMMITAH ta cika da time data rasu" ya fada kai tsaye yana miqewa yabar dakin kirjinsa na wani irin riqewa amma kuma lokaci yayi da fuskanci abinda yaketa gujewa shekara da shekaru musamman a yanzu da wannan unbelievable lamarin yake shigowa a lamarin.

Sayd da babu abinda yakeso din kaman ya gansu a Nigeria din daman sbd ya fuskanci Dr ismail da kansa take ya kalli Fahad yace

"Ayi clearing gaba daya appointments na AY din da schedules nasa na satin gaba daya har zuwa wani satin"

Yes" fahad ya fada yana juyawa shima ya fice,

Sayd din kuwa take ya kira ya saka akai musu booking ticket din tafiya ba bata lokaci.

Mama batasan da tafiyarsu ba sai washe gari kawai kai tsaye taji tafiya AZIZ din zaiyi Nigeria da bayason zuwa tinda Ummitah ta rasu dan haka tasan koma menene zai kaisa yanada matiqar mahimmancin gaske wanda kilama ya shafi Ummitah ko falaq ne dan sune kadai zasu sakashi zuwa Nigeria lokaci daya.

Cikin kwana biyu aka gama komai jirginsu ya saika Nigeria.

A lagos suka sauka kuma anan zasu zauna dan bayajin zai iya zuwa abuja dan haka lafiyayyan Lodge ya sauka wanda securities dinsa kadai da tsaron gurin zakasan ko masu kudin sai wainda suke amfani da dollars ne ke suke gurin.

Koda suka iso lagos din a daren shima latif jirginsa ya sauka a lagos daga abuja dan haka bai samu ganin AZIZ dinba sedai Sayd sai washe gari Sayd ya shiga dashi inda AZIZ din yake ya gaidasa cikeda farin cikin ganinsa da tsananin girmamawa da kaunar dayake masa.

Abinda ya kawosu shi Sayd yake dan haka kwanansu daya a lagos ya nufi jos tareda Latif daman tin kafin su iso Nigeria Latif yaje jos din yayi confirming address din Dr ismail ya kuma gansa ya tabbatar da shi dinne dan haka koda suka isa jos lafiyayyan masauki su sauka sai washe gari suka isa gidansa inda suka tarar dashi zaune daure a kujera baya iya komai.

Dayake ansan ana zuwa dubasa duk da ya dauki shekaru a hakan shiyasa kai tsaye suna fadar gurinsa suka taho dubasa aka shigo dasu har palonsa yana zaune abin tausayi kan kujera an dauresa da belt sbd fadowa dayake.

Sayd ne a gaba sai Latif yana bayansa suka shigo da sallama....

Idanuwansa dake rufe ya bude ya saukar dasu akan Sayd wanda ya sauya gabaki daya sedai kuma kamanninsa basu sauya daga Idanuwansa ba sbd dasu yake kwana a ransa dasu yake tashi sbd sanadin komai da akai musu yake tamkar matacce yanzu rai ne kadai banbancinsa da matacce dan shima mutuwar yake fada tafi masa akan azabar dayake ciki.

Wasu zafafan hawayene masu tafe da radadin dayake zuciyarsa da danasanin da batada amfani suka gangaro gefen Idanuwansa yana kasa kallan fuskan Sayd din wanda shi kuma hawayen dr ismail din da kallan daya kasa masa ya saka zuciyarsa fara karyewa dan abinda yake shirin tabbata...

Zaunawa sukai suna mai masa sannu da fatan samun lafiya sedai kwata kwata Dr ismail din ya kasa kallan Sayd sai hawaye yake zubarwa.

Shiru sukai babu wanda ya iya cewa komai saida matarsa ta shigo Sayd din ya kalleta yana mata tambayoyi akan yanayin jikin nasa tana masa bayanin babu kowane irin cigaba daga yanayinsa.

Nunfashi Sayd din ya sauke ahankali yace

"Zamu dauki nauyin nema masa lafiya tin daga Nigeria har zuwa qasashen da sukeda manyan likitoci idan hakan zai muku"

Ya qarasa maganar yana kallan Dr ismail din wanda ya fashe da kuka yana rintse idanuwansa baki a juye ba damar magana.

Matarsa saurin kallansa tayi kafin ta dawo da kallanta kan Sayd din wanda yake kallansu cikeda yanayi na buqatan amincewansu.

Numfashi ta sauke tana jin farin cikin hakan sbd lura da Dr ismail din ya gane koma su din su waye sedai kukansa daya sakata jin jikinta na mutuwa.

Godia tayi musu cikin tsananin farin ciki da godewa Allah.

Duk yanda sayd yaso magana da dr din kwata kwata ba dama sbd babu abinda zasu iya samu daga garesa sbd bakinma ko kadan baya haduwa bare yayi magana dan haka suna buqatan nema masa lafiya kafin komai sbd shine zai bude musu komai a yanda yake.

Masaukinsu suka koma ya kira AZIZ yayi masa bayanin komai na cewan Dr ismail din bazai iya tahowa ba kaman yanda ya umarta a taho dashi sbd sosai yake cikin ciwon dan haka lafiyarsa zasu nema dan samun biyan buqatansu.

Kwana uku su sayd suka kwashe a jos kafin aka gama shiri a familyn dr ismail din suka taho lagos dashi tareda matarsa da qaninsa babba sbd jinyarsa.

Suna isowa wata lafiyayyar asibiti aka kaisu take aka zubar da kudaden gaske sukace lafiyarsa suke so koda ta wuni daya ce indai zaiyi magana.

Hakan kuwa akai take aka fara kulawa dashi a Amenity tareda tsaro babu abinda suka nema suka rasa,

Matarsa da kaninsa ma duk abinda suke buqata an tanadar musu dan haka hankalinsi kwance suna fatar a dace da yiwa Sayd addua me tarin yawa sbd duk abinda ake basu taba sanin akwai wanda yake bayan taimakon nasu ba bare su sansa su iya sayd din suka sani sai Latif dayake kamar yaronsa.

A bangare daya AZIZ zuciyarsa ta dena tinanin komai na duniya abu daya take buqata shine zancen da zai fito daga bakin Ismail akan Rasuwar Ummitah wadda baisan me zaijiba amma koma menene shi yake tsananin son ji fiyeda komai a duniya yanzu dan haka kudi sosai suke sakewa akansa.

Ganin an dauki lokaci sai ahankali sai kawai ya umarci a fita zuwa italy gurin dr Nico da ismail din dan haka aka fara shirya tafiyarsu wadda cikin saa aka samu kallama komai a cikin wata daya suka tattara suka tafi harda matarsa da qanin nasa.

Sati daya yayi a italy ya koma gida dan jiran labarin samun saukinsa daya tabbatarwa dr Nico koda na minti biyar ne yanason buduwan bakin ismail.

*****A rayuwarsa wannan lokacin shine lokaci mafi nauyi a garesa sbd gaba daya baida abinda yake jira kaman dr ismail sbd jin yake kamar zaice masa Ummitah bata rasu ba tana duniya dan haka ganin an dauki lokaci babu wani cigaba sosai sedai yana samun sauki ba laifi sosai maganar ce kadai da motsa gabban jikinsa basa aiki.

Zuciyarsa ta kasa dauka,kansa ya dauki zafi ya riqe nasa ciwon na neman dawowa na trauma dan haka kai tsaye ya kira Sayd yace ya siya musu ticket na tafiya italy.

Rana tsaka dr Nico ya gansu cikin nutsuwa ya gama yiwa AZIZ din bayanin cigaban da ake samu na lafiyan dr ismail din.

Shiru AZIZ yayi bayan ya gama sauraron dr ya nufi gurin ismail din ya zauna yana facing dinsa tareda zuba masa idanuwansa yana kallansa tsawon mintina.

Numfashi mara sauti ya sauke kafin ya miqe ya fice.

Kwanakin da zasuyi bai iya yinsu ba ya koma gida sbd Bazai iya tsayuwa a gaban mutumin da ransa yake rawaba ya tambayesa abinda bama zai iya fada da bakinsaba.

A ranar da suka isa shima dr ismail din jin yayi kaman duniyar zai bari dan haka a sanyaye yake ko idanuwansa bayason budewa wanda hakan ya saka jikin matarsa sanyi tayita kuka tana rasa yaya zatai da ranta.

Da daddare sayd ya iso palonsa ya tarardashi zaune yayi shiru fuskansa tayi fayau wanda ya saka Sayd jin jikinsa yana sake mutuwa sedai kuma kaman yanda Dr Nico ya kira yace ismail din zai iya amsa tambaya kowace iri batareda ya bude baki ba sbd idanuwansa suna motsawa ya sakasa yanke shawarar fuskantar komai a yau din dan haka ipad dinsa da fuskan dr Nico take bayyane ismail na gabansa zaune akan kujeransa dauke da belt ya ajiye a gaban AZIZ din wanda ya dago idanuwansa da sukai ja ya sauke akan screen din yana zubawa ismail din su yanajin zuciyarsa na wani irin nauyin gaske....

Sayd ne ya bude baki Ahankali cikin tsananin nauyin kirjin shima yace

"A ranar da Ummitah ta haihu a asibitin zaadens da kanta haihu ko cs akai mata????

Rintse idanuwa ahankali dr ismail yayi hawaye masu zafi da baqin cikin rayuwarsa suna gangaro masa ya bude idon tareda kyaftasu ahankali alamar da kanta ta haihu.....

Daukewa numfashin AZIZ ya kusa yi sedai bai motsaba

Sayd da kafafunsa suka kafa rawa bude baki ya sake yi bugun zuciyarsa na tsananta yace

"Meye aikin da kukai mata a kirjinta wanda batada shi????

Qarasa tambayar yayi muryansa na tsananin rawa.....

Ahankali cikin tsananin sanyin jiki dr ismail ya gangaro da idanuwansa zuwa setin kirjinta AZIZ gurin zuciyarsa ya lumshe idanuwansa ahankali wasu hawayen na gangaro masa masu tsananin zafi.....

Kasa magana sayd yayi sbd zuciyarsa data dena bugawa.....

Dr Nico ne yayi saurin kallan ismail din da rawar murya cikeda tsananin tashin hankali yace

"Zuciyarta aka cire?????

Rintes ido yayi alamar hakan

"Kun sakawa wani????

Sake rufe idanuwansa yayi amma kafin yama gama rufewa AZIZ ya miqe ya nufi kofa sedai ko taku daya yayi yana yin na biyu kafafunsa suka gasa sukai wata irin mummunan sarewa ya fadi a gurin.

#MAMUH

#BEST REVENGE

#BROTHER's LOVE

#AZIZ AY LIMBA

#SELFMADE BILLIONAIRE

#JANNAH ZAD

ZAFAFA BIYAR

KALBIM 500

mamuhgee

A DUNIYATA 500

Huguma

AJIYA A DUHU 500

Billyn Abdul

KIRJIN ME HANKALI 500

Miss xoxo

Pay at

0022419171 AccessBank

Maryam sani gummi

Shedan biya

09033181070

Or mtn vtu at

09032345899